[14/07, 7:37 am] Mom Islam Ce: *YARINYA MAI TAƁAR GAZA*

Typing✍

STORY AND WRITING
BY
*Zainab Habib [mom islam]*

*BISMILLAHIR RAHMANIR RAHIM DUKKAN YABO DA GODIYA SUN TABBATA GA ALLAH MAƊAUKAKIN SARKI MAI KOWA MAI KOMAI YA ALLAH KABAMU RAI DA LAFIYA DAKUMA NISAN KWANA KAMAR INDA NAFARA RUBUTA WANAN LITTAFI KABANI IKON KAMMALAH WANAN LITTAFI LAFIYA AMEN YA ALLAH*

Masoyana masu son ganin farinciki na, dominku nafara rubuta wanan littafi sbda ƙauna da kuke nunamin ,amma inhar kuka ƙi yin comments wlh Allah zankoma wattpad da typing gaskiya dan babu abinda na tsana irin kayi karatu ka wuce . dafatan zaku bani haɗin kai.

*AREWA WRITERS ASSOCIATION*

Telegram links https://t.me/joinchat/IaKr804dfndik1e2

Wattpad momislam2020

FREE BOOK 

Page 1 & 2

Wata yarinya ƴar madai daiceya na hango zatakai shekara goma da aihuwa , tafe take tana rawa tana gudu , tana isowa gidan nasu mai ɗauke da ginin siminti da ɗakuna huɗu , ɗaya na mahaifiyarta , ɗaya kuma na mahaifinta ɗayan kuma kitchen ne, ɗayan kuma nata wanda take kwana ,
Su biyu Allah yabawa iyayensu da Aisha da yayanta Zakari .
Zaiyi kimanin shekara ashirin da bakwai a halin yanzu yana neman auran wata yarinya mai suna Fiddausi....!

Ranar Juma'a Aisha taci kwaliya tasa rigar atamfa ta sallar ta , da gudu ta ƙaraso ta hau kan cinyar mama tana cewa " mama nayi kyau kuwa ?" murmishi mama tayi tace " ƴar albarka kinyi kyau sosai .
Aisha nason intayi kwaliya ace tayi kyau inko mutum bai faɗa ba yasan ragowar.
Fitowa tayi babu mayafi a jikinta , ƙofar gida ta nufa tana tafiya nata ƙwalawa ƙawarta kira mai suna Ummi , tunda Ummi ta hangota ta taho da gudu ta rungumeta tana cewa " yanzu ta ina zamu fara ?,samun dakalin ƙofar gidansu Ummi sukayi kana suka zauna sunata shawara a tsakaninsu ,
Shin ta ina zasu fara , ganin wata yarinya na tahowa kanta ɗauke da tiren tallah , da alamu gyaɗa ce .
Aisha ce ta miƙe kamar zatayi gaba ta ɓaro da tire da wawushi gyaɗa ƙulli biyu , ƴar hamsin hamsin , kururuwar ihu yarinyar tasa tana ɗura musu zagi , ko ɗar basuyi ba suka ruga da gudu dan zagi ba damuwarsu bace ,
sudai susamu burinsu ya cika.

Suna zuwa wani lungu kowacce ta kunce nata ɗaurin gyaɗar tanaci suka shiga hirar insun cinye ina zasu nufa ?"
Ummu dake bushe gyaɗar da ta ɓare tace " shagon lawali zamu wlh duk wayonsa yau saimunci wanan kaji da yake soyawa ta amare , tafawa sukayi kana suka karkaɗe zani suka nufi shagon lawali , lokacin ƙarfe huɗu na yamma , samunsa sukayi kwance a gefe tukubar gashin na cikin shagon , saɗaf saɗaf Aisha ta shige ta janyo tsinken da ya tsire kaza , ƙarar ƙarfen da yaji ne yasashi buɗe ido , sunayin ido biyu suka ruga da....!

Wanan somin taɓi ne inaganin comments da shar'hi zakuga wani insha Allah kunsan zuciya nason mai kyautata mata ��.
[14/07, 7:37 am] Mom Islam Ce�: *YARINYA MAI TAƁAR GAZA*

Typing✍.

STORY AND WRITING
BY
*Zainab Habib [Mom Islam]*

*AREWA WRITER'S ASSOCIATION*

Telegram links https://t.me/joinchat/IaKr804dfndik1e2

Wattpad momislam2020

FREE BOOK�

*BISMILLAHIR RAHMANIR RAHIM*.

Page 3 & 4

Shima da gudu ya bisu amma ya kasa kamasu , haka dai ya haƙura ya dawo kan dogon bencin da yake zaune yana maida nunfashi .
Na shiga uku kazar dubu biyu shegiyar nan ta zunduma , cewar Lawali harda ƴar ƙwallar sa yana tuna ɗan jarin nasa dabai taka kara ya karya ba .
Su Aisha basu tsaya ko inaba sai a shagon wani mutumi mai siyarda goro , sanin shidai bashida abinda zasu cuceshi kuma ko sun zo baya korarsu yasa suke yada zango anan .
suna zama suka fito da kazar lokacin mai shagon ma ya rufe ya tashi yace " musu insun gama su shigar masa da buhunsa cikin rumfa ,
Amsawa sukayi da to
Suna shirin fara rabo sukaji hirar wasu samari suna cewa "
Ai wlh yanzu kazar Lawali tazamo wa ƴan mata masifa sai dai amare suci dan wlh duk budurwa ko saurayi yaci kazarnan to ranar saiya gane bashida wayo .
Haɗa ido su Ummi sukayi gabansu ya fara faɗuwa dukda basusan aure ba ,sunajin labari a gurin ƴan matan islamiyarsu sunsan wani abin daga ciki ,
ƙudun dune kazar sukayi Aisha ta miƙawa Ummi tace "barin samo leda zanzo in gaya miki inda zamu kai.
Jikin Ummi banda rawa babu abinda yakeyi, gashi har ana kiran sallar magrib Aisha bata dawo ba , idanunta duk sunyi ja tsabar tsoro,
Hango Aishan da tayi ne tana tahowa hankalinta ya kwanta ,
cewa Aisha tayi , ke Ummi Lawali yakusa kamani hmm badan Allah y temake ni ba aida nashiga uku ,

inayin kwana na janyo leda a shagon Hambali kawai ya taho da gudu yana shirin cafkemin mayafi , tana maganar tana maida nunfashi .
Ganin fuskar Ummi da alamun fushi yasata dakatawa da bata labarin tace " lafiya kuwa Ummi ?Hawaye ne suka zubo daga fuskar Ummi tace " yanzu ina komawa gida wlh Ummana sai ta dukeni gashi dare yayi ,
Dariya Aisha tasa kana tace " aiko duka baya kisa a daki fata abar fata karma kiji tsoro yanzu zomuje kawai ,
Ta miƙawa Ummi baƙar ledar tace " sako kazar anan muje kiga ,
Ummi ta saki ranta amma yawunta na tsinkewa , kasa haƙuri tayi tace " Aisha ina zamukai kazar ? nidai wlh a raba abani tawa ,
Aisha da tafi Ummi wayo tace " lallai kinason a kasheki a gida wanan kazar tanasa hauka , zaro ido Ummi tayi kana tace " taɓɓ gara da kika faɗamin yanzu wa zamu kaiwa ? Aisha ce ta ƙyal ƙyale da dariya tace " budurwar yaya Zakari Fiddausi ...!

Muje zuwa fans ina gwada yanayin karɓar littafinne inkunason typing mai yawwa to kuyi comments inji daɗi .

MOM ISLAM
[14/07, 7:38 am] Mom Islam Ce: *YARINYA MAI TAƁARGAZA*

Typing✍.

STORY AND WRITING
BY
*Zainab Habib [Mom Islam]*

*AREWA WRITER'S ASSOCIATION*

Telegram links https://t.me/joinchat/IaKr804dfndik1e2

Wattpad momislam2020

FREE BOOK

*BISMILLAHIR RAHMANIR RAHIM*.

Page 5 & 6

Suna tafe suna hira har isha'i tayi ko a jikin su , Aisha tasan yau yayan ta bazai zo hira ba amma ba lallai budurwar ta sani ba kasancewar bata da waya , shikuma yatafi ziyara gidan abokinsa .

Aisha dake daɗa gyara ledar kazar tace " Ummi ki gyara gyalenki ki shiga gidannan kice wai Fiddausi tazo inji yaya Zakari , riƙe baki ummi tayi tana jimama aikan , cikin faɗa Aisha tace " tunda bazaki je ba mu kunce wlh wanan karan inmuka kunce mundena magana ,
Da sauri Ummi ta faɗa gidan ta ƙarasa har ƙofar ɗakin su Fiddausi tayi sallama ,
Mamanta ce ta fito tana cewa waye ? tare da amsa sallamar , nice Fiddausi tace " ta tsuguna har ƙasa ta gaida maman Fiddausi .
Wai anty Fiddausi tazo inji yaya Zakari ,
Washe baki maman tayi kana tace "ɗan albarka kice tana zuwa , miƙewa Ummi tayi tare da cewa " to ta fice zuwa gurin shugaba Aisha.

Aisha na ganinta tace " ya akayi Ummi ? gatanan fitowa Ummi tace " jiyo ƙamshin turare yasasu waigawa , ganin Fiddausi ce sanye da rigar atamfa sai zuba ƙamshi takeyi , yasa su durƙusawa kamar da gaske , cikin haɗin baki sukace ina wuni anty .
A yangace ta kallesu tace " lpy ina My Zak ɗin ? Aisha ce ta harareta ta gefen ido , bata bari ta gani ba ,
Tace " mu a maƙotansu muke
Ni sunana Ladidi ta nuna Ummi tace " ita kuma sunanta Kande , ƙunshe dariya Fiddausi take tace " taɓɓ wanan suna haka kamar kun fito karkara , basuce komai ba suka miƙa mata ledar kazar , karɓa tayi cikin farinciki tace " my Zak yana sona over to ku wuce ku tafi gara da baku kawomin gida ba ,
suna tafiya suna waigenta , ganin ta sami guri a dakalin ƙofar gidansu ta zauna ta buɗe ledar yasasu tsayawa can nesa suna kallonta ,
Cin kazar nan takeyi hannu baka hannu ƙwarya kamar mai yunwa kasancewarsu talakawa ba koda yaushe akecin kaza ba .
Juyawa suka sunata dariya , Ummi tace " dare fa yayi nizan wuce gida yunwa nakeji , kowacce ta shige gida kasancewar katanga ce ta raba gidajen nasu , Aisha na shiga tayi arba da yaya Zakari a zauren gidansu , wata uwar harara ya galla mata tare da cewa ina kikaje nafita nemanki tun ɗazu ban ganki ba ?" kuka Aisha tafara tana cewa " kayi haƙuri yaya wlh ba ko ina naje ba , gidan su mama naje Ummi ta dubanin littafin islamiyata shine maman ta aikemu mu siyo mata gari tayi daren girki ,
To zabiya wuce gida Zakari yace " tare da yimata nuni da yatsansa , tana shiga mama ta tare ta , inda ta gayawa yaya Zakari haka ta gayawa mama , cikin sa'a ba'ayi mata komai ba .
Ummi na shiga gida ta tarar da mamanta tana kwashe shanya , cikin faɗuwar gaba ta ƙarasa tare da cewa sannu mama
Ywwa a yawo maman tace " tana zabga mata harara ke bakida gudun magana ko ? bakyajin abinda ake gaya miki ko Ummi ina kikaje ?" gidansu Aisha batada lafiya cewar Ummi , subhanallah mama tace " cikin sigar tausayi , mai yake damunta ? mura Ummi tace " kana ta shige ciki ,
Babu maganar sallah sai ma janyo kwanon abincin ta da tayi ta fara kai loma .
Saida Fiddausi ta cinye wanan kazar ta taune ƙashi ta goge hanunta da mayafinta kana ta nufi gida , tana shiga ta wuce ɗakin da take kwana dama ita kaɗai ce mace " yayunta maza su biyu ne kuma a shagon ƙofar gidansu suke kwana ,
Kwanciya tayi tana juyi tanajin soyayyar Zak ɗinta a cikin kowane sassa na jikinta , misalin ƙarfe goma na dare baci na shirin ɗaukarta tafara jin wani irin kasala tare da mutuwar jiki , tunda take a duniya bata taɓa jin abinda takeji yau ba , jitayi mararta na murɗawa ga sha'awa da takeji tama rasa ya zatayi , runtse idanunta tayi tanata juyi tana cije baki tare da ambaton sunan Allah , nashiga uku , Fiddausi tace " tana hawaye ga ciwon mara , a sunkuye ta fice ta tafi bayi tana nishi , da gudu mamanta ta fito dan taɗan jima tanajin kamar ana kuka , ganin Fiddausi a haka yasata zaro ido tare da cewa gudawa kikeyi ne ......!

*Mom islam✍*
[14/07, 7:52 am] Mom Islam Ce: *YARINYA MAI TAƁARGAZA*

Typing✍.

STORY AND WRITING
BY

*Zainab habib [mom islam]*

*[AREWA WRITER'S ASSOCIATION]*

Telegram links https://t.me/joinchat/IaKr804dfndik1e2

Wattpad momislam 2020

FREE BOOK

*BISMILLAHIR RAHMANIR RAHIM*

Page 7 & 8

Hawaye nabin kumatunta ta yi azamar janyo hanun mama tana yimata nuni da mararta , jinjina kai mama tayi tare da saƙe saƙe iri iri , bari mahaifinki ya dawo daga siyo maganin sauro ayi magana , aure kikeso wlh ,
Wani uban ihu da Fiddausi ta kwaɗa ne yasa mamanta yin shiru da maganar tayo kanta a firgice , Fiddausi .....Fiddausi .. shiru babu motsi a tare da ita , wata uwar tsufa ce tafara suntiri a fuskar mamanta tana mai maita innalilahi , komawa ɗaki tayi da gudu ta ɗauko wayarta Nokia ta danna lammbar yayan Fiddausi , cikin sa'a ta shiga , yana ɗauka kafin yace " wani abu mama tace " kazo gida babu lafiya , tana faɗar haka ta kashe wayar tana cigaba da kuka , gashi babansu bai shigo ba.
Da gudu yayan Fiddausi ya shigo jiki na rawa dan tunda mamansu tace " babu lafiya Hankalin shi ya tashi , gani mama ,
Fuskar mama jiƙe da hawaye tace " kaimu asibiti a mashin ɗinka ,
babu musu ya fice ya gunguro mashin ɗin suka nufi asibiti , daƙyar suka sami ganin likita har aka basu gado , likitar data shigo duba ,Fiddausi tace " su mama subata guri , ficewa sukayi cikin jimamin halinda ta shiga , ƙoƙarin ceto nunfashinta tashigayi cikin sa'a dakuma ikon Allah akayi nasara nunfashin ya dawo dai dai.
Fiddausi na buɗe ido ta fashe da kuka hanunta akan mararta , likitar ce ta matso kusa da ita kana tace " a sannu ya jikin ?" ɗaga kai tayi alamar da sauƙi .
a gwaje gwajen da mukayi mungano magani kikasha na ƙarin sha'awa shiyasa kika galabaita .
ƙara sautin kukan Fiddausi tayi tana cewa " wlh ban taɓa zina ba kuma ni bansha kowane magani ba , ɗan murmishin gefen baki likitar tayi kana tace " to shikenan yanzu kinsan dole in sanar da iyayenki abinda bincike ya nuna mana ? zaro ido tayi tafara haɗa likita da girman Allah , kasancewar likitar mai tausayi dakuma sauƙin kai yasata cewa " dont worry bazan faɗa ba ,
amma ki kiyaye saboda gaba ,
Yan zun ma bawai an gama bane dole ki fito da miji cikin sati sbda nanda one month idan ba'ayi miki aure ba komai zai iya faruwa , sbda abinda kikasha mai ƙarfi ne dole sai kinyi aure zai lafa ,
Firgici tashin hankali duk Fiddausi ta shigeshi , to nagode doctor cewar Fiddausi .
Dafa kafaɗar ta likita tayi tace " na ɗaukeki a matsayin ƙanwata so karki damu nasan abinda zan cewa iyayenki .
likitar na fita Fiddausi ta runtse idanunta tare da tuno kodai kazar da taci ne yasata wanan masifar , noo ta girgiza kai my Zak bazai bani abinda zai zamo min matsala ba sai dai ko gidansu Ameera danaje ne naci wani abu abinka da masu aure .
Anan dai tabar zancen bacci yayi awon gaba da ita .
Koda likita ta sami su mama , tace " yayan Fiddausi ya basu guri yana barin gurin likita ta dubi mama tace " ba' ba wanan ɗiyar taki gaskiya munyi iya bincike .
Binciken mu ya nuna mana inhar ba'ayi mata aure nanda wata ɗaya ba komai zai iya faruwa , tanada ƙarfin sha'awa so sai a kula ,
to nagode mama tace " idanunta sun ciciko da hawaye ,

Zamu ƙara mata ruwa zuwa gobe da safe sai abaku sallama , daganan likitar tayi gaba .
Tunani iri iri mama tafarayi akan Fiddausi to gadon wa tayo a danginsu dan basuda mai kalar halittar ta lolz .
Washe gari marar tayi mata sauƙi sai dai rashin ƙarfin jiki haka yayan ta ya dawo ya biya kuɗin asibiti aka basu sallama, kasancewar ba gida ya kwana ba.
yayan ne yace " Umma mai akace yana damunta ? kawar da kai mama tayi tace " muje gida kawai banason tsayin magana yanzu , haka ya goyosu a mashin suka dawo gida ,
Mama na shiga ita da Fiddausi suka samu baba yayi musu abin karyawa ya share gidan yana shirin shiga wanka , fashewa da kuka mama tayi ta nufi ɗaki zuciyarta babu daɗi , itama Fiddausin ɗakinta ta nufa ta kwanta tanata saƙa da war wara tarasa mafitar lamarin .
Washe gari safe , maman Aisha ta fito da shirin zuwa anguwa , cuno ɗan ƙaramin bakinta tayi tana cewa " mama nifa yunwa nakeji gashi rana tayi wlh inbabu abinci ficewa ta zanyi ehe , dariya mama tayi tace " haba auta ina zaki kibari yanzu mallam zai shigo ya bada kuɗun cefane , hu'um nifa koda ya bada banida kuɗin ciko dan naga kusan kullum sai ribar ƙulu ƙulinki ya shige a cefane , mama ce tace " ke banison kini bini yana kawowa ki ɗora tuwo za'ayi har dare ,ki kwashe kowa ki sa masa nasa zuwa kafin ayin isha'i zan dawo ,Allah ya dawo dake lafiya Aisha tace " tana tsalle , mama na fita ta shige ɗaki tana neman mayafinta zata fice yawo.
Sallamar mallam da ta jiyo ne yasata ɓata rai tayi wurgi da mayafin , sannu da sawowa Aisha tace " kanta a sunkuye , yawwa yar albarka ga kuɗin cefanen yi maza kizo ki ɗora tuwo , da rawar jiki ta karɓa ɗari huɗu ne .
Ja tayi ta tsaya tare da ƙarewa kuɗin kallo tace " mallam kuɗin bazai isa ba gari ɗari uku da hamsinne wani shagon ma ɗari hudu ,
zan saɓa miki Aisha ko mahaifiyarki ɗari uku nake bata dan yau naga kece zakiyi harda nama shine zakiyi min rashin kunya maza kije kiyo cefane kizo ki ɗora tuwo , ficewa tayi fuskarta ɗauke da murmishi , taje ta auno gari mudu ɗaya ragowar hamsin ɗin tace " mai shago yabata gullisuwa ta duka , yana miƙo mata ta cukuai kuyeshi a zaninta ta nufi gida , tana shiga ta haɗa wuta ta wanke tukunya tare da ɗora ruwa , komawa ɗaki tayi tafara binciƙar ƙuli mai suga , cikin sa'a taga ɗaurin hamsin aikuwa ta fito dashi da gishiri ta ɗauko turmi tafara daka , sai da yayi laushi ta kwashe lokacin ruwan tuwo na tafasa .
Ruɗe tayi ta koma ɗaki tana ta shan gullisuwa saida ta shanye ta hamsin a lokaci ɗaya sanan ta fito ta tuƙa tuwo , kwaso kwanuka tayi dana mallam dakuma kwanon miya dana mama dana Yaya Zakari ,
bayan ta sauke tuwon ta nemo mara tafara kwashewa tana gamawa takai na malam ɗaki takai na mama ɗaki dakuma na yaya Zakari ɗakinsa , janyo kwanukan miyan guda uku tayi kowanne tasa masa garin ƙuli ƙuli a ciki ta rufe takai ɗaki , tana gama kaiwa tafice gidan su Ummi .....!

Kuyi haƙuri jiya baku sami typing ba jiya Lahadi bazan dingayi asabar da lahadi ba amma insha Allah daga wanan zan ƙara yawan read more insha Allah .

*MOM ISLAM*
[14/07, 7:52 am] Mom Islam Ce: *YARINYA MAI TAƁARGAZA*

Typing✍.

STORY AND WRITING
BY
*Zainab habib [mom islam]*

*[AREWA WRITER'S ASSOCIATION]*

Telegram links https://t.me/joinchat/IaKr804dfndik1e2

Wattpad momislam 2020

FREE BOOK

*BISMILLAHIR RAHMANIR RAHIM*

Page 9 & 10

Ummi na zaune da kwanon shinkafa da miya a gaban ta ,
Tana ganin Aisha ta tura ƙasan sikel ɗinta tare da ɓata rai , kasancewar maman Ummi tare suka tafi da maman Aisha yasa Aisha zaro wa Ummi ido tace " wlh ko ki ajiye shinkafar nan muci ko in kwashe abincin tukunyarku duka , babu shiri Ummi ta matso dan tasan ba ƙaramin aikin Aisha bane , sai da suka kuma ciko kwano da abinci suna gamawa Aisha ta wuce gida tare da cewa " wlh inhar kikace na shigo gidanan gobe bazani yawo dake ba , to Ummi tace " tana muzurai.
Malam na shigowa ya ɗauki butarshi dake ƙofar ɗakin mama ya wnke hanunsa kana ya nufi ɗakin dan cin abinci , yana buɗe kwanon tuwo yafara sanyawa Aisha albarka , cokali ya ɗauka kana ya buɗe kwanon miya , ganin garin ƙuli yasashi cewa kambun uba ina Aisha ,
Kwala mata kira ƙudundunewa tayi cikin kayan wankin mamanta dake gefe , koshi da yake ɗakin bai san tana ciki ba , ashe tayi bacci ma .
Koda yaya Zakari ya shigo , ɗakinsa ya nufa domin cin abinci , shima yana ganin aikin da akayi yasan aikin na manya ne , ko magana baiyi ba ya fice waje,
Sallama mama tayi tana cewa ina yar albarka harta gama aikin ?
Malam dake ɗaki baƙinciki ya isheshi ko kulata beyi ba yahau jan carbi , shigowa ɗakin tayi tana sallama amma shiru , ganin yana jan carbi yasata ɗaukar kofin ruwa tasha tahau gado ,
Ajiye carbin yayi a gefe yafara bal bala masifa yana cewa " kinbar ƙara fita da magriba tunda huɗubar da kikayi mata kenan , maman bata fahimci inda ya dosa ba tace " malam ban fahimceka bafa , eh ai bazaki fahimta ba naba Aisha ɗari huɗu kuɗin cefane nazo nasami tuwo da ƙuli .
dariya ce taso suɓucewa mama sai ta waske tare da cewa dama ciko nakeyi ita tayimaka na dai dai kuɗinka ne , ta inda malam ya shiga ba tanan yake fita ba , gashi an rasa Aisha , mama ta hangota sbda karta ja mata duka yasa batace ta ganta ba ,
Washe gari da safe malam yayi sammako zuwa jos kasancewar wani aiki da aka kirashi yi na malinta , ran Aisha fess cikin sauri ta shiga wanka tana fitowa ta leƙa ta katanga tace " Ummi na shirya ke nake jira , Ummi dake wanke kwanuka saura tukwane tace " nima koda ruwan sanyi zanyi wanka yanzu na fito wanan tukwanen sun sha ruwa , ta tsallake ta wuce gurin rijiya , wucewa ɗaki Aisha tayi tare da shafa hoda da pink ɗin janbaki sbda mama akwaita da ƙoƙarin siya mata kayan kwaliya kuma babu laifi ta iya kwaliyar , doguwar riga tasa ta atamfa ɗinkin ba ƙaramin kyau yayi mata ba , mama jeki duba akuyoyi sun shigo , da sauri mama ta miƙe sbda tana gudun ɓarna ta fice da sanda .
Jin mama ta zauna a waje yasa Aisha ɗauko wata ƙaramar breziya da suka sato a gun mai gwanjo ta cikata da safar makaranta ta cire rigar tasa , ɗauko dogon hijab tayi tasa takuma yafa gyale ta fice da uban gudu , bata tsaya ko ina ba sai gidansu

Ummi , tun daga zaure take ƙwala mata kira , cikin sa'a Ummi ta fito ita kuma da riga da wando na shadda babu laifi tayi kyau itama harda breziyar tasa tayo waje da gudu , mamanta na ƙwala mata kira amma duk a banza ko juyowa batayi ba.....!

Da nayi muku alƙawarin zan ƙara read more jiya banga comments ba , da bazanyi typing ɗin yauba tunda litrafin baiyi muku ba raina ya ɓacci zan tafi hutu inhar babu comments wlh.

Tofa manyan mata sun fice ko ina zasu dosa oho kubiyo da shar'hi domin jin cigaba 

*MOM ISLAM*
[14/07, 7:53 am] Mom Islam Ce: *YARINYA MAI TAƁARGAZA*

Typing✍.

STORY AND WRITING
BY
*Zainab Habib [Mom Islam]*

*AREWA WRITER'S ASSOCIATION*

Telegram links https://t.me/joinchat/IaKr804dfndik1e2

Wattpad momislam2020

FREE BOOK

*BISMILLAHIR RAHMANIR RAHIM*.

Page 11 & 12

Suna tafiya suna yanga wai su a dole ƴan mata lolz fans kuji fa ƴan shekara goma da wanan lamarin .
Wani saurayi dake zune a kan dakalin da zasu wuce ya kallesu ya tintsire da dariya harda tafawa , Aisha da takai ƙololuwa gurin jin haushi ta juya zatayi gurinshi , janyota Ummi tayi tare da cewa " kinsan fa inda zamuje karki kulashi gabama zamu haɗu sai mun zubar masa da haƙwara munyi masa wawulo suka kwashe da dariya sukayi gaba.
Gidan wata amarya da aka kawo satinnan suka nufa .
Gidane mai ɗauke da ɗan madai daicin get dakuma flawoyi masu kyau yanayin tsarin gidan yasa baza'a kira mai gidan talaka ba amman yanada rufin asiri , amaryar a layinsu take kusa da gidan su Ummi hakan yasa yau zasu kai mata ziyara .
Buɗe get ɗin sukayi kana suka shige , zaune suka sami amaryar mai suna Sudat tana kallo a tv tana sanye da doguwar riga ta atamfa , gaisheta sukayi cikin ladabi kana suka mai da hankali ga tv .
Miƙewa tayi naga ta nufi wata ƙofa , sai gata ta dawo da plet cike da cin cin da cake ,dakuma jug mai ɗauke da haɗin fresh a ciki , da ƴaƴan jug ɗin .
Zuba musu tashiga yi tana gamawa ta miƙe ta shige ciki .
Aisha ce ta kalli Ummi tace " musha ruwan lemu ga leda mu ɗura cincin , haka kuwa akayi suka juye cincin duka .
Aisha ce tace "wa Ummi zokiji kawo kunnenki bansan mai ta gaya mata ba naji sun sa dariya .

Saudat na fitowa sukace zasu tafi har sunyi kamar zasu wuce suka dawo tare da cewa " wlh anty mijinki bin mata yakeyi jiya muka ganshi da wata budurwa yana gyara mata sa takalmi wani uban ihu Saudat tasa tare da cewa Ƙamalu......yau akwai bala'i .
Da gudu suka fice suna maida nunfashi basu tsa ko ina ba sai ƙofar gidan su , a zauren gidan su Ummi suka tsaya aka raba cincin kowa ya shige gida .
tun magrib yaya Zakari ke shirin zuwa gurin Fiddausi anayin isha'i ya na dawowa daga masallaci ya nufi gurinta ,
zaune yake a kan dakalin ƙofar gidan su yana jiran yaga yara ya aika kasancewar bai samu ya siya mata waya ba , cikin sa'a wani yaro yazo wucewa .
kai dan Allah shiga gidannan kace ana sallama da Fiddausi cewar yaya Zakari .
Ba musu yaron ya shiga nanda nan sai gashi ya fito tare da cewa"  wai gatanan zuwa , to nagode yaya Zakari yace " mintuna ƙalilan sai gata nan cikin sanyin jiki , tun daga tahowarta yagane kamar batada lafiya amma baiyi magana ba sai da ya bari ta zauna sannan yace " lovely y kwana biyu ya su mama , lafiya lau tace " kanta a sunkuye .
Meke faruwa ne naga duk kinyi wani iri ,
Cewar yaya Zakari .
Su baba ne sukace nafito da miji nanda kwana uku , zaro ido Zakari yayi yana nazarin maganarta .
Hmm yaya Zakari ya nisa kana yace " gaskiya ina sonki Fiddausi amma maiyasa suke gaggawa ?" anan kam maganar tafara yiwa Fiddausi nauyi cikin dakiya tace " sha'a ...sha'a Zakari ya kasa ganewa ita kuma sauran kalmomin sun maƙale a bakinta ta miƙe da gudu tana kuka .
Babu inda ya iya ya miƙe tare da komawa gida , dama baici abinci ba ya tafi gashi yaci karo da tashin hankali gashi ba wani kuɗi yake dashi masu yawa ba , juyi yakeyi yana tunanin duniya dakuma abubuwan cikinta bashi yasamu bacci ya ɗaukesa ba sai waje ƙarfe uku na dare .
Washe gari malam na fitowa ya leƙa ɗakin kwanan Aisha kasancewar tun jiya ya dawo da daddare bai sameta ba .
Ko sallama baiyi ba yafara kai mata duka da carbi da gudu tayo waje bata tsaya ko ina ba sai zauren gidansu Ummi .
Jiyo kururuwar kuka yasata tsagaita nata kukan tana saurarar mai kukan , tabbas Ummi ce.
Ji tayi maman Ummi na cewa " dan ubanki tun baki tafasa ba zaki ƙone uban wa yabaki breziyar da nagani cikin kayanki , babu kowa mama Ummi tace " tana zabga ihu .
Jin saukar bulala yasa Aisha waigawa malam ne har zauren gidansu Aisha ya rufeta da duka.
Saida yayi mata lilis sanan ya koma gida inbaku manta ba dama yatafi da haushin gayan tuwo da ƙuli ,haka taja ƙafafuta ta koma gida , kai tsaye gurin kayanta ta nufa ta janyo breziyar data cire jiya ta ƙudundune a leda ta taje ramin wani bulo ta ɓoye .
Bayan duka ya baje mama ko uffan batace ba sbda itama yawon ya isheta , wanka Aisha tayi ta janyo kayan kwaliya tasa hoda da janbaki ta ciro atamfarta ta sallar bara ta sanya , ɗinkin yayi mata kyau sosai kasancewarta mai ɗan ƙiba kaɗan , Matsowa tayi gurin katangar gidansu Ummi tace " Ummi fito muje , Ummi dake sanya hijab tace " kifito ganinan .
Niko nace wai su basu gajiya ne ..
a tare suka fito kowanne mamansa na ɗakinta shiyasa suke samun damar ficewa , suna cikin tafiya kowacce na bada labarin dukan dayasha .
Ganin mai sai da kwakwa yasasu cewa tsaya zamu siya mai kwakwa da fara'arsa ya sauke yana cewa yan mata kunyi kyau sosai dazaku amince dani kowacce zan bata ƙwalon kwakwa bi biyu .
Sun gano mai yake nufi kasancewarsu masu shegen wayo kuma iyayensu na yimusu nasiha tun ba yau ba , mun anince bamu , kun amince fa kukace ?

Eh su Ummi sukace cikin haɗin baki , to kuzo muje ɗakina na gaban mai siyarda shayin cikin kasuwa , Aisha ce tace amma babu mutane ko ? eh ba kowa ma gurin . to muna zuwa bari mu zo , suka nufi zauren gidansu Aisha tare da ɗauko wani abu a baƙar leda da basa rabo fashi  komai runtsi .....!

Shar'hi yayi low🏃

*MOM ISLAM*
[14/07, 7:54 am] Mom Islam Ce🌹: *YARINYA MAI TAƁARGAZA*

Typing✍.

STORY AND WRITING
BY
*Zainab habib [mom islam]*

*[AREWA WRITER'S ASSOCIATION]*

Telegram links https://t.me/joinchat/IaKr804dfndik1e2

Wattpad momislam 2020

FREE BOOK📚

*BISMILLAHIR RAHMANIR RAHIM*

Page 13 & 14

Da wowa sukayi gurinsa suka ɗunguma zuwa ɗakinsa  , ganin sunja sun tsaya yasa mai kwakwa cewa " kushigo man babu kowa , shigewa yayi da tiren kwakwarsa ya fara cire riga yana shirin cire wando Aisha ta kutso kai tana riƙe da hanun Ummi sai da suka bari ya cire wando saura gajere yana yimusu dariya suka fesa masa ƙarara wato wanan abin  mai ƙai ƙayi , wani razanannen ihu mai kwakwa yasa tare da cewa " ubanku dan uwarku yana susa yana rawa , Aisha ganin abin yafara aiki yasasu kama yin rawa suma , har kwanciya yayi a ƙasa yana birgima amma babu wanda yasan yanayi bare a kawo masa agaji , yayi nan da gudu yayi can da gudu kamar sabon kamu .
Shigewa gurinda ya ajiye tiren kwakwa sukayi yanaji yana gani suka kwashi ƙwalo uku manya , sai yayi kamar zai hanasu sai ƙai ƙayi yayi masa sallama .
suna cin kwakwa suna cewa oya shoki shoki suna jefa ƙafa , nufosu yayi da gudu suma suka ɗiba da  gudu suna haki . basu tsaya ko ina ba sai a ƙofar gidansu .
Ummi ce ta jiyo hayaniya daga gidansu , Aisha zomuje ana faɗa a gidan mu
Suna shiga sukaga maman Aisha da maman Ummi ke faɗa , maman Ummi ce tace " wlh yarinyarki kesa Ummi yawo kuma anyi na farko anyi na ƙarshe tunda bazaki jawa yarinyarki kunne ba ,
Fitowa sukayi da gudu Aisha ta nufi gidansu Ummi ma binta tayi ganin Aisha ta ɗibo ruwa a bokiti yasa Ummi cewa mezakiyi Aisha ?" Aisha dake kuka tace " raina ya

ɓaci Ummi meyasa zasu dinga faɗa ruwa zan kwara a katifarsu , kema jeki kwara a ta mamanki .
Cikin azama Aisha ta sheƙa ruwan a katifar tana haki , zuciya ce ta ɗibi Ummi itama taje ta faki idonsu ta sheƙa a katifar mamanta wai a dole ransu ya ɓacci lolz.
fitowar maman Aisha ne yasa Ummi shigewa gidansu , tana shiga mamanta tahauta da masifa wai yanzu ta ɓaci da yawo tana biyewa Aisha , haƙuri Ummi tashi ga badawa harda yar ƙwallah , shiru maman nata tayi alamun ta haƙura hakan yasa Ummi shigewa ta zauna tana tuno mai kwakwa , kwashewa tayi da dariya harda tafawa ta fito da gudu kamar wacce aka zabura ta leƙa gidansu Aisha ta katanga tana cewa Aisha ya mai kwakwa , sheƙewa da dariya sukayi suna ƙarawa .

*WASHE GARI DA RANA*
Zaune yaya Zakari yake gaban iyayensa yana gaya musu yanason yin aure , malam dake jan carbi yace " wato kai ka riƙa harda iya zuwa mana da zancen auranka?
Mama ce ta katse malam da cewa " yaronnan fa inza 'ayi adalci to abin abinda yakeso shiru malam yayi batare da ya ƙara bi takan mama ba , ya janyo buta ya kuskure baki yayi gaba .
Mama ce ta dubi yaya Zakari tace " kayi haƙuri zani ƙauye gurin yayana inyimasa magana karka damu , kan yaya Zakari a sunkuye yace " to mama.

*ISLAMIYA*
Kowa ya sansu walau malami ko ɗalibi ko sunyi latti ba'a dukansu babu ma mai kulasu .
Suna shigowa cikin islamiyar suka tarar anyi sabon malami zasu wuce ya daka musu tsawa tare da cewa " ku tsuguna ku ɗaga hannu sama tsabar baku da kunya zaku wuce kai tsaye .
Wata uban hajijiya Aisha tayi sai ga........!

Muje zuwa fans

More comments more typing✍.

in naga shar'hi zakuga sabon update anjima

*MOM ISLAM*
[14/07, 7:55 am] Mom Islam Ce: *YARINYA MAI TAƁARGAZA*

Typing✍.

STORY AND WRITING
BY
*Zainab habib [mom islam]*

*[AREWA WRITER'S ASSOCIATION]*

Telegram links https://t.me/joinchat/IaKr804dfndik1e2

Wattpad momislam 2020

FREE BOOK

*BISMILLAHIR RAHMANIR RAHIM*

Page 15 & 16

Jin saukar duwatsu yayi a jikinsa, Aisha na tabbatar da yaji zafi tace " Ummi ga naki .
Ganin zasu yi masa illa yasa shi binsu da gudu su kuwa suka fice waje , suna gudu malam na gudu .
Ummi ce tace " Aisha taro mai ayaba aikuwa cikin ankara ta janyo tiren mai ayaba dama da akwai ɓararun ɓawo ta wurgawa malamin cikin sa'a ya taka ya sule , sukuma suka yi hanyar gidan su kowacce na maiyar da nunfashi .
Zaune malam yake yana aikin nasa wato jan carbi, duban mama yayi yace " a ina aka tsaya ?" mama da bata fahimta ba tace " ban gane ba , ai bazaki gane ba cewar malam.
Shiru mama tayi dan ance faɗan da yafi ƙarfinka sai ka maidashi wasa . sai da malam ya gama jan carbinsa sanan ya juyo yace " ba yaronki yace " aure yakeso ba ? uhm mama tace " tana nazarin irin maganar da zata faɗawa malam.
Amman kasan ba yabon kai ba Zakari ya mallaki hankalinsa bugu da ƙari yanada gini nasa na kansa bayan haka kuma yanada zuciya dan wanan aikin garejin da kake rainawa yana temakonsa bama shi kaɗai ba har mu .
To to to naji zabiya mai yabo inhar ya tara kuɗin aure yazo zanyi masa amma nikam banida kuɗi .
Shigowar Aisha da gudu ne ya katse musu zance ta shige ɗakin da yake a mazaunin nata da gudu tana haki .
Kingani ko wlh da yarinyar nan zata sami miji aurar da ita zanyi .
zaro ido mama tayi cikin mamaki tace " wanan wace irin magana ce ? yarinyar da ko shekara goma sha ɗaya bata cika ba kace aure zakayi mata ?" to wlh bazan lamunta ba ehe wane marar lissafin ne zai aureta , jin mama tahau masifa yasa malam jan baki yayi shiru amma cikin zuciyarsa har ga Allah Aisha ta ishe shi yanzu .
Ta taro takalmansa yayi ya fice yana mita , miƙewa mama tayi ta shiga gurin Aisha , samunta tayi zaune tana maida nunfashi .
Keda waye ? cewar mama
Babu kowa mama rige rige mukayi shine na riga Ummi zuwa gida , janyota mama tayi ta kwantar da ita kan cinyarta tace " yar albarka , na'am Aisha cewar Aisha .
Maiyasa kikeson ganin ɓacin raina ? ko kinfiso indinga kuka kullum .
Haɗe rai Aisha tayi kana tace " mama ki yafe min nadena in Allah ya yarda .
Cikin farinciki mama ta rungumeta tanajin son autar tata a cikin zuciyarta .
Aslamu alaikum mama ta jiyo sallama .
Wa'alaikumussalam cewar mama kashigo man.
Shigowa yayi Zakari yayi yana kallon Aisha dake kwance a jinyar mama , mama ina wuni cewar yaya Zakari.
Lafiya lau ya aiki,
yaya Zakari ne yace " aiki alhmdulilh ya kukayi da malam?
Bayanin da malam yayiwa mama tayi masa dariya yaya Zakari yasa , abin yaba mama mamaki amma sai ta tambayesa tace " lafiya kuwa ?
lafiya mama wato malam tun yanzu ya fara karaya kenan ikon Allah mahaifinka ma kenan yayima haka bare wani , to yasha kuriminsa na tanadi komai jiya aka yiwa gidana fenti ansa komai , kuma na gayawa ogana yace " duk abinda nake buƙata kar naji nauyinsa in gaya masa ɗazu ma yabani kyautar dubu ɗari da hamsin yace " inkai sadaki , wasu hawayen farinciki ne suka ziyarci kumatun mama tare da ɗaga hannu sama tana yiwa Allah godiya ,
Aisha dake kwance tace " wlh kudena yarda malam yanada kuɗi masu yawa a ɗakinsa shiyasa baya bari kowa yana shiga .
Ina ne ɗakin nasa da ya wuce na mama ?" yaya Zakari ya katse ta .

Ka mance ɗakin dabobinka da ya mayar ɗakinsa ku jirani .
Binta kawai sukeyi da kallo babu wanda ya tambayeta ina zataje suna zaune sunyi jugum.....!

Nagode na ƙin yin comments wlh badan haƙuri da aka bani ba nadena typing ɗin book ɗinnan raina yana mugun ɓacci shiyasa ko nayi tunanin ƙara yawan rubutun nake fasawa tunda bakusan maiyi muku ba typing ɗin littafin kuɗi nakeyi na ajiye shi nake yimuku wannan shima kuma ina yinsa duk baku godemin ba , am sorry to say gobe da jibi da gata kai har one week bazaku sami typing ba nabarku lafiya 🙏.

*MOM ISLAM*
[14/07, 7:55 am] Mom Islam Ce🌹: *YARINYA MAI TAƁARGAZA*

Typing✍.

STORY AND WRITING
BY
*Zainab habib [mom islam]*

*[AREWA WRITER'S ASSOCIATION]*

Telegram links https://t.me/joinchat/IaKr804dfndik1e2

Wattpad momislam 2020

FREE BOOK🙏

*BISMILLAHIR RAHMANIR RAHIM*

Page 17 & 18

Suna zaune sai gata da wata jaka mai kamada algara ra an ɗaure bakinta da zaren lilo , buɗe baki mama tayi tace " Aisha a ina kika samo wanan abin haka ? Aisha da gumi yafara rufeta tace " wanan fa kuɗi ne a ciki kuma wlh masu yawa ku kunce ku gani , a tsorace mama ta ɗagawa yaya Zakari hannu dan yana shirin karɓar jakar , karka sake ka karɓi wanan jaka itama tazo ta mayar inda ta ɗauko , haɗe rai Aisha tayi kana tace " tsoronsa ku keyi ne ? taɓɓ kunce jakar tayi ta zazzage duka kuɗin a ƙasa da mamaki mama ta dubi yawan kuɗin da a kinta tawa zai kai sama da dubu hamsin tace " Aisha ban isa dake ba ko amma me na gaya miki ? bakida gudun magana ko ? shidai yaya Zakari kansa na ƙasa bai ce komai ba kuma bai ɗago ya dubi kuɗin ba , ana haka suka jiyo sallamar malam , ba Aisha da ke tsaye ba harsu mama gaban su na dukan uku uku tabbas sun shiga uku yau kam , girgiza kai malam ya shiga yi tare da cewa " a lallai ashe dama bincike kuke yimin a ɗaki in bana nan ? Aisha na shirin magana ya zula mata carbi tare da sunkuyawa ya tattare kuɗaɗen ya tura a jakar da Aisha ta fito da ita , to wlh karkuga ko dan kunga kuɗinnan kuce nerata zatayi ciwo hukuncin masu bincike kenan munafukai daga haka ya wuce da kuɗinsa zuwa ɗaki .

Gumm Aisha tayi tana zaro ido kuma taci alwashin ɗaukar kuɗin ankon bikin yaya Zakari a ciki koda za'a kasheta.

Ɗan uwan mama yazo daga ƙauye sunje sun tambayo auran Fiddausi mahaifinta yace " inda hali bayason bikin ya wuce wata ɗaya , wata uwar zufa ce ke karyowa malam sbda a tunaninsa shine zai yi komai .
Ji yayi ɗan uwan mama yace " karku damu a shirye muke , wanan karon malam shiru yayi , sai rarraba ido ya keyi , bayan sun gama tattaunawa aka yanke lokacin biki nanda wata ɗaya bayan an bada dukiyar aure.
Tun a hanya da suka fito malam yafara masifa yana nuna ɗan uwan mama da carbi , kasancewar tafiyar ƙafa zasuyi yasa ɗan uwan mama yin gaba bai kula harkar malam ba.
labari yayi wa Fiddausi daɗi zata auri masoyinta , zaune suke ita da yaya Zakari suna hira , bayan shiru ya biyo baya yaya Zakari yace " inason in munyi aure ƙanwata ta dawo gidan mu da zama , kasancewar Fiddausi batasan ƙanwar tasa ba yasata cewa aiko danaji daɗi sosai wlh , nan suka ci gaba da hirarsu wacce rabi ta maganar bikin su ne.

Biki saura 2 weeks anata shirye shirye ta kowane ɓangare amarya tasha gyara ,su mama anata ƙoƙarin ganin an haɗa akwati malam ko baya magana ya zuba musu ido.
Aisha ce zaune a gaban mama tace " mama ni wai baza ayi min anko bane ?" dariya mama tasa tace " nima fa yayanki ne ya kawo min a ɗinke dan haka ki kwantar da hankalinki inada atamfa ragowar guda ɗaya sai ayi miki riga da zani .
kuka Aisha tasa tana ta turje turje tana cewa " wlh sai nayi anko wlh sai nayi , shigowar Ummi ne ya sata tsagaita kukan ta dubi Ummi tace " Ummi yau rabon mu da fita kwana uku kenan zomuje gidan dilaliya in kai mata wanan ƙyalen atamfar ko za'a samu a gidan ta .zaro ido Ummi tayi kana tace " Aisha a ina kika sami kuɗi ? ban sani ba in bazaki rakani bane to ki barshi .
Aisha ko da wasa kar inga ƙafarki ta taka waje dan zanyi miki duka ,
Dan ƙawa Ummi ƙyalen tayi tace " kije ki cewa dilaliya in akwai inaso wlh inhar bakije ba ko na siya bazan haɗa dake a ɗinki ba kuma kinsan sauran ,
Kasancewar a hankali Aisha ke maganar yasa mama bata jiyosu ba, ficewa Ummi tayi cikin rawar jiki ta doshi gidan dilaliya sallama tayi ,
Cikin sa'a ta sami dilaliya zaune a tsakar gida da bahon kaya a gabanta......!

*MOM ISLAM*
[14/07, 7:55 am] Mom Islam Ce: *YARINYA MAI TAƁARGAZA*

Typing✍.

STORY AND WRITING
BY
*Zainab habib [mom islam]*

*[AREWA WRITER'S ASSOCIATION]*

Telegram links https://t.me/joinchat/IaKr804dfndik1e2

Wattpad momislam 2020

FREE BOOK

*BISMILLAHIR RAHMANIR RAHIM*

Page 19 & 20

Ina wuni an aikoni  cewar Ummi , dillaliya ce tace " lpy daga ina ? cewa akayi in tambayo ko akwai wanan atamfar ? eh kin koyi sa'a saura tirmi ɗaya, nawa ce Ummi tace "jikinta na rawa .
Dubu uku da ɗari biyar cewar dillaliya , to Ummi tace " bari inje in gayawa wacce ta aikoni Ummi ta fice da gudu zuwa gidansu Aisha,
Ganin Aisha a tsakar gida yasata cewa " Aisha wai dubu uku da ɗari biyar , ƙaraso ki zauna babu kowa a cikin gidan mama ta tafi kasuwa , zama Ummi tayi tana rarraba ido , miƙewa Aisha tayi ta nufi ɗakin ajiya , bata wani jima ba sai gata da dubu biyar a hanunta , zaro ido Ummi tayi tace " Aisha sata ? shittt kiyi shiru kuɗin malam ne bayaci sai tari zomuje suka fice ammafa gaban Ummi na dukan uku uku, kai tsaye gidan dillaliya suka nufa Aisha ta miƙa dubu huɗu aka basu canjin ɗari biyar , suna fitowa suka wuce gidan mai ɗinki Aisha ce tace " ayi mana mu biyu , mai ɗinkin ce ta dubesu tace " bazai isheku ba sai dai ayi muku ƙari da wani abun , sun yarda a hakan, mai ɗinki ta buƙaci dubu ɗaya , miƙa mata Aisha tayi suka fice , idanun Ummi cike da hawaye tace " Aisha bakyajin tsoron malam ko ? nidai babu ruwana , tsaki Aisha tayi kana tace " ina ruwana nida zan koma gidan Yaya Zakari zaku dena ganina , dan Allah can zaki koma ? cewar Ummi eh man sai ma ranar tazo .

Yau kwana goma da ɗaukar kuɗin Aisha kasancewar malam ba duba kuɗin yakeyi ba yasa bai san abinda ya faru ba , biki saura kwana huɗu baƙi sun fara cika gidan su Aisha yaya Zakari yayi bakin ƙoƙarinsa gurin yiwa ɗakin mama fenti .
Bayan sun karɓo ɗinkin ta wuce dasu ɗakin mama , mama na zaune tana duba kayan akwati taji an jefo mata leda , duba ledar tayi tana ganin anko ta ɗago kai tare da cewa " na waye ? dariya Aisha tasa tace " nawa ne mama zokiji , dai dai kunnen mama taje tayi mata raɗa wanda nima banji me akace ba ,
Faɗa mama ta hauta da shi kamar zata daketa sai da mutane suka dinga bada haƙuri , buɗe kayan mama tayi ganin dogayen riguna har biyu yasa mama cewa " to ya naga kala biyu , Aisha ce tai carb tare da cewa ta Ummi ce jin jina kai mama tayi kana ta miƙe ta nufi katangar gidansu , tana ƙwalawa maman Ummi kira .
Leƙowa maman Ummi tayi tare da cewa "mama ya taro ?alhmdulilh mama tace " kana ta miƙawa maman Ummi ɗinkin Ummi , cikin farinciki maman Ummi ta karɓa tana cewa waye da  wanan abin alherin ? hmm mama tace " kedai bari yanzu inada mutane zan baki labari bayan taro ya watse , maman Ummi tace " ganinan shigowa ma.
Daga haka kowa ya kama gabansa .
Fiddausi tasha lalle ba ƙaramin kyau tayi ba , yau ake walima kowa ya sanya albarka kasancewar yaya Zakari yace " baya son bidi'a gobe ɗaurin aure gidan su Fiddausin ma a cike yake da yan biki anata suyar cin cin ana wasa ana dariya .
Tun a daren yau Aisha tafara haɗa kayanta a jaka babu abin da ta bari komai ta tattara , Ummi dake Ummi dake zaune gefen Aisha ta zuba tagumi da alamun damuwa tace " yanzu Aisha tafiya zakiyi ki barni , itama Aishan nanda nan ta shiga damuwa ta rungume Ummi tare da cewa " kema ai zaki dinga zuwa muna gaisawa kuma zamu dinga haɗuwa a makaranta ko ? girgiza kai Ummi tayi alamar eh .

*WASHE GARI WEEDING*

Ranar asabar.

Duban jama'a suka sheda ɗaurin auran Zakari malam Abdullahi da Fiddausi Umar anyi ɗaurin aure cikin farinciki da ƙaunar juna.
Da yamma motocin ɗaukar amarya suka zo tunda Aisha taji labari ta fito da jakarta .....!

Fans kuyi haƙuri yau ɗinnan banajin daɗi wlh ciwon kai gashi ma banyi typing da yawa ba innaji sauƙi anjima zakuga wani jinjina ga masoya masu son ganin farinciki na nagode da shar'hi 🙏🙏.

*MOM ISLAM*
[14/07, 7:56 am] Mom Islam Ce🙏: *YARINYA MAI TAƁARGAZA*

Typing✍.

STORY AND WRITING
BY
*Zainab habib [mom islam]*

*[AREWA WRITER'S ASSOCIATION]*

Telegram links https://t.me/joinchat/IaKr804dfndik1e2

Wattpad momislam 2020

FREE BOOK📚

*BISMILLAHIR RAHMANIR RAHIM*

Page 21 & 22

Jin ance ai har an gama kai amare hankalin Aisha ya tashi ta shiga kuka , mama da keta fama da jama'a tace " kai Aisha menene kuma? cikin she sheƙar kuka Aisha tace " ba su yaya bane suka tafi suka barni , riƙe baki mama tayi kana tace " to ke banda abinki daga ɗaurin aure zaki koma gidan ? eh mama shine yace " zai ɗaukeni dariya mama tasa tace " yaro yaro ne ai kafin ki tafi sai kin amsa laifinki gurin malam bazaki janyo min fitina ba , rau rau Aisha tayi da ido ita yanzu duk damuwarta kawai ta ganta gidan amare gashi dare nayi .
Mama tayi rarrashin amma ina fur taƙi saurarar ta haka ta koma ɗaki ta barta a gurin Ummi kam tun ɗazu ta tafi , Aslamu alaikum , yaya Zakari yace " shida abokansa suna sanye cikin shadda mai ruwan ƙasa kowannen su ba ƙaramin kyau yayi ba , bayan su mama sun amsa sallamar ne yaya Zakari ya dubi mama kana yace " mama ki yafemin dan Allah sai kuma ya hau share hawaye , itama maman kuka takeyi ta kunto gefen zaninta tana cewa " na yafe maka Allah ya albarkaci auranku, amen y Allah suka amsa .
Hango gimbiya yayi da jakar kaya a gabanta ta zuba uban tagumi tana gyan gyaɗi , keee ...yaya Zakari ya kira sunan ta , tashi kije ki kwanta murmushi mama tayi tana jira taji inda za'a kaya , cuno baki Aisha tayi tare da buga ƙafa tana cewa " wlhi

ƙafata ƙafarka ai kai kace  zan koma gidanka akwai ɗakina acan , dariya suka sa shida abokansa suka ce to taho mu tafi .
Lokacin ƙarfe goma na dare gari ya yi shiru haka suka shiga motar abokinsa suka wuce ,sai da aka biya gurin Lawali mai kaza , tunda sukazo gurin Aisha ke ɓoye fuska har suka wuce , sun ɗanyi tafiya mai nisa kana suka iso anguwr  parking sukayi a gefe da ƙofar gidan suka fito Aisha ma fitowa tayi da jakarta a hannu , yaya Zakari ne ya ƙarɓi jakar yace " zai sanya mata a ɗakinsa , suka ɗunguma zuwa ciki , gidan ya tsaru gidane mai ɗakuna biyar kowanne ciki da palo kowa da nasa dakuma kitchen da ɗakin baƙi masha Allah gida yayi kyau tsakar gidan yasha siminti ,
Yana riƙe da hanun Aisha suka shiga tun daga palo suketa jin surutan ƙawaye.
Kai tsaye da shi da abokan suka shiga cikin ɗakin , amarya Fiddausi na luluɓe cikin zani yayin da ƙawayenta ke gefe anata hira , suna ganin su yaya Zakari suka shiga wasa da dariya bayan anyi siyan baki abokan ango suka mayar da ƙawaye gida , ɗaki ya rage daga Fiddausi  sai yaya Zakari da Aisha , matsowa yaya zakari yayi tare da buɗe mayafin Fiddausi amarya bakya  laifi  zaro ido Aisha tahauyi tana rarraba ido , Aisha tashi muje in rakaki ɗakinki ki kwanta , kuka Aisha tasa tana cewa " nidai anan zan kwana , Fiddausi ce ta buɗe ido kana tace " ƴan mata dan bata lura mutuniyar ta bace  kabarta mu kwana man my sweety , kashe mata ido yaya Zakari yayi tare da janyo hanun Aisha cikin wayo ya fito da ita ya kaita ɗakin da yake a mazaunin nata , miƙa mata sweet ɗin da ya siyo mata yayi tare da yimata adu'a ya rufo mata ƙofa bayan yagama lallashin ta , ya fito ya janyo mata ƙofar ya dawo ɗakin amarya , samun ta yayi tana zaune da waya a hanunta , to na lallaɓo ƴar rigima , ya rungume Fiddausi kana ya raɗa mata ,tashi  muje muyi alwalah  babu musu ta miƙe tayo alwalah shima yayi ya shinfiɗa musu sallaya kana ya shige gaba ya tada sallah yana yin sallama yafara jero adu'oi itama haka , dafa kanta yayi kana yayi mata adu'a tare da sa albarka  , tsabar zumuɗi yaya Zakari ya riƙe baki tare da cewa "afuwan sweet ban ɗauko miki abinci ba murmishi Fiddausi tayi batare da tace " komai ba  fitowa palo yayi ya ɗauko musu cup da plet da fresh milk ya dawo janyo ledar kazar yayi tare da juyeta a plet ya shiga ciyar da ita bata wani ci da yawa ba ta ture hanunsa , ya ɗago hannu zai kai bakinsa ta amshe tafara bashi , bayan sun gama yana shirin miƙewa kai kayan da sukayi amfani dashi ta karɓa ta kai , tana dawowa ya ɗagata can ya direta a bed ja musu blanket yayi tare da rungumeta ......!

Afuwan banida lafiya ne fans ina godiya da irin soyayyar da kuke nunamin kuyimin adu'a tare da suburbuɗo shar'hi .

*MOM ISLAM*
[14/07, 7:56 am] Mom Islam Ce: *YARINYA MAI TAƁARGAZA*

Typing✍.

STORY AND WRITING
BY
*Zainab habib [mom islam]*

*[AREWA WRITER'S ASSOCIATION]*

Telegram links https://t.me/joinchat/IaKr804dfndik1e2

Wattpad momislam 2020

FREE BOOK

*BISMILLAHIR RAHMANIR RAHIM*

Page 23 & 24

Haɗe fuskarsu yayi guri ɗaya yafara aika mata da hot kiss jin shigowar mutum yasa yaya Zakari miƙewa babu shiri kamar marar gaskiya , Aisha meya fito dake cikin wanan daren ? kuka shaɓe shaɓe a idanunta tace "yaya nidai bazan iya kwana ni kaɗai ba , mitsw Fiddausi tsaki tare da ɗago kai tana ƙarewa Aisha kallo , tabbas kamar tasan fuskar nan amma ta rasa a inda ta santa , janyo yaya Zakari Fiddausi tayi ya faɗa jikinta ta luluɓesu har kansu , Aisha dai na tsaye jin yayan nata bai ce komai ba ya sata neman guri a ƙasa ta ƙudun dune tana kuka ƙasa ƙasa , can a cikin bacci taji ana ihu farkawa tayi a firgice amma ɗakin duhu babu haske , wayo mama nidai a kaini gida wlh bazan zauna ba .
  Su basu san ma tanayi ba dan basajin ɗuryar Nigeria , ihun da Fiddausi ta saki na ƙarshe ne yasa Aisha takurewa gefe tana share guntun hawaye tabbas tayi dana sani kodai anty Fiddausi ta mutu ne yaya yana bacci , tunani Aisha ta shigayi marasa kan gado , jin ana cewa " my Fiddy kin biyani Allah yayi miki albarka banida bakin gode miki , yaya Zakari ya ma mance da Aisha a ɗakin yanata surutansa itama Fiddausin ta mance da Aishar tace " my Zak wlh nasha wuya gaskiya baka tausaya min ba , duk cikin duhu suke wanan surutan Aisha da tagaji da zama da kuka ta ƙara kwanciya tana matsar hawaye ,
Yaya Zakari na miƙewa ya kunna light haske ya baiyana , hango Aisha yayi a kwance ta takure kamar mai jin sanyi ya waro ido tare da cewa" my Fiddy yaushe Aisha ta shigo ? nima dai ban sani ba Fiddausi ta faɗa cikin ƙarfin hali dan Allah ne kaɗai yasan zafin da takeji , wucewa toilet yayi kana yai wanka ya fito, ya ɗauki Fiddausi kamar baby ya kaita toilet ya sata a bahon daya tara mata ruwan ɗumi wani uban ihu ta kurma tare da cewa wayo zan mutu , karab a kunnen Aisha ta miƙe a zabure tana waige waige , ganin babu kowa a ɗakin ya sata miƙewa tana lalube ta kunna wutar palo ta fito ta koma ɗakin da aka zaunar da ita daga farko.
Zama tayi tana tunanin kodai yaya Zakari yakai anty Fiddausi asibiti ne dan taga kamar batada lafiya kasancewarta ƙarama batasan aure ba duk hatsabiban cin ta , abinda ta sani shine faɗan da mama take yimata akan karta bari namiji ya riƙe mata hannu koda wasa , haka dai takuma komawa bacci rabi da rabi har asbha tayi , jin ana buga mata ƙofa ya sata miƙewa da sauri ta buɗe ƙofar tare da cewa " ya jikin anty Fiddausi , kunya yaya Zakari yaji gani yake Aisha tasan abin da ya faru , taji sauƙi yaya yace " kana ya wuce masallaci , gari nayin haske Aisha ta ɗauki tsintsiya ta share gidan ta dawo ɗakin Fiddausi ta gaishe ta , kana ta nemi guri a ƙasa ta zauna mekika tsaya yi ? tamabayar da Fiddausi ta jefo mata kenan , babu komai Aisha tace " cikin tsoro , to maza ki koma ɗakinki dan yanzu yayanki zai shigo , jiki babu ƙwari Aisha ta miƙe ta koma ɗaki , tana zama tafara tuno abubuwan da sukeyi ita da Ummi , ƙwafa tayi tare da cewa " tabbas wanan antyn sai na koya mata hankali da 'alamu batasan ko waye Aisha ba.....!

Kuyi haƙuri banida lafiya naso nayi muku da yawa 😢.

*MOM ISLAM*
[14/07, 7:57 am] Mom Islam Ce: *YARINYA MAI TAƁARGAZA*

Typing✍.

STORY AND WRITING
BY
*Zainab habib [mom islam]*

*[AREWA WRITER'S ASSOCIATION]*

Telegram links https://t.me/joinchat/IaKr804dfndik1e2

Wattpad momislam 2020

FREE BOOK

*BISMILLAHIR RAHMANIR RAHIM*

Page 25 & 26

Yaya Zakari na dawowa daga masallaci ya leƙa ɗakin Aisha kasancewar shine na farko kana shigowa , samunta yayi a kwance kan katifa ta ƙudundune da blanket kamar mai jin sanyi , wucewa ɗakin Fiddausi yayi tare da sallama a bakinsa , oyoyo my honey Fiddausi ta miƙe tare da rungum shi daɗi ne ya kama yaya Zakari cikin ranshi yace " aure ni'ima tabbas nayi dacen mata ,lol  na tanadar maka farinciki da safennan mijina , yaya Zakari bai ce komai ba sai bin Fddausi da ya keyi kamar jela , janshi tayi suka faɗa gado , Fiddausi ce ta tuno akwai yarinya a gidan hakan ya sata miƙewa ta rufe ƙofar kasancewar cikin ɗaki akwai ƙofa haka ma palo , dawowa tayi ta ƙara kai masa hug  shiko abin nema ya samu ai yafara ƙoƙarin rabata da komai na jikinta ,sai wani shi shige masa take niko nace" anty Fiddausi kamar ba amarya ba , kusan zaucewa yaya Zakari yayi dan duniyar da ya shiga ta yau daban da ta jiya , duk wata magiya da Fiddausi keyi akan ya ƙyaleta bai san ma tanayi ba kasancewar wani irin yanayi da yake ciki , ya daɗe yana sarrafa ta daga ƙarshe ya mirgina gefe , lokacin idon Fiddausi yayi jage jage da hawaye .
Aisha nata buga ƙofa shiru basu buɗe ba taja tsaki dan ita yanzu duk wani son zama da takeyi yanzu bata sha'awa tunda sun iya wulaƙanci , kitchen ta nufa tana dube dube  ganin robar yaji ya sata dariya tana cewa " duk mai wanka da mai fitsari zai yi a bonus , roba biyu ne yajin manya  ɗayar ta ɗauka ta je tankin ruwa ta , taka turmi ta buɗe murfin tankin ta juye yajin duka ta wurga robar ta bayan gidan nasu , ta gyara murfin tankin ta koma ɗaki ranta fess kamar anyi mata kyauta , shiru shiru basu fito ba har ta fara jiyo surutun su Fiddausi na cewa my sweet wlh ka wahalar dani  over ,oh sorry pls keɗin ce ta daban barinyi wanka in fito , no kabari inyi sbda inason inyima kwaliya kafin ka fito cewar Fiddausi  , ina jiranki my lovely  , tana saukowa daga gado taji ƙafafu sun riƙe babu hali gashi tashi ɗaya tafara jin zafi a ƙasanta , bazan iya tashi ba ,
Da sauri yaya Zakari ya temaka mata ta nufi toilet ɗin dake maraba da palo wato tsakiya ya dawo ya kwanta yana jiran fitowarta , dawowa palo tayi ta ɗauki flaks ɗin ruwan zafi ta rage  , tare da ajiyewa ta shige toilet ɗin ta rufo ƙofa , ruwa mai ɗan zafi ta zuba a baho ta shige ciki wani irin zafi taji ya ziyarceta ta ɗauka wuyar da gurin yasha ne , fita tayi a cikin ruwan takuma zuba wani , wani uban ihu ta kurma wanda yai sanadiyar fitowar Yaya Zakari ba komai a jikinsa , da gudu Fiddausi ta riƙeshi tana nuna masa gabanta , mai ya faru ? zafi zafi wlh akwai zafi nashiga uku

ka temakeni , zafi kuma na jiya baiyi zafi ba sai na yau zatayi magana taji kamar an watsa mata ruwan barkono ai da gudu ta shige toilet ta tari ruwa a buta tana tsarki , nanfa abu ya girmama babu sauƙi wai ciwon arna yaya Zakari yarasa inda zaiyi da ita gashi yanason yin wanka , tana kukan ya shige toilet ya tara ruwan sanyi yafara tsarki ,bai kai ga fara wankan ba yaji yayi sallama , shikam tsalle ya shiga yi yana salati yana kiran Fiddausi da take ta lafta  basilin a gurin wai dan tadena jin yajin ,nata yaɗan ragu dan tayi shiru amma har yanzu bata nemi kaya ba bare maganar ƙara wanka, wani uban tsalle da yaya Zakari ya doka tare da cewa wai menene mai wanan yajin nifa ina zargin dangin ki ne basu wanke bokintan da kyau ba , dariya Fiddausi tasa tare da cewa alhaki na ne ai inata cewa ka ƙyaleni kaƙi gashinan muna jin jiki ai kuma wlh in kayi wasa aljanuna mugaye ne babu abinda basuyi , yaya Zakari dake rawar yaji ya zaro ido yana kallon Fiddausi , to gara mu fara kiyayewa tunda kinada hatsabibai a kanki nidai nafi ƙarfinsu wlh, duk wanan maganar da ya keyi yanayi yana rawa , can jin yajin nasu ya lafa ,Fiddausi takuma nufar bayin tana cewa insha Allah ƙalau zan fito , tana shiga ta fara da wanke fuska a gigice ta fito tana cewa Zakari gidannan babu lafiya wayo Allah na tana cikin tafiya taci karo da bango takuma sakin wani sabon ihun .

Koda Malam ya dawo gida bai duba kuɗinsa ba sai da ƴan biki suka watse , saɗaf saɗaf ya shige ɗakin dabobin tare da turo ƙofa , ya nemi wata kujera ta katako ya zauna , zanyo jakar kuɗin yayi tare da kunce ɗaurin tun daga kan ɗaurin ya fara zargin an taɓa jakar  , beyi magana ba ya fito da kuɗin duka ya fara ƙirgawa , kambun uba kalmar data fito daga bakin malam kenan wato an fara yimin sata ko ? dan wanan ba ƴan biki bane ƴan gidanne , ya tura kuɗin da ya ciro dakuma wasu a aljihunsa ya haɗa ya maidasu ma'ajiyarsu tare da sanya ɓawon masara akai wai duk dan ya gane ko an taɓa kuɗin , da sauri ya fito da carbi a hanunsa ya nufi ɗakin mama daketa baccin gajiya , gurinki nazo wato bakuda godiyar Allah duk uban gudun mawar da kika samu gidan wa kika kaishi ? abin ma harda sata to wlh bazan lamunta ba adinga sacemin kuɗi ko nace " ku nake tarawa ? tun wuri karki ƙara kuma hukunci na gaba na dena bada kuɗin cefane har sai anyi wata biyu , a hakan ma nayi mutunci .
Mama dai na jinsa batace komai ba dan bacci ne  a idonta shigowa ciki malam yayi tare da cewa " wato kin maidani mahaukaci ko inata magana kamar inayi da dutse to wlh duk munafurcinki sai dai ya ƙare miki , kuma naga an kawo miki dankalin hausa dama kafin in dawo ki dafa shi ba siyan ƙuli za'ayi ba iyakaci kisa gishiri , har yanzu mama batayi magana ba tana dai kallonsa dariya ma yaso bata yanayin abu kamar wani zautacce.....!

*MOM ISLAM*
[14/07, 7:57 am] Mom Islam Ce: *YARINYA MAI TAƁARGAZA*

https://www.youtube.com/channel/UCcAjVQ74qod9_dL0e_AqkiQ

*DUNIYAR LITTAFAN HAUSA TV*

*Zainab habib [mom islam]*

*[AREWA WRITER'S ASSOCIATION]*

Page 27 & 28

Bayan sun gama rawar yaji Aisha ta fito sanye da kayan islamiya a lokacin ƙarfe sha biyu , ɗakin anty Fiddausi ta nufa inda ta shiga da sallama batayi aune ba ta hango yaya Zakari rungume da anty Fiddausi , zaro ido Aisha tayi tare da rufe baki suna hirar su ko sallamarta basuji ba , dama yaya kai ɗan iska ne ? batasan lokacin da tayi maganar ba kasancewar a cikin zuciyarta take maganar , mekikace ? Fiddausi ta jefo mata tambayar tare da shirin miƙewa , no ƙyaleta yarinya ce batasan komai ba , sai yanzi Aisha ta tuno ashe tayi TAƁARGAZA juyawa tayi zata fice yaya Zakari yace " ina zuwa na ganki da kayan islamiya ko abincin rana baki ciba ? daga nan zan wuce gidan mama ne ta bashi amsa ,Fiddausi ce ta kalleta tare da cewa aiko sai kinci abinci dan bazaki tafi da yunwa ba , Aisha dai zaman gidan ya isheta dama so takeyi da zarar ta tafi gida bazata dawo ba , jininsu bai haɗu da anty Fiddausi ba ko kaɗan , komawa ɗakinta tayi tafara kuka tana cewa " ɣan iska kawai sai da suka gama iskancin su zasu bani abinci to wlh sukayi wasa har su bazasuci ba ashe dama yaya ɗan iska ne ban sani ba tabb , jin sunata dariya har da tafawa yasa ta ƙara tabbatarwa ɣan iskan ne da gaske kasancewar a islamiya ana yimusu wa'azin babu kyau namiji ya riƙewa mace hannu to su gasu a cinya ma taga yayanta kamar jinjiri , tunowa tayi ba tada biron rubutu dan haka ta koma kai tsaye ɗakin anty Fiddausi ba tare da tayi sallama ba , sun koma kan kujera suna kallo a TV hanun yaya a kafaɗar Fiddausi hakan ba ƙaramin haushi ya bata ba , ficewa tayi yayan na kiranta bata saurareshi ba ta fice waje ,ta nufi wata ɣar makaranta ta almajirai dake ƙofar gidansu , kuzo ku karɓi sadaka ta kirasu zasuyi su biyar da gudu almajiran suka biyota suna murna , direct kitchen ɗin dake jikin ɗakinta ta nufa ta buɗe tukunyar da anty Fiddausi ke dafa taliya sbda ƙawayenta zasu zo yasa take dafa leda biyu , sauko da tukunyar tayi ta ɗauki abin ɗiban abinci tafara karɓar robar kowa tana zuba masa , duk wanda tasa masa sai yace " Allah shi karɓa har abinci yazo ƙarshe saura kaɗan a tukunya , dai dai Fitowar anty Fiddausi tana dariya tayi arba da aika aikan da Aisha tayi mata , salati tafara tana tafa hannu tare da riƙe baki tace " Aisha mezan gani kodai bakida lafiya ne ? lafiyata ƙalau Aisha tace " tana cigaba da suɗe ragowar ta tukunyar , to me nayi miki da zaki rabar min da abinci dan mugunta ? cewar anty Fiddausi .
malamin islamiyar mu yace " in ka ɗauki sadaka kabawa almajirai Allah zai yafe maka laifukanka gaba ɗaya shiyasa nayi haka naga kunada tarin zunubai ke da yaya , hakan karaf a kunenen yaya Zakari ya matso tare da cewa " Aisha wane zunubi kikaga munyi dahar zaki yiwa antynki haka , kuka Aisha tasa tana cewa " nidai bazan zauna a gidanan ba wlh mama tace " abokin ɗan iska shima ɗan iska ne , baƙin ciki da takaici ya ishesu su basu fahimci abinda take cews ba , yaya Zakari yace " kar in sake jin maganar komawa gida a bakinki dan anan zaki zauna har girmanki kinyi na farko kinyi na ƙarshe duk ranar da kika ƙara bada abinci batare da kin tambaya ba jikinki zai gaya miki , islamiya kuma kibari zan saki a ta nan anguwar inna sami kuɗi.Fiddausi dai na tsaye ranta in yayi dubu ya ɓaci dan yanzu ji take ta tsani Aisha sosai, jiyo sallama ƙawayenta yasa ta yi musu oyoyo yaya Zakari ya gaishe su ya fice yabar Aisha da Fiddausi da ƙawayenta anan gurin , shigewa ɗaki sukayi tare da rangaɗa shewa suna tafawa , Fiddausi ce tace " sai ku shiga kitchen ku ɗora girki cikin farinciki suka shiga hada hadar ɗorawa bayan sun gama haɗa komai na girkin suka koma ɗaki suka ja ƙofa suna tambayar Fiddausi ragowar kaza , Aisha na tsaye inda take bata ko motsa ba ta tuno ai da ita aka siyo wanan kazar kan uban yasin sai nayi aika aika yanzu ma ko za'a kasheni , kitchen ta

nufa tare da leƙawa ko suna shirin fitowa , cikin sa'a tajisu shiru , robar gishiri da robar suga ta nufa ta saka kowanne ludayin shan kunu  kowanne ɗaya ta fito ta nufi ɗakinta , cike da kewar Ummi , kuka tasa tana shu shura ƙafa tana cewa " ni wlh a mayar dani gida , babu wanda ya jita hakan yasa ta ƙaraci shirmen ta tayi bacci , ƙawayen Fiddausi na zuwa kitcen sukaga ruwa na tafasa , farke ledar indomie irin manyan nan guda huɗu sukayi aka saka tare da ƙara mangyaɗa suka kuma komawa , bayan mintuna ƙalilan ɗaya ta fito dubawa , cikin sa'a ta samu ta tsotse kwasheta tayi a baban faranti aka nufi ɗaki da ita aka kuma rufo ƙofa , cikin nishaɗi aka zauna ci harda Fiddausi , lomar da Fiddausi zasu kai ita da wacce ta sako abincin suka kasa ban bance wabinda yafi yawa a ciki ga suga suga gakuma gishiri gishiri , yau nashiga uku Lawiza gishiri kika cika a girkin ne ? Lawiza dake shirin yin amai tace " iya fa magin indomie wlh , Fitowa Fiddausi tayi ta leƙa ɗakin Aisha samu tayi tama daɗe da bacci ga bushashen hawaye a fuskarta , juyowa Fiddausi tayi cike da mamaki ace jiya ruwan gidan akwai barkono yau kuma ace an faura mata gishiri kai da sake kodai masu ruqiyya suzo kokuma taje gidansu inyaso komai ya dai daita ta dawo bazata iya wanan wuyar ba. haka dai suka haƙura suka haɗa fresh suka sha duk da ruwan kanajin tashin yaji ta maƙogwaro , bayan anyi la'asar sukayi mata sallama  cika musu leda tayi da cincin dakuma dublan mai yawa suka wuce.
Yaya Zakari yana yin la'asar ya nufi gidansu inda daga shigarsa ya tarar da Ummi a gaban mama tayi shaɓe shaɓe da hawaye wai gurin Aisha zataje , dariya ma taso bashi  bayan ya gaishe da mama ta tambaye shi yasu Aisha yace " suna lafiya ya tambayi malam mama tace " malam ya fita inajin yayi nisa , Allah ya dawo dashi lafiya miƙo masa shinkafa da wake mama tayi wanda taji man ƙuli , dama ba wani abinci yaci ba dan Aisha tayi musu rabo basu shirya ba, haka ya dinga lodawa cikinsa abinci har ya ƙoshi ya rufe kwanon ya kai dubansa ga Ummi yace " itama Aisha tana nan tana kuka wai tanason dawowa to yanzu dai ki kwaso kayanki koda kala biyu ne inkikayi kwana biyu sai ki dawo , da gudu Ummi ta nufi gidansu tayi sa'a babanta na gida ta gaya musu basu musa mata ba kasancewar sunyi zaman arziƙi da su mama , aikuwa mamanta ta bata kayanta ta fito da gudu.
da gudu ta fito daga gidansu ta nufi gidansu Aisha jikinta na rawa , to taho mu tafi yaya Zakari yace " yana yiwa mama sallama , Allah ya kaisu lafiya mama tayi musu suka fice , da isarsu bakin titi mashin ya tare duk da tsakaninsu za'a kai ka a nera arba'in wani lokacin ma har hamsin , bawata tafiya mai nisa sukayi ba sai gashi sun iso , farinciki fal zuciyar Ummi zataga masoyayyar ta Aisha, bayan ya bawa mai mashin kuɗin ya riƙe hanun Ummi suka nufi gidan , da sallama suka shiga hanunsa ɗauke da jakar kayan Ummi , Fiddausi ta fito da gudu tayi arba  da Ummi riƙe da hanun yaya Zakari turɓune fuska tayi tare da cewa " lovley wanan kuma wacece ? dariya yaya Zakari yasa kana yace " wanan sister na ce   tazo tayi miki kwana biyu ne , murmishin yaƙe tace " to barka , har ƙasa Ummi ta durƙusawa Ummi tayi ta gaida Fiddausi  tanata rarraba ido burinta taga Aisha amma shiru.

Nagode da adu'arku gashi nasami lafiya fans.

*MOM ISLAM*
[14/07, 7:58 am] Mom Islam Ce: *YARINYA MAI TAƁARGAZA*

*Zainab Habib [Mom Islam]*

*Wattpad @momislam2020*

*AREWA WRITER'S  ASSOCIATION*

*29~30*

Aisha najin muryar Ummi ta fito da gudu tana cewa " wlh dama dan ke zan koma gida yanzu kam na fasa Aisha ta shiga rawa hanunta a na Ummi , yaya Zakari da anty Fiddausi sai kallonsu suke kwata kwata Fuskar anty Fiddausi babu walwala lura da hakan yasa yaya Zakari cewa muje ki bani abinci , suna tafiya Ummi da Fiddausi suka wuce ɗaki cike da murnar ganin juna ,suna shiga Aisha tace " bani labarin abinda ya faru bayan tafiya ta , ke nifa babu inda naje kuma kullum sai nayi kuka saboda ke , dariya Aisha tasa tace " kinga matar gidannan batada mutunci Allah yasa dai kinzo min da wanan abin da muka sawa mai kwakwa dan wlh sai na koya mata hankali , eh nazo da shi ke ai wanan abin ba ƙaramin hukunci yake ba , suka ɗan taɓa hirarsu , suna daga ɗaki Aisha ta jiyo shewarsu  kallon Ummi tayi tace " kinji yan iska ko wlh kullum cikin zunubi suke wai dan nayi sadaka da abinci ɗazu shine wanan masifaffiyar take ta yimin faɗa , ke har na tattara kayana gudun kar in kwashi nawa kason zunubin , Ummi ce tace " jiya anyi gurmi a gidanku Aisha tace mai ya faru ? nisawa Ummi tayi tace " ham ingaya miki malam ya duba jakar kuɗinsa babu wasu kuɗin kuma yace " ya dena bawa mama kuɗin cefane , zaro ido Aisha tayi tace " Allah sarki mama kiyi haƙuri nice na janyo miki kuma wlhi malam yaci bashi duk ranar da na dawo gida sai yayi dana sani , riƙe baki Ummi tayi tace " malam ɗin ? wlh Aisha karki fara kin mance wa'azin da akayi mana a islamiya? cewar Ummi .ke wa'azo dallah in ɓata min rai kikazo yi kitafi kina gani zai bar mama da yunwa , koda yake nan gidan ma bawani ci ake ana ƙoshi ba ni wlh yunwa ma nakeji , miƙewa Aisha tayi tare da cewa" barin je in nasami abinci in taho mana dashi , to Ummi tace " tana dubo garin biskit ɗin da ta ɗibowa mamanta bata sani ba , sallama Aisha tayi a ƙoafar ɗakin anty Fiddausi ta ƙwala ihu ta shiga tsalle tana bige bige , da sauri yaya Zakari ya buɗe ƙofar cikin fargaba yake tambayarta lafiya ? Aisha dake ta mutsuka ido tace " yaya ruwan tankin nan wallahi akwai barkono naje wanke ido naji yaji kuma yunwa ma mukeji , anty Fiddausi dake kwance ta miƙe tare da cewa " yunwa ko to wlh sai dai kushiga kitchen ɗin amma badai niba , yaya Zakari ne ya kalleta yace " haba yaran nan har guda nawa suke da zasu shiga kitchen ? juyawa anty Fiddausi tayi ba tare da ta bashi amsa ba , Aisha dai na tsaye riƙe da ido gakuma hawayen dole , girgiza kai yaya Zakari yayi ya nufi gurin fampo ya buɗe ruwan dama ragowar babu yawa ruwn ya wuce ta rariya yafara ƙoƙarin tara wani , juyowa yayi gurin Aisha yace " ina Ummi ? gani Ummi ta fito da gudu , ku shiga kitchen ku dafa ko shinkafa ko taliya babu abinda babu kuci ku ƙoshi kunji ? eh sukace  ruwa na cika ya kashe yace " ni zan fita sai dare zan dawo , Allah ya kiyaye sukayi masa tare da shigewa ɗaki shikuma ya koma ɗakin anty Fiddausi yayi mata sallama , gani yamma tayi yasa Aisha fitowa tace " Ummi zo kiyimin jajjage nikuma zan soya mai , risho Aisha ta kunna ta ɗauko tukunya pot a ƙalla za'a iya kiranta da lamba biyar ta ɗora , galan ɗin man gyaɗa ta buɗe tare da tsiyayar rabi ta kawo murfin ta rufe man nayin zafi tasa albasa gidan ya buɗe da ƙamshi , Fiddausi dake ɗaki tace " wlh nama huta ku gama inci dan nayi kwaliya bazani kitchen ba , ta janyo wayarta ƙirar y2 tafara game , albasa nayin ja aka watsa jajjage , aka kife turmin , Ummi ce tace "ina maggi in ɓare , yawwa Ummi na kinason aiki

Aisha ta faɗa tanata juya jajjagen , sai da jajjagen ya fara soyuwa sannan ta ɗibo ruwa ƙaramar robar fenti biyu ta zuba takuma ƙarawa , fitoda farin maggi da dunƙule tayi aka sa farin magi biyar dunƙule aka raba gida biyu tasa rabi , gishiri kuwa ba'a magana , Aisha ta kakaɓe hannu tace " tashi mu koma ɗaki kafin ruwan ya tafasa, miƙewa sukayi suka koma ɗaki bini bini Aisha ta fito duba abinci a fitowa ta uku ne ta samu ruwan na tafasa , auno shimkafa mudu uku tayi bata wanke ba ta zuba , buɗe baki Ummi tayi tace " Aisha baki wanke ba fa , ke dallah ƴar gwamnati ba'a wanketa kuma tafi garɗi , haka ta dinga cakuɗawa tana juyawa daga ƙarshe ta ɗaga kanta sama , ganin kori da onga dakuma time yasata tsalle tace " Ummi ban mu kashe yau duk wanda yaci abincin mu wlh sai ya ruga da gudu tsabar daɗi ,ɗibo su tayi ta buɗe ko wanne sai da tasa cikin cokali uku na cin abinci , onga kuma tasa babba guda ɗaya , ta juya ta kawo murfin tukunyar ta rufe suka nemi guri a bakin kitchen ɗin suka zauna , lokacin ana kiran sallahar magriba , Aisha ce tace " Ummi tashi kije kiyi sallah kina dawowa sai inyi , taɓɓ wlh bazani ba kedai ki fara zuwa ai naga manya ma ƙinyin sallah sukeyi muma yau mu haƙura , cewar Ummi , ƙundun uba to yaya na zuwa kashinmu ya bushe tun wuri kitashi ƙilama kafin ki idar girkin ya tsotse , miƙewa Ummi tayi badan taso ba tana tafiya tana mita haka dai tayo alwalar ta fito taje tayo sallaha , tana fitowa ta samu Aisha ma tayi alwalar binta ɗaki Ummi tayi tace " Aisha mu kira anty Fiddausi ta gane mana girki , kul yasin karki kuskura inmun gama ma bata mun fita har ga Allah amma yanzu wani abu nakeso kuma banida ko sisi , inada ɗari ɗazu baba ya bani wai inhau mashin kuma yaya Zakari ne ya biya , yawwa barin idar da sallah kiji wata magana, Aisha na idarwa tace " kawo kuɗin nan bata kuɗin Ummi tayi suka fice , kai tsaye chemist suka nufa mai za'a baku , Aisha ce tace " mamana ce tace " ka bata mganin sa gudawa rabonta da kashi yau sati kenan , waro ido mai siyarda magani yayi yace " aiko rashin kashi babbar matsala ne ga wanan kice tasha ɗaya yanada ƙarfi sosai, Aisha ce tace " nawa ne kuɗin ? hamsin mai maganin yace " Aisha ta miƙa masa tare da riƙo hanun Ummi suka dawo gida , suna shigowa suka samu abinci ya fara ƙauri da gudu Aisha ta nufi kitchen ganin anty Fiddausi bata fito ba har yanzu gashi ana kiran sallahar isha'i, sauke abincin sukayi ita da Ummi Aisha tace " indomie zan dafawa anty nasan yaya shi zai ci shinkafa , cikin mintuna ƙalilan aka gama dafa indomie wace tasha jagwal gwalo aka juyeta a plet , aka haɗa fresh na apple kasancewar Aisha taga anty Fiddausi na so , juyewa tayi a jug tare da daddaka maganin kashi guda uku tasa , sbda ta ɗanɗana bashi da ɗaci sai ma ɗan tsami tsami, cokali ta samu ta gauraya kana ta ɗauki na plet ɗin da jug ta nufi ɗakin anty Fiddausi , sallama tayi daga can ɓangaren anty Fiddausi tace " waye ? nice anty abinci na kawo miki , da sauri Fiddausi ta miƙe ta buɗe ƙofa dama yunwa ta keji kuma batason shiga kitchen , yawwa nagode ƴan albarka , harda lemo ne ? nasani badan zuwan Ummi ba bazaki tayani aiki ba , dariya Aisha tasa anty Fidausi na karɓa ta wuce kitchen , samu tayi Ummi ta ɗauko wata rantsatsiyar kula ta zuba abinci a cikinta , zaro ido Aisha tayi kana tace " kinaso aci uban mu ko......!

*kuyi haƙuri na rashin ganin post pls kuna raina koda yaushe masu comments and shar'hi ina godiya kuke ƙaramin ƙwarin gwuiwa ana tare iya wuya*

*MOM ISLAM*
[14/07, 7:58 am] Mom Islam Ce: *YARINYA MAI TAƁARGAZA*

*Zainab Habib [Mom Islam]*

*Wattpad @momislam2020*

*AREWA WRITER'S  ASSOCIATION*

*31_32*

Ke dallah babu mai cin uban mu cewar Aisha cika kular tayi fam da abinci ta nufi ɗakin anty Fiddausi , anty Fiddausi na ganinta tace " kan uba wlh yau zakuci ƙaniyarku sabuwar kular tawa ? caɓ ana haka yaya Zakari ya shigo , ganin Ummi zaune a kichen ya leƙa kasancewar an kawo wutar nepa  me kikeyi anan cewar yaya Zkari  , cikin tsoro Ummi tace " yanzu muka gama abinci ina jiran Aisha ne , kamar ance leƙa kitchen yana leƙawa yaga ƙatuwar tukunyar da aka ɗora ga kitchen ɗin kamar anyi wasan ƙasa yayi biji biji, bai yi magana ba ya shige ɗakin anty Fiddausi , samu yayi tana yiwa Aisha faɗa , neman guri yayi ya zauna kana yace " ai ga aika aika can tashi kije ki gani maganin mai lalaci kenan , ƙin tashi tayi ta cigaba da cin indomie n ta Aisha na tsaye tana zaro ido , ɗaukar lemun tayi ta cika ƙaramin cup ta shanye takuma tsiyayo wani zata sha yaya Zakari yace " ina nawa karfa ki shanye , ga shinan anty Fiddausi ta miƙo masa jug ɗin , har Aisha zatayi magana ta fasa gudun kar ta jawa kanta duka , ficewa tayi tunda babu wanda ya kulata , kitchen ta koma ta sami Ummi ta cika roba da abinci tana ta kai loma tana shirin amai , wlh wanan abincin duk wanda ya cishi inhar cikin babu kyau to sai yayi gudawa , cewar Ummi , zuciya ce ta ɗebi Aisha tace " ai nagama yi miki komai tunda na dafa kikazo kina zagina , ta murguɗawa Ummi baki , miƙewa Ummi tayi tace " nidai na ƙoshi ga kwano ki zuba , wata uwar harara Aisha ta zabga mata tare da cewa " gobe zance yaya ya kaiki gidanku , har ƙasa Ummi ta sunkuya tana bawa Aisha haƙuri to na haƙura amma ki dubomin ƙai ƙayin nan ki ajiye mana shi a kusa , to Ummi tace " jiki na rawa a dole batason komawa gida ,
zuba abincin Aisha tayi tana masifa ita wlh bazata zama baiwarsu ba garama su nemi yar aiki.
9:pm Aisha da Ummi sunyi bacci tun takwas hira yaya Zakari suke shida anty Fiddausi da gudu anty Fiddausi ta miƙe tana cewa ka biyoni da ruwan ploshin me zakiyi , bata gama bashi amsa ba ta saki tusa mai wari , toshe hanci yaya Zakari yayi yana mata masifa , kasancewar toilet ɗin a kusa da ɗakinsu take yasa shi jin ƙarar kashin nata ji kake ɓirrrrrr cikin yaya Zakari ne ya murɗa shima ya fito da gudu yana salati , tunowa Fiddausi na bayi yasa shi cewa " wlh inhar baki fito ba inna shigo janyoki zanyi , ba shiri ta fito badan ta gama ba , yana shiga ya saki gudawa shima saki nasa ɓirrrr kafin ya nunfasa Fiddausi ta ƙwalara ƙara tare da cewa " kayimin rai ka ka fito dan girman Allah , yaya Zakari da ya keta wuli wuli da ido yace "ke kibari in gama bazan fito ba kema ai kin daɗe, kafin ta yi wani yunƙuri bata zata ba taji saukar abu kamar fitsari a jikinta , tana duba wa taga ashe gudawa ne , zaro ido tayi tana cewa " hankalinka ya kwanta nayi a wando inba so kake in mutu ba to ka fito kamar ka shiga ɗakin bacci , ko kulata bai yi ba shikam cikinsa ma murɗawa yake gakuma wani sabon kashin , yana gamawa ya kora kashin ya fito, a guje ta shige tana ihu kamar ba dare ba , ta ɗau mintuna kana ta tsarkake jikinta ta fito ta nemi kayan sawa , tana shiga bedroom ɗinta ta sami yaya Zakari yayi ruf da ciki yana zauke nunfashi , ƙara sowa tayi tama kasa zama tsaɓar zafin da ta keji tace " my Zak cikin dauriya yana nishi yaya Zakari yace " kirani da ZAKARI NA kawai yau ba love ka tashi ka ɗoramin koda wani abun ne insa a baki na wlh yunwa nakeji ,

tsaki yayi kana yace " ke gara ke ma yunwa kike ji nikuwa ɗuwawuna ya ɗaɗe ko juyowa banajin zan iya...!

Abban Islam babu lafiya shiyasa kuka jini shiru 😢.

*MOM ISLAM*
[14/07, 7:59 am] Mom Islam Ce: *YARINYA MAI TAƁARGAZA*

*Zainab Habib [Mom Islam]*

*Wattpad @momislam2020*

*AREWA WRITER'S  ASSOCIATION*

*Page 33*

Kukan shagwaɓa tahau yi masa tana riƙe da cikinta dake murɗa mata , tun suna tafiya bayi da ƙarfinsu daga ƙareshe dai anty Fiddausi dafa bango ta koma yi shi kuma yayan babu ƙarfi a jikinsa ko kaɗan , yana tafiya yana layi ya nufi ɗakin su Aisha bubuga ƙofa yayi cikin sa'a yaji alamun ana buɗewa , Aisha ce tana mutsike ido tace " anty Fiddausin ta aihu ne ? zaro ido yaya Zakari yayi kana yace " uban aihuwa tayi fito ki dafa mana shayi , kallon agogo Aisha tayi tace " ƙarfe uku fa sahur zakuyi ? mari ya wanketa da shi yace " azumin muka ɗauka yayi gaba , fitowa tayi tana mita ta nufi kitchen kunna risho tayi ta nemi tukunya lamba biyu ta cikata da ruwa ta ɗibo lifton guda shida tasa ta rufe tukunyar , ta dawo ɗakinsu , shiru babu Aisha babu dalilin ta gashi yunwa ta adda be su , yaya Zakari mai ɗan dauriyar ya fito ya samu tukunya nata tafasa kamar zai faɗa kan  tukunyar ya sauke cike da mamaki yake kallon uban ruwan da aka zuba gakuma lifton da yawa ba shida lokacin ƙirga ko nawa ne hakan yasa shi tsiyayo musu a baban jug ya nufi ɗakin anty Fiddausi , tana ganinsa ta miƙe jiki na rawa tace " har Aishan ta gama ? eh kawai yace " madara ya zuba da milo ya ɗauko bredi ya miƙo mata sai da sukaji cikinsu ya cika sannan kowa ya kwanta , anty Fiddausi ta kai hannu tana shafo sajen yaya Zakari cikin jin haushi yace " kifa ƙyaleni niba mota bane wanan uban kashin da mukayi kina tunanin zamu taɓuka abin arziki yasin bazan iya ba , anty Fiddausi ce tace " haba sweet daga taɓa gemun sweet ko yau babu sweet , rungumeshi tayi bacci yai gaba dasu, da asbha Aisha da Ummi sun tashi da gudu Aisha ta nufi kitchen tana salati , nabar shayi akan wuta ko waye ya sauke oho , Ummi da take shirin shiga toilet ɗin waje tace " waye mai shan shayi kuma , oho Aisha tace " can kuma tace " suwaye masu gidan ? kulata Ummi tayi ta shige , bayan sunyi sallah har ƙarfe takwas ba suji motsin su anty Fiddausi a , Aisha ce ta dubi Ummi tace " walh yunwa na keji kamar zan mutu , Ummi dake rakuɓe gefen katifa itama da alamun yunwar ta keji tace " naga ɗakin nasu a buɗe , ki ɗumama ruwan lifton ɗinnan ni kuma zani in kamfato madara dan yau sai munsha mai kauri , to Aisha tace " ɗorawa tayi tana jiran yai zafi , can anjima taji yana ƙarar tafasa saukewa tayi tare da

juyewa a roba tace " Ummi nagama barin kai ɗaki ,saɗaf saɗaf Ummi ta shige ɗakin anty Fiddausi ganin madarar a palo yasa ta ɗaukar robar dakuma haɗawa da milo guda huɗu , ta fito , kai tsaye ɗakinsu ta nufa ta sami Aisha na zubawa a cup ɗin da zasu sha , zuzuba madarar sukayi suka ajiye a gefe , Aisha ce tace" Ummi ina suga , ke ban gani ba kalan su kamani karma azo sun mutu ne nafara jin tsoro wlh ace basu tashi ba har yanzu kodai zamu leƙa ne ? harara Aisha ta gallawa Ummi tace" wa zamu leƙa babu inda zani wlh jeki ɗauko suga da biredi , to Ummi tace " tare da ɗibar  robar madara ta koma da shi , jin alamun ana magana yasa Ummi ɗauko biredi ta rugo da gudu takuma mancewa da suga , tana shigowa ta faɗa kan Aisha tace " wlh sun tashi , Aisha dake miƙo hannu ta karɓi suga taga sai biredi , cewa "tayi dan kutumar ubanki ina sugan ?ban ganshi ba cewar Ummi , a zuciye Aisha ta miƙe ta nufi ɗakin cike da masifa , tana zuwa ta janyo robar sugan tana shirin fitowa taga yaya Zakari na rarrafe , cikin mamaki ta tsaya kallonsa tace " ikon Allah yaya ya koma jinjiri ta tuntsire da dariya, cikin dauriya yaya Zakari yace " Aisha larura cefa ba yin kaina bane , yaya meya sameka ?cewar Aisha ,gudawa ce ta samemu nida antynki kodai abincin da kukayi jiya ne ya lalata mana ciki , anty Fiddausi dake tafiya kamar Mai ciki tana riƙe da bango tana nishi tace " shine ma wlh shine , riƙe baki Aisha tayi tace " yaya ka mance nice nakeyin abinci a gida , cikin dauriya yace " tabbas to ni na rasa mene ne ya lalata mana ciki , anty Fiddausi ce ta sami guri a kan 3siter ta kwanta ta rame kamar wacce tayi sati tana ciwo dama ba mai ƙiba bace , Aisha ɗibo min ruwa anty Fiddausi ta faɗa da muryarta da take fita da ƙyar , Hu'um Aisha tace " kalan in ɗibo muku ya saku gudawa kujira dai ku ɗora girki ni shayi zani insha , waro ido anty Fiddausi tayi da mamaki tace " ni kike gayawa haka , maza ki dafa min ƙwai guda biyu kokuma jikinki ya gaya miki , yaya Zakari dake ƙoƙarin tashi ya ce " Aisha bana son raini fa , ɗaukar robar suga tayi ta fice dan tasan tunda ta gansu a sharɓe kamar kayan wanki ba komai zasu iya ba , dawowa tayi ta kunna tv tasa musu ƙiɗa cikin ƙanƙanin lokaci gidan ya kaure da waƙa ga spiku da keta tashin kiɗa , rawa ta fara tana juyi daga ƙarshe ta fice , daga yaya Zakari har Fiddausi babu mai magana gasu a zube babu mai iya taɓuka komai.....!

*MOM ISLAM*
[14/07, 7:59 am] Mom Islam Ce: *YARINYA MAI TAƁARGAZA*

*Zainab Habib [Mom Islam]*

*Wattpad @momislam2020*

*AREWA WRITER'S  ASSOCIATION*

*Page 34*

Mamakin hali irinna Aisha anty Fiddausi keyi , shikam yayan da ya gaji da kwanciya ya miƙe ya dafa bango ya nufi ɗakin su Aisha , zaune ya sa mesu suna ta shan tea , suna ganinsa suka gai shesa bayan ya amsa yace " Ummi kuzo ku kira mana likita a chemist ɗin ƙofar gidanan , to suka ce kana suka miƙe dan zuwa kiran , hijab suka

ɗauka suka fito , tun a hanya Aisha ta fara tunani inhar wanda ya bata maganin kashi ne to bazata bari yazo gidan ba dan asirinsu zai tonu , Ummi da kejin surutan Aisha itama tsoro ne ya kamata dan tafi Aisha tsoro , suna zuwa bakin chemist ɗin suka tsaya ganin wani yaro yazo wucewa yasa Aisha tarar shi tace " dan Allah akwai wani shagon siyarda magani bayan wanan ? eh yaron yace " ga shican na gefe mai farin fenti , tafiya sukaci gaba da yi suna surutunsu , suna isowa suka samu akwai mutum ɗaya duban Aisha Ummi tayi tace" maganin kashin zamu kuma siyowa , Aisha da kamar jira take tace " kice dai mu kashesu mu huta kawai inba haka ba kina ganin ko tafiya basa iya yi , cikin tsananin tsoro Ummi tace " idan asirinmu ya tonu fa , tsalle Aisha tayi ta cukumo wuyan hijab ɗin Ummi tace " da naci uwarki babu mai tonawa sai ke shi yasa na dena shiri dake , haƙuri Ummi ta shiga bawa Aisha daganan suka shirya mai chemist ya leƙo yana ganin kamar suna shirin faɗa yace " in faɗa zakuyi ku tashi a nan kuyi gaba , gurinka aka aiko mu Aisha tace " tana murguɗa masa baki , togani cewar mai chemist "wai kazo ka ƙarawa yayana da anty na ruwa sun kwana suna gudawa ko tafiya basayi nice nayi musu girki ma sunanan a palo kamar an zuba shanya , tunda tafara magana yake kallon bakin tsiwarta , wane gida ne ? mai chemist ya tambaye ta nuni tayi masa da hannu , yace " gani nan , komawa gida sukayi ita da Ummi suka nufi ɗakin anty Fiddausi , har yanzu suna zaune babu wanda ya tashi daga inda yake ga kuma kiɗa na tashi , kashe waƙar Aisha tayi ta dubi yaya Zakari dake binta da ido tace " gashinan zuwa , to yayan yace " suka fice ita da Ummi , Aisha ce ta hau buga ciki tana kiran yunwa , to muje mu ɗumama shinkafar nan mana , Aisha dake nufar hanyar kitchen tace " wlh ƙwai zamu soya yau ɗinnan sai dai suji ƙamshi , ɗibo ƙwai tayi guda bakwai da magi da mangyaɗa , ta ɗauko abin suya tana gama suyar ta juye musu a plet Ummi tace " barmin mangyaɗan zan soya dankali , to yi sauri ki fere cewar Aisha , Ummi na ferewa Aisha na suya haka gidan ya kaure da ƙamshi har waje , ƙwala mata kira yaya Zakari yayi tana jinsa tayi shiru a hankali suka kashe risho suka koma ɗaki , ana zuwa aka hau rabo suna ci suna shirin muguntar da zasu yiwa su yaya da zarar sun warke, sallamar da sukaji ne yasa Aisha dake bakin ƙofa ta leƙo dan taga ko waye , tana ganin sa tace "ka shiga suna ciki , haka ya wuce ya samesu a kwance yaya Zakari a ƙasa Fiddausi a kan kujera, bayan sun gaisa yayi musu yan tambayoyi ya ciro kayan aikinsa ya fara sanya musu ruwa na tafiya da gudu , yana zaune yana jiran ƙarewarsa yasa musu wani , wanan da yasa ne yake tafiya a hankali , ficewa yayi yace " yanzu zai dawo , Aisha na gama ci ita da Ummi suka tara kwanukan a kitchen harda najiya basu wanke ba , dawowa ɗaki sukayi suna shawarar inda zasu je yawo....!

*MOM ISLAM*
[14/07, 8:00 am] Mom Islam Ce: *YARINYA MAI TAƁARGAZA*

*Zainab Habib [Mom Islam]*

*Wattpad @momislam2020*

*AREWA WRITER'S ASSOCIATION*

*Page 35*

Doctor na shigowa ya samu drip ɗin da ya sa musu ya ƙare gashi kuma jikinsu ya ɗanyi ƙwari hamdalah yayi ya basu magani , yaya Zakari ya tambaye sa kuɗin da zai bashi , ka bada 5k ok yaya Zakari yace " kana ya miƙe ya nufi cikin ɗakin su ya ɗauko kuɗin ya dawo ya miƙa masa , godiya sukayi mai kana ya fice bayan ya gaya musu dokokin shan magani , zuwa azhar duk sun sami lafiya anty Fiddausi ce ta fara fitowa sai ga yaya shima ya fito yayi wanka ya sauya kaya , direct ɗakin su Aisha suka nufa inda suka sa mesu suna ɓare dafaffen ƙwai , anty Fiddausi ce ta shige har cikin ɗakin tahau dukansu babu abin da yayan yace " mata yasan sunyi aika aika a gidan ficewa yayi ya barta da su tana tafama , hango wayar wuta tayi ta ɗauko sai da tayiwa kowa huɗu sanan ta fita a ɗakin , kitchen ta wuce dan ɗora girki ga mamakinta sai taga kitchen ɗin kamar tsohuwar bola yayi kaca kaca da kaya , ga baƙin tukunya , wlh sai na ƙara muku dukan shegun yara irin bala'i , ta kuma koawa ɗakin tana masifa , tana shiga ta sa mesu sun haɗa kai suna ta ihu , zaginsu ta shiga yi tana turr da halinsu , da ta gaji tayi waje , dama ga jikin babu ƙarfi sosai ta koma ɗaki ta dinga haki tana mai da nunfashi .
Washe gari tun asbha ta je ta taso su suna magagin bacci haka suka fito mari ta bawa ko waccen su babu shiri suka wartsake, maza ku shiga kitchen ku share ku goge wlh inba haka ba sai ranku ya ɓaci in a gidan iyayenku ne zakuyi haka ? kokuma haushin rashi iyayenku suka turoku ku ɓatamin kaya , kansu a sunkuye suka shiga kitchen suka hau aiki , kafin gari yai haske har sun kammalah komai , leƙowa tayi taga komai ya gyaru ta tsaya riƙe da kwankwaso tace " ke Aisha kunna risho ki ɗora mana ruwan shayi ke kuma Ummi haɗa kayan wanke wanke kiyi , Ummi na turo baki ta haɗa ta kai gurin wakewa ta ɗibi ruwa a pampo ta ɗauko omo ta fara wankewa , tana gamawa tayi alwalah tayi sallah Aisha ma haka , yaya Zakari na shigowa ya same su zaune sunyi jugum jugum yana jiran gaisuwa amma babu wacce ta kula shi , ƙarasowa yayi yace " yan mata lafiya kuwa ? Ummi dake shirin kuka tace " anty Fiddausi ce tace " wai iyayenka jahilai ne da zasu kawo mata mu bamusan ciwon kaya ba , a zuciye ya fice ya nufi ɗakin anty Fiddausi samunta yayi taci kwaliya tana zaune da waya a hannunta , yana zuwa ya wanketa da mari kana yace " nagode da zagin iyayena da kikayi naji komai kuma kin kyauta , na shiga uku nice na zagi iyayenka me suka yimin da zan zagesu?" cewar anty Fiddausi,kuka ta saki mai ban tausayi tama mance ta yiwa su Ummi faɗa badan haka ba da tace sune da wanan sharrin amma ko waye Allah zai saka mata , kayi haƙuri dan Allah nidai nasan ban faɗa ba , yaya Zakari ne yace " ai abin ne ya ƙona min rai amma ya wuce .su Aisha najin faɗan su anty Fiddausi sai dariya suke suna tsalle.
Yau watan anty Fiddausi biyu a gidan yaya Zakari tayi ƙiba tayi kyau shirin zuwa gidansu takeyi tun safe misalin 12:pm ta fito da hand bag tana sanye da material baƙi mai adon flawoyi yellow kai tsaye ɗakin su Ummi tayi ta sa mesu zaune kowace hanunta da plet ɗin soyayyen dankali , zaro ido anty Fiddausi tayi tace " wlh rainin wayon yayi haka ko ni da nake gidan banacin abinda kuke ci baga shinkafa can ba ? barinje anguwa in dawo wlh sai kunbar gidannan nanda kwana uku haka kawai .su dai ko kallonta basuyi ba bare tasa ran zasu amsa mata , saura inga ɓarna wlh sai nayi muku duka ta fice fuu kamar zata tashi sama , tana fita ta hango yaya Zakari na tahowa tsayawa tayi har sai da ya ƙaraso yana zuwa ya tambayeta harta fito ne ? eh tace " yanzu zan tafi , to muje in nema miki abin hawa , bakin titi suka nufa bai dawo ba har sai da yaga tafiyarta , fasa komawa gidan yayi ya nufi gareji dan ɗazu an kirashi gyara .
Aisha ce ta ɗauko abin ƙai ƙayin nan tace " wa Ummi zo muje wlh daga ita har yaya yau sai sun ɗana tunda ko ana dukanmu baya magana , ɗakin anty Fiddausi suka nufa kasancewar bata kulle ba iya turo ƙofa da tayi , direct cikin ɗakin suka nufa Ummi miƙo min tsintsiya cewar Aisha, to Ummi tace " ta dawo palo ta ɗauko wa Aisha tsintsiya ta miƙo mata , ywwa Aisha tace " zasu raina kansu wlh ta buɗe baƙar ledar ta dinga bi ta kan gado tana hura wa tana sharowa da tsintsiya , har kan fillo

ta shafa , suka fito tare da mayar da ƙofar suka rufe ,ɗaukar tsintsiya Ummi tayi tace " barin yi shara kekuma ki gyara mana ɗakinmu , haka suka dinga aiki har kusan magriba , kasancewar kafin anty Fiddausin ta tafi tayi musu girki tasa a flaks.
mamanta na ganinta ta hau washe haƙora tana cewa maraba da amarya abinci aka yi mata mai rai da lafiya suka shiga hira anty Fiddausi tabawa mamanta labarin yaran dake gidanta da kuma mugun cin da sukeyi , jin jina lamarin maman tayi kana tace "ai wanan ba wata matsala bace kawai ki miƙe ƙafa ki huta lokacin hutunki ne yazo wankin ki ki basu inkuma kaiwa kukeyi ki basu wanke wanke da shara har gyaran gado girki kam kiyi kayanki karki kuskura ki dinga wahalar da jikinki naga kamar ma ciki ne dake ko ? zaro ido Anty Fiddausi tayi tace " ba nida komai mama , ƙarya ne muga tafin hanunki cewar mama , miƙa mata anty Fiddausi tayi murmishi mama tasa kana tace " alhmdulilh kinada ciki ga ƙwayar idanunki nan ta nuna , nikam banason ɗaukar ciki yanzu Fiddausi ta faɗa a shagwaɓe , kallon banza mama tayi mata kana tace " bakida hankali bakisan cikin shine hanya mafi sauƙi da zaki dinga tatsarsa ba , kina temaka mana ? ga babanki babu aikin yi sai dai fa in yayanki yayi aiki a mashin shine muke samu, to tun wuri ki farka daga mumunan mafarkin da kikeyi , to mama anty Fiddausi ta faɗa badan taso ba , zuwa ƙarfe biyar anty Fiddausi ta fara shirin tafiya gida , magunguna mamanta ta haɗa mata na mata , tace " tunda tanada ciki tayi amfani da kaɗan , godiya Anty Fiddausi tayi ta fito domin tafiya gida , mai mashin ta tara tayi masa kwatancen inda zai kaita bayan ta hau suka nufi anguwarsu , tana sauka ta bada kuɗin mashin , da sallama ta shiga gidan jin gidan shiru yasa ta leƙa ɗakin su Aisha babu kowa a ciki hakan yasa ta nufi ɗakinta , cire kayan jikinta tayi ta ɗauko farar vest mai siririn hannu da dogon wando yaɗan kama jikinta, ta sanya ko ɗankwali babu ta fito ta nufi kitchen ta ɗauko cup ta dawo ɗaki , maganin da mama ta bata shi ta ɗauko na sha da madara , sai da ta cika cokali biyu sanan ta zuba ta nemi madara ta zuba mai yawa ta kafa kai ta shanye tana faɗin yau my sweet zai sha daɗi .
Ana kiran isha'i taji sallamar su Aisha lokacin tana sallah , tana idarwa ta fito tana ce musu daga ina kuke ? yawo mukaje cewar Aisha , kan uba ni kike gayawa haka to wlh bazan ɗauki rani ba Ummi dake rakuɓe jikin bango tace " anty kiyi haƙuri bamu taɓa fita bane shine muka fita , maza kuyi alwalah kuyi sallah kuzo ku ɗumama shinkafar kular can dan na taɓa naji babu zafi , in tayi ɗumi ku zubo min nida yayanku , to suka ce Ummi ta nufi kitchen jiki na rawa , kasancewar a gida bata girki yasa sai da ta tambayi Aisha inda zatayi sanan aka kunna risho aka juye abincin a tukunya aka zuba ruwa suka rufe tare da fitowa daga kitchen ɗin.
bayan sunyi sallah suka jiyo ƙaurin abinci da gudu Ummi ta fito ta sauke suka kashe rishon , fara zubawa su anty Fiddausi tayi kana ta zuba nasu ta kai musu ɗaki , Aisha ko fitowa batayi ba , anty Fiddausi na ganin Ummi tace " ywwa sannu ina marar kunyar tayi , wacece marar kunya ? cewar Ummi , Aisha man , wlh sai na gaya mata , zaro ido anty Fiddausi tayi tace " uban me zata yimin kin daɗe baki faɗa ba , abincin dake hanunta ta saki a ƙasa ya zube , dan uwarki abincin namu kika zubar ?kallonta Ummi keyi ba tare da ta amsa mata ba anty Fiddausi tayi faɗan tayi amma shiru Ummi batace komai ba , anty Fiddausi ce tace " ina magana kina jina ? harara Ummi ta zabgawa anty Fiddausi kana ta ruga da gudu ta shigo ɗakinsu, tana shiga ta faɗa kan Aisha dake zuba loma tace " wlh Aisha antynan tama sameki ne , Aisha ce tace "maiya faru ? wai kece matsiya ciya tsalle Aisha ta doka kafin Ummi takai ga ƙarasa magana Aisha ta fice , ɗakin Anty Fiddausi ta nufa ta ɗaga wayarta ta kwaɗa da ƙasa ta fito tana huci , anty Fiddausi lamarin ya fara bata tsoro sbda gani take duk sun canza kasa magana tayi sai ma kuka da ta fashe dshi, komawa ɗaki Aisha tayi taci gaba da cin abincin ta hankali kwance , Ummi ce ta dubeta tace " amma antyn nan tama samemu wlh dan taga muna ƙyaleta ko da jar fuska kamar zabiya , sai ma anjima cewar Aisha zamuga rawar disko suka sa dariya .
Anty Fiddausi taci kukanta ta gama ta janyo wayarta ta haɗa Allah yasa bata fashe ba ta kunna cikin sa'a ta kawo , murmishi tayi dan tana tunanin inhar ta rasa wanan wayar to sai ta Allah.

Idan su Aisha biyu har ƙarfe goma na dare amma sun rufe ƙofa , suna jin shigowar yaya Zakari suka fara kasa kunne domin jin abinda zai wakana .
Da sallama ya shiga ɗakin anty Fiddausi tarar shi tayi da gudu ta rungumeshi suka zauna , bayan ya huta yaci abinci tace " to ya aikin ? lafiya lou yace mata amma inason yin wanka , miƙewa tayi ta haɗa masa ruwan wanka ta dawo ta riƙo hanunsa tare da cire masa kaya suka nufi toilet,  wanka tayi masa suka fito cike da soyayya ta tayashi shafa mai , bayan ya kammala shiri ya dawo gurin anty Fiddausi da ta kame a palo tana jiransa , my Fiddy rigima ta tashi ko ? kashe masa ido tayi tare da cewa " kasan me ?girgiza kai yayi alamar a'a tace " nayi maka tanadin wani abu da sauri ya taho dan ya gane ko meye ya rungumeta ya hau shafa kanta yana kai mata hot kiss ta ko ina , cikin sauri ta hau maida masa daga nan labari ya fara sauyawa , cikin sauri ta hau cire komai na jikinta ta haye kan yaya ,cak ya ɗauketa kamar baby ya direta kan gado , a zabure ta sauko tare da kurma uban ihu yana shirin hawa ya fasa dan ya rasa me ya tsorata ta, my Fiddy lafiya ? yaya zakari ya tambayeta cikin sweet voice , bata sami damar bashi amsa ba sai ma soshe soshe da takeyi gashi jikin babu kaya , yaya zakari idanunsa sun rufe yama mance ga abinda ta keji ya taho kamar mahaukacin zaki yana shirin wurgata gado ta zaburo , palo ya dawo da ita yai mata rumfa tana cewa " bazaka tausaya min ba ?" ƙai ƙayi ya dameni da fara kuka , ina shikam bai san tanayi ba gashi kamar ana ƙaro ƙaiƙayi ga uban ihu da take zundumawa amma duk bai saurara mata ba , sai da ya daɗe yana kwasar gara sanan ya ɗagata , ganin hawaye a fuskarta ya tuno abinda ya faru ,to meye a gadon ?" ko saurarar sa batayi ba ta mirgina tana cigaba da sosa bayanta tana kuka.
tun daga ɗakin su Aisha ke jiyo ihun anty Fiddausi rawa suka dinga yi tsabar murna , Ummi ce tayi suɓutar baki tace " saura yaya ma , gallah mata harara Aisha tayi tace " insha Allah yaya baze kwasa ba wlhi sai dai ita , daga haka bacci ya kwashesu .
Bayan yayi wanka ya dawo ya ɗauketa yai mata wankan a mai makon ƙai ƙayin ya tafi sai gantsarewa take tana tsalle , ganin abin nata yana neman ya zamo wasa yasa shi yi mata dariya , cikin muryar kuka anty Fiddausi tace " dariya kake yimin ko ? bakasan inda nake ji bane da sai ka tausaya min , taci gaba da susa , am sorry my Fiddy tashi muje mu kwnta , wlh bazani ba gadonne mai ƙai ƙayi , yaya Zakari da taso sashi dariya yace " ya za'ayi gado yayi ƙaiƙayi dan Allah kizo mu kwnta ,ƙin zuwa anty Fiddausi tayi ta nemi guri a palo ta kwanta ,shikam shiga cikin ɗakin yayi ya nemi gajeren wando yasa yai bismillah.......!

*Masoya naga ruwan sharhi shiyasa nayi muku da ɗan yawa *

*MOM ISLAM*
[14/07, 8:00 am] Mom Islam Ce: *YARINYA MAI TAƁARGAZA*

https://www.youtube.com/channel/UCcAjVQ74qod9_dL0e_AqkiQ

*DUNIYAR LITTAFAN HAUSA TV*

*Zainab Habib [Mom Islam]*

*Wattpad @momislam2020*

Ya haye gadon farko yaɗan ji ƙai ƙayi ya nuna kamar bai damu ba sai da ya kuma juyawa yaji kamar ana ƙarawa a zabure ya sauko daga gadon yai palo da gudu har anty Fiddausi ta fara bacci taji gudu ta farka , kai ma kaji ko ? tambayar da tayi masa kenan yaya Zakari babu bakin magana sai rawar susa yake yana juyi abin dariya , yaba anty Fiddausi tadinga dara wa , da ya gaji da susa ya nufi toilet ya ɗibi ruwa yana kwarawa jikinsa , da gudu ya fito babu wando yana kiran wayo Allah na zan mutu wanan ƙai ƙayi kamar cutar ajali?" tun tsirewa da dariya anty Fiddausi ta sake yi tana cewa "alhaki na ne ka jira kawai sai lokacin da Allah ya yaye maka , sai da ya gama rawa sanan zuwa wani lokaci yaji sauƙin ƙai ƙayin , toilet ya wuce ya sake wanka ya sauya kaya ya dawo palo ya kwanta a ƙasa kan kafet , daganan bacci mai nauyi ya kwashesa ,  washe gari an tashi da sanyi har ƙarfe bakwai babu wanda ya leƙo waje daga su anty Fiddausi har su Aisha , tunda sukayi sallah suka koma bacci basu suka tashi ba sai misalin ƙarfe taƙwas na safe , yunwa ce ta tada Aisha Ummi najin tashin Aisha ta miƙe tana rarraba ido , tashi mu shiga kitchen tunda basu tashi ba , cewar Aisha Ummi ce tace " jeki ni zan gyara ɗaki , tashi Aisha tayi ta nufi hanyar kitchen jin ƙarar ana buga cokali ga ƙanshin ƙwai yasa Aisha dawowa da baya da baya , jin ta bugi mutum yasa ta ware ido ta juyo , saukar mari taji tare da cewa " yaya kayi haƙuri ban san kai ne ba , harara ya galla mata yace " to me kikazo yi amshewa tayi da nazo taya anty aiki ne shine tace " min wai kwaɗayi nazo yi , ita Fiddausin ta gaya miki haka ?" jiyo muryar anty Fiddausi sukayi tana cewa " wlh na kamaki babu wanda ya isa ya hanani dukanki tunda sharri ne aikin ki , kuka Aisha tasa tana cewa " wlhi da bakinki kika faɗi haka jin alamum an fito da gudu yasa Aisha rugawa ɗakinsu ta saka saƙata tana maida nunfashi , kiyi haƙuri yaya Zakari yace " tare da ruƙo hanunta , suka nufi kitchen , ganin ta kammala suyar ƙwan yasa shi riƙo ta suka nufi ɗaki , fashewa tayi da kuka tana cewa " wlh bazan yarda ba har ga Allah nayi ƙoƙarin zama da yarannan jiya sukayi min rashin kunya Aisha ta yarmin da waya Ummi ta yimin rashin kunya wlh bazan iya ba ka maidasu gidan ku , tunda ta fara maganar yaya Zakari ke kallon bakinta , yasan riƙon Aisha alƙawari yayi bazai iya mai data ba tun tana jaririya yace " inhar yai aure to zai ɗauketa Ummi kuwa dalilin sa na kawota yaga Aisha na neman guduwa , tsagaita tunanin yayi ya dubeta yace " kiyi haƙuri suma fa zaki dinga morarsu abinda na keso da ke dan Allah kiyi haƙuri komai ya wuce gobe zan saka su a islamiya zuwa gaba kuma inna sami halli zan sasu a boko , to kawai tace " ta buɗe foodflaks ta ɗauko plet ta zuba masa nasa ƙwan da biredi kana ta tsiyaya masa tea a cup , zubawa su Aisha tayi ta sa musu ƙwan da bredin da tea ta ƙwala wa Ummi kira dan sunfi shiri ƙaɗan , Ummi na zuwa ta gai da anty Fiddausi da yaya bayan sun amsa tace " ga naku , ɗauka tayi ta miƙa ɗakin ta ajiyewa shugaba Aisha a gabanta ta janyo nata ta fara sha , bayan sun gama suka fito takwanukan suka fara wanke wanke , shikuma yaya Zakari ya fito zai tafi gareji , bayan sun gama suka koma ɗaki suka fara wasa suna dariya.

Washe gari anty Fiddausi ta tashi babu lafiya banda amai babu abin da take kwarawa kamar zata amayar da hanjin cikinta , yaya zakari ya ƙiɗime ya ɗibo mata ruwa ta wanke baki ya zubar da aman kasancewar a po tayi , tashi muje asibiti yaya zakari yace " wa anty Fiddausi ganin galabaitar da tayi , hijab ya ɗauko mata ya sa mata suka fito leƙa ɗakin su Aisha yayi yace " wlh saura inji ko inga kunyi ɓarna ni da ku ne, ina zaku yaya ?Aisha ta tambaye shi , zamuje asibiti ne Fiddausi babu lafiya , cikin haɗin baki suka ce Allah ya bata lafiya , ficewa sukayi zuwa bakin titi

suka tari mashin ya gaya musu sunan asibitin da zai kai su. suna ganin sun fice dukan su suka fito kai tsaye ɗakin suka nufa samun ragowar ayaba sukayi a faranti sunkai huɗu rabawa sukayi kowa biyu , Aisha ta buɗe madara ta ciko cokali takai baki haka ma Ummi sunsha yakai cokali uku uku , suka share ɗakin suka fito , kitchen Ummi ta nufa Aisha ɗaki ta koma ko me taje yi oho naga ta fito da farar leda tace " ɗibo min ƙwai guda huɗu Ummi , mai zakiyi dashi ? Ummi ta tambayeta , zan kai a soya mana ne a'a , Ummi tace " mu soya a nan inyaso sai mu share kitchen ɗin ko ? eh kuma fa haka ne to kunna wuta , cikin sauri Ummi ta kuna risho suka duba babu maggi haka suka sa gishiri cikin ƙanƙanin lokaci suka gama tare da share kitchen ɗin , ɗaki suka wuce aka fara walimar cin ƙwai , sallamar su anty Fiddausi ce ta sasu tashi da gudu suka ɓoye plet ɗin a cikin jakar Ummi , yaya ne yace " babu kowa ne a gidan anata sallama amma shiru ? muna nan walkslm Aisha tace " kamar marar gaskiya , jikinsa ya basa basuda gaskiya dan gidan ya kaure da ƙamshi sosai , wucewa ɗaki yayi da anty Fiddasuyi ta kwanta kan kujera tare da cewa zanci ayaba , juyawa yayi zai ɗauko a inda suka barshi yaga wayam babu ɓawon ayabar babu ayaba ,mamaki ne ya kamashi yace " ina zuwa , ficewa yayi zuwa inda ake siyarda lemu da kankana da ayaba ya siyo na 1k ya shigo da shi , miƙawa Fiddausi ayabar yayi bayan ya ɓare mata guda uku taci tace ya isheta ta maida kanta ta kwanta , kasancewr magungunan da tasha a asibiti masu sa bacci ne bacci mai nauyi ya kwasheta , shi kuma ganin tayi bacci ya tafi masallaci yin azhar da la'asar , Ummi da Aisha na lura da komai ta window hakan yasa Aisha da bata da tsoro ta fito , ta shiga ɗakin anty Fiddausi saɗaf saɗaf ta ɗauko lemu ɗaya abarba yanka ɗaya tafito da gudu , ɗakinsu ta wuce inda ta sami Ummi na jiranta , wanne kikeso Aisha tace "nuna lemo Ummi tayi dan tasan Aisha bama bata lemon zatayi ba sbda abarba ba damuwarta bane , kan uba wlh bazaki sha ba sai dai ki karɓi abarba , maganar abarba da Aisha tayi karaf a kunnen yaya Zakari da ya shigo yanzu, faɗawa ɗakin nasu yayi babu sallama ya cire belt ɗin wandonsa ya fara jibgarsu bai tsaya yi musu bayani ba sai da yayi musu lilis sanan ya ƙyalesu yana nunasu da yatsa yace " wlh daga yau sai yau inhar kuka sake shiga ɗakin Fiddausi kuka ɗauko mata wani abu wlh zan saɓa muku kunga na dawo ban baku ba ? ina lallaɓa baiwar Allahn amma kuna nema ku ƙureni , wuli wuli suka shiga yi da ido ganin lemu a gefe da yankan abarba yasa shi ɗaukewa yace " tunda kuna nema ku zamo ɓarayi to wlh zan gyara muku zama , zasu sake sakin kukan ya dawo yana shirin ƙara musu tsit sukayi ko tari babu har ya wuce ciki , anty Fiddausi najin shigowarsa tayi masa sannu tare da tambayarsa lafiya taji yana ta faɗa kuwa ? lafiya lau yace " wai yunwa sukeji shine suke kuka , lah su ɗibi indomie su dafa mana man ai ni nama mance , ficewa yaya Zakari yayi yace " wa Aisha ki tashi ki ɗora indomie kiyi sauri , babu musu ta miƙe ta zuba ruwa dan kamar tsumbule take shirin yi tasa mai da magin indomien takuma ɗauko wani maggin tasa ta rufe ta zauna tare da rafka tagumi , can anjima taji ruwan na rafasa sanya indomie tayi ta juya takuma zama tana tunanin mama , gaskiya gara su gudu a gidannan koda nama ake ci sukam sun yafe wlh bazasu iya zaman takura ba a gida babu mai dukansu a nan kuwa abu kaɗan kayi za'a dakeka ta share hawayen da ya gangaro mata ta duba ganin ta tsotse yasa ta saukewa ta nemi kwanonsu ta sa musu ta nemi kula tasawa su yaya taje ta kai musu , ganin anty Fiddausi kwance tayi fillo da ƙafar yaya yasa Aisha cewa "aji tsoron Allah ta fito da gudu , girgixa kai yaya Zakari yayi yana mamakin duka da baya tsirga fatar Aisha , kasa kiranta yayi ya miƙe tare da ɗauko plet da cokali ya sanya musu ya ɗibo ruwa a jug ya ajiye yace "Fiddausi ta tashi ta ci tana sauko wa tayi cokali biyu ta koma ta kwanta , yaya Zakari ne yace " wai ita Aisha yaushe zatayi hankali ne ? uhm kawai Anty Fiddausi tace " tare da sakin kuka , kiɗimewa yaya Zakari yayi yace " mekuma ya faru ? a shagwaɓe anty Fiddausi tace " nidai a cire min wanan cikin wlh bani son shi wuya zai bani meyasa da nayi magana a asibiti kaji haushi na shikuma doctor ya hau yimin nasiha ? taci gaba da kuka.......!

manage

*MOM ISLAM*
[14/07, 8:18 am] Mom Islam Ce: *YARINYA MAI TAƁARGAZA*

https://www.youtube.com/channel/UCcAjVQ74qod9_dL0e_AqkiQ

*DUNIYAR LITTAFAN HAUSA TV*

*Zainab Habib [Mom Islam]*

*Wattpad @momislam2020*

*AREWA WRITER'S ASSOCIATION*

*Page 37*

Wani irin kallo yaya Zakari yai mata mai kamada baki da hankali , tsit tayi da bakinta dan tasan zuwan da dawowar gargaɗi na ƙareshe , yaya Zakari ya nuna ta da yatsa ko da wasa inhar kikasha maganin da zai illata jinina wlh sai kinyi dana sani matuƙa , ya miƙe a zuciye ya fice " bai gama cin abincin ba , kuka taci gaba dayi ganin babu mai rarrashin ta yasa ta yin shiru tana jin tashin zuciya gashi duk jikinta babu ƙarfi , runtse idonta tayi tana tuno rayuwarta na amarci yanzu ko son ganin yaya Zakari a kusa da ita batayi , dafa bango tayi ta nufi gado ta kwanta tana dana sani da tun kafin auransu tayi planing bakin alƙalami ya bushe ta faɗa a fili .
9pm yaya Zakari ne ya shigo da baƙar leda a hanunsa ya nufi ɗakin su , ganin bata palo yasa shi ƙarasawa ciki ya ajiye ya dawo palo ya ɗauko plet ya nufi cikin ɗakin , Fiddy tashi kici ko bakin zai yi miki daɗi , miƙewa tayi tana nufar fashi ta ɗauki ɗaya tasa a baki jin amai da ya taso mata yasa ta miƙewa da gudu ta sauko kafin ta wuce ta kwarowa yaya Zakari amai a jiki , bai damu ba kasancewar yana son abinsa ya miƙe tare da ajiye plet ɗin a gefe ya riƙe mata hannu suka nufi toilet ya sauya kayan jikinsa , bana son ƙamshin naman dan Allah ka fita da shi , Allah sarki bawan Allah ya kiɗime ya ƙwalawa su Aisha kira har sun fara bacci Aisha ta amsa ta fito , miƙa mata ledar naman yayi yace " musu sai da safe , Aisha na shiga tayi tsalle ta faɗa katifa tace " kura tashi yau walimar raga dada zamuyi , zaro ido Ummi tayi tace " wanan uban naman fa , yaya ne ya shigo da shi cewar Aisha , tashi ki raba mana dan wlh ni bazan iya ba amma tunda ni na karɓo nice za'aba mai yawa , hakan akayi koda Ummi ta raba na Aisha yafi yawa suna gama ci suka kwanta babu zancen wanke baki sunma mance da rufo ƙofa .
Washe gari, bayan sunyi karin safe sunyi wanke wnke dan yaya ya gaya musu anty Fiddausi babu lafiya , 10:am yaya ya shigo yace " su shirya za suje gida gaida su mama , murna ba'a magana cikin ɗoki suka shirya harda tura kaya a jaka , yaya na shigowa ya samu sun ajiye jaka a gabansu , ina zakuje da jaka? yaya ya tamayesu , kwana biyu zamuyi cewar Aisha ,murtuke fuska yayi yace " wlh zaku fasa zuwa Fiddausin babu lafiya koba komai ai zaku temaka mata da wani abun ko , badan sun

so ba suka ajiye jakar yayi musu umarni da su fito suna fitowa ko ɗakin anty Fiddausi basu leƙa ba sukayi hanyar waje , ganin mai mashin yasa su hawa yaya yayi masa kwatancen inda za'a saukesu ya basu ɗari huɗu yace " in zasu dawo , ba wata tafiya mai nisa sukayi ba suka iso gidan nasu sa gudu kowacce tayi gida su tana ƙwalawa mamanta kira , maman Aisha dake shirin ɗora abinci taji maganar Aisha da sauri ta ɗago tace " kaga yaran amare tana washe baki , dariya Aisha ta sa kana tace " ina malam ɗin ? ya fita waje mama ta bata amsa , mai zaki dafa mana mama ? cewar Aisha , mama dake ta fama da wutar murhu tace " taliya ce kinganta nan ita zan dafa , ficewa Aisha tayi batace komai ba ta nufi cikin kasuwa , tana zuwa taga mai kifi ya kasa a faranti , mai kifi nawa gammo ɗaya ? kawo ɗari biyu mai kifi yace " cikin fara'a yana ganin zaiyi ciniki dama tund ya fito babu wanda ya siya , sauƙi fa Aisha tace " tana yagar fatar kifin tana kaiwa baki , mai kifi ne yace "yarinya ga kan kifi ya miƙa mata , karɓa tayi sai da ta dangwala da yaji ta suri gammo guda ɗaya ta arce da gudu tana dariya , ɗora hannu a kai mai kifi yayi yana salati gashi har yana bata kan kifi wanan wace irin yarinya ce ? ya tambayi kansa da zan san gidan su wlh da sai na bita ya ɗauki tirensa yayi gaba yana mita , cikin nutsuwa ta shigo gidan tace " maa ga kifi na siyo miki , riƙe baki mama tayi tace " a ina kika sami kuɗi Aisha ? mama kuɗin da yaya Zakari ya bamu ne shine na siyo a ciki , to ba wai naƙi bane danasan kifi zaki siyowa da nace ki barshi , shigewa ɗakinta Aisha tayi tare da cire hijab tana tuno mai kifi ta ƙyal ƙyale da dariya harda tafawa , mama dake shirin zuba taliya ruwa na tafasa ta girgiza kai dama tasan mai hali baya fasawa Allah ya shirya min ke Aisha lallai matar Zakari tayi fama wlh dan nasan bakwajin magana keda Ummi, tana daga ɗaki ta kwalawa mama kira amsawa mama tayi tace " kin dawo zaki fara ko ? Aisha ce tace" nidai wlh bazan koma gidan yaya ba wlh bazamu koma ba , to me kuma ya faru keda kike ɗoki ? mama ta tambayeta , Aisha dake daga ɗaki tace " antyn tayi mana duka sau shida yaya sau huɗu so sukeyi su kashemu , jinjina zancen mama tayi tace " taɓɓ ashe kun daku maganin marasa ji kenan , ya matar yayan ? mama ta tambayi Aisha , tana nan kwance babu lafiya sai amai takeyi , to masha Allah mama tace " tanajin farinciki , jin kalamar da mama tayi ne yasa Aisha cewa " antyn na ciwo kike murna mama ? mama ce tace " nifa godiya nake yiwa Allah akan Allah ya bawa yayanku da babanku abinda zai ciyar da ku , uhum babafa yana da shi wlh yine bazai yi ba , mamaki maganar Aisha taba mama sbda a iya ƙaracin shekatunta tasan bu mai kyau dakuma marar kyau , tun daga bakin ƙofa malaɓ ya jiyo furucin Aisha a tsawace yace " kinci gidanku waye ya baki damar dawowa ba cewa nayi nabashi ke duka ba? nidai bazan zauna ba wlh cewr Aisha, kinji abinda take faɗa ko wlh zan saɓa miki rasa kunya , muna zaman lafiya zaki zo ki haddasa mana fitina tafiyarki gidannan har yayi saƙat , mama ce ta dakatar da malam da cewa "haba malam wanan yarinyar har guda nawa take da zaka zauna kana gaya mata wanan maganar gaskiya bai dace ba , zoki koma malam ya nunawa Aisha hanya da carbin dake hanunsa , kuka Aisha ta fara tace " wlh bazan koma ba nikam , uban me suke yi miki muma mun gaji dake maza ki fito in tare miki mai mashin inda hamsin a aljihu na , dariya mama tasa tace "malam kenan ba ɗazu kace rabonka da riƙe ashin ma ka mance ba ? harara ya gallawa mama kana yace "to yar baƙinciki shiyasa nace wanan sai ta koma yaushe rabon da muyi faɗa dake gashi tana shigowa muka fara , ya fice yana mita , ganin kukan Aishan babu sauƙi yasa nama cewa " inhar bakiyi shiru ba to wlh zan saɓa miki ya kikeso inyi ne Aisha , share hawayeta tayi tace " mama gobe yaya zai samu a islamiyar can anguwar , to masha Allah mama tace " amma mai yasa bazaki koma ba nifa karki shafamin kashij kaji tom.

Ummi na shiga ta faɗa jikin mamanta tana dariya dubanta maman tayi tace " wai wai naga kinyi ƙiba ne harda kumatu lallai kuna cindaɗi , dariya Ummi tasa tace " mama kullum shayi ta bredi ga ƙwai jiya ma nama mukaci da dare , to masha Allah kice shiyasa kuka mance damu ko ? dariya Ummi takuma sawa.

Dai dai saitin kunen mama Aisha taje tace " gidan yaya ba'ayin tuwo wlh kuma daɗi sukeci ya barki da dafa taliya , girgiza kai mama tayi tace " lallai Aisha aiko ko

duniya zasu ci bazan ce komai ba tunda nima yana yimin badan shi ba da sai dai inyi garinmu tunda ɗan jarin nawa ya ƙarye babu shi babu dalilinsa , mama yau ɗinnan zanyi miki cefane amma bazan bar gidan yau ba har sai anyi bidirin , mama bata fahimci komai ba tace " a ina zaki samu kuɗin Aisha banison rigima fa, ficewa Aisha tayi ta nufi.......!

*MOM ISLAM*
[14/07, 8:19 am] Mom Islam Ce: *YARINYA MAI TAƁARGAZA*

*Zainab Habib [Mom Islam]*

*Wattpad @momislam2020*

*AREWA WRITER'S  ASSOCIATION*

*Page 38 _39*

Ɗakin malam ta nufa kasancewar mama ta shiga ɗaki raba abinci ta nufi gurin ajiyarsa , cikin sa' a ta hango algara rar da yake naɗe kuɗi , ɗaukowa tayi taga kuɗi da yawa ita kanta sai da ta tsorata da ganin wanan kuɗi , mama.... Aisha ta ƙwala kira , na am mama tace "tana daga ɗaki ta fito da sauri , kina inane Aisha ? mama ta tambayeta , gani a ɗakin malam zaro ido mama tayi tare da ɗora hanunta a baki tana salati ta nufi ɗakin malam hango kuɗi a gaban Aisha tana ta taraww yasa mama kiɗima tace " a ina kikaga wanan uban kuɗin Aisha ? a gurin ajiyar malam Aisha taba mama amsa , maza ki mayar dashi mama tace " idanunta na shirin zubar da hawaye , ganin mam na shirin kuka yasa Aish share hawaye tace " mama wlh sai mun ɗibi kuɗinnan tunda bashida tausayi , mama tana mamakin magana irin ta Aisha intayi wata maganar kai kace babbar mata ce , nidai babu ruwna kitafi ki barni da masifar shi gara mu jira Allah ya bamu kowa yayi na gari dan kansa, mama ta juya tabar Aisha da tulin ƙuɗi a gabanta , ƙirga dubu biyar tayi tasa a hula ta tattara sauran tsabar sauri bata sani ba tabar dubu biyu a gurin ta mai da kuɗin ta fito , ganin mama bata gurin yasa ta ficewa da gudu ta nufi shago , malam dake zaune kan tabarma da carbi a hanunsa ya girgiza kai tare da cewa "yarinya sai kace aljana nidai banyi murna da dawowarki ba dan fitina zaki haddasa mana , kai tsaye shagon da ake siyarda kayan abinci ta nufa tace " a bata shinkafa mudu huɗu da kuma magi leda biyu da mangyɗa kwalba ɗaya da manja da wake mudu ɗaya , sai da taga kuɗin ya ƙare duka sanan ta haƙura ya zuba mata a bako daƙyar take tafiya tana jan kayan , ware ido malam yayi tare da ƙwala mata kira yace " meye a cikin wanan bakon kayan abinci Aisha ta faɗa tare da shigewa ciki , farinciki ne ya kama malam a fili yace " mun sami sabil kai masha Allah , tana shigo da kayan takai ƙarƙashin gado ta ɓoye , mama dake kallon ikon Allah tama kasa cewa komai sai da Aishan ta fito tace " badai kuɗinsa kika ɗauka kikayo siyayya ba na faɗa miki banason tashin hankali Aisha haka wancan lokacin yazo yana ta yimin masifa kidinga gudun magana , sai da mama ta gama faɗanta Aisha tace " dubu biyar na ɗauka wlh zaro ido mama tayi cikin fargabar abinda zai je ya zo tace " Aisha kice

yau bazamuyi bacci ba a gidannan wato kin mance ko waye malam ko ? Aisha da ko a jikinta tunda ba tsoronsa take jiba tace " to ai mama iya kaci ya dokeni ke bazai iya dukanki ba , naji amma ai da wani faɗan gara duka ya kikeso inyi Aisha ? Aisha dai batace komai ba ta nufi inda mama ta ajiye mata abinci ta fara ci hankali kwance, tun daga zaure malam ke kwaɗa sallama mamaki ne ya kama mama dan taji muryar tasa kamar anyi masa bushara da aljannah ,wlkslm mama tace " tana jiran shigowarsa yau kuma hadaya muka samu ne naga Aisha da cefane fal jaka , murmishin yaƙe mama tayi tace " ban sani ba , nima kaji muna furci dan karma insa albarka to shikenan ina Aishar ,tasowa Aisha tayi daga inda take tace " malam gani , waye ya baki kayan da nagani a bako ?kuɗinka ne naɗiba dubu biyar Aisha ta faɗa babu alamar tsoro ,kutumar uba malam yace " ya faɗi ƙasa sumamme da gudu mama tayi randa ta ɗibo ruwa tana ta yayyafa masa amma shiru babu nunfashi salati ta shiga yi tana kuka tana cewa "malam ka tashi dan Allah haba malam , malam kam ko motsi bayayi dariya Aisha tasa tace " malam akwai son kuɗi kawai in ɗibo miki dubu biyu a ɗakinsa mu kaisa asibiti ,takaici ne ya kama mama gashi batada kuɗi sisi bata magani , kodai tabi shawarar Aisha ne wata zuciyar tace "ki barshi zai farka wata zuciyar tace " ki ɗauko kuɗin karfa a rasa rai , jeki ɗibo dubu biyu muga abinda Allah zaiyi tana shiga taci karo da ragowar kuɗin da ta bari kwasowa tayi tana cewa " mama ai har nabar wasu a ƙasa ma , mama bata tsaya kulata ba ta fita waje ta nemi temako aka ɗora malam wani ya hau bayansa mama ta tari mashin suka hau ita da Aisha suka nufi asibiti , da isarsu akace kuɗin kati ɗari biyar babu inda mama ta iya haka ta bada kuɗin suka kuma buƙatar dubu biyu , dubu ɗaya da ɗari biyar mama tace " za'a ciko ragowar , basu musa ba suka bashi gado tare da temakon gaggawa , tun 2:30pm suke abu ɗaya har 4:pm shiru sai can sukaji ya nunafasa yana surutai yana cewa " kuɗina kuka ɗiba yanzu kuɗina kuka ɗiba ? likitar da ta fahimceshi tace " wanan bawon Allah anyi masa sata ne ta tambayi mama , ko ɗaya mama tace " tare da miƙewa ta shige bayin ɗakin dage gefe , tana fitowa ta tada sallah tana idarwa tace wa Aisha tayi alwalah , bayan Aisha ta fito mama ta bata tabarma tayi sallah , suka zauna jiran tsammani, alurar bacci sukayi masa cikin lokaci kaɗan bacci mai nauyi yai gaba da shi , zuwa ƙarfe biyar ya farka alhmdulilh ya sami sauƙi aka rubuta musu sallama ,likitan yace " subar ɗari biyar ɗin , godiya mama tayi masa suka nufi bakin titi malam kam babu bakin magana jiki yayi laushi , suna isa gida akayi masa shinfiɗa a tsakar gida yai alwalah yai la'asar , ya koma ya zauna Aisha na fitowa ya tuno abinda ya faru , cikin faɗa yace " ki tattara kayanki ki koma wlh banison zamanki a gidannan zaki iya kasheni , inalilahi mama tace "wacce irin kalma ce haka malam gaskiya ka dena yo inba kasheni takeson yi ba ina ita ina kwasar min kuɗi , Aisha dake shirin zama tace " nifa kwana uku zanyi in tafi ɗazu ma da kuɗinka aka kaika asibiti , uwaki mama ta wurga mata daƙuwa , a zabure malam ya kalli Aisha yace " ba dan kin nuna ba ina aka san da kuɗin ? wlh inga kafin kibar gidannan sai nayi miki duka ,ya juya ga mama yace " kekuma waye yace " ki ƙara ɗaukar min kuɗi ? mama dake shirin tashi tace " ka samu nunfashin ka ya dai daita dole ka fara wata magana ta daban , nayi ɗin malam yace " cikin masifa , wucewa mama tayi ta barsu shida Aisha yana gallawa Aisha harara , malam na kawar da ido Aisha ta sa dariya jiyo sautin dariyar yayi yace "kinyiwa idi dan uwarki ƙanin mamanki mai huɗa , miƙewa Aisha tayi ta nufi waje tana dariya dan malam ma dariya yake bata musamman ma yau , Ummi ce ta ƙwalawa Aisha kira , na'am Aisha tace " ta fice da gudu , samun Ummi na yin alewar gyaɗa tayi da sauri Aisha ta ƙaraso tana cewa " zamu tafi da shi gidan yaya ne? eh Ummi tace " ai kuɗin da yaya ya bamu wanda kika miƙo min lokacin da zamu hau mashin shine nake yi mana wanan , lallai yau da masifa Aisha ta riƙe ƙugu , maman Ummi ce ta fito tana cewa " bazamu ga masifa ba insha Allah , meyasa zaki ɗaukar mata kuɗi ? maman Ummi ta tmbayeta, ita ma fa zata sha ko barta kawai mama , gwalo Aisha tayi mata tare da cewa " woooo ba yau zamu tafi ba ta fice ta dawo gidansu , lokacin malam ya lallaɓa zuwa masallaci , bayan sunyi sallah sai ga malam ya shigo tun daga zaure yake surfa masifa akan kayan da Aisha ta siyo mama

dai na jinsa tayi burus tasan matayi yake nema , ƙarasowa yayi ya banƙaɗa labulen mama yace " ina kayan kuɗina ai sai a ɓani in gani tunda ta iya sata ta kawo miki ke kuma ki karɓa , ni yata bata sata dan haka karka ƙara wanan furucin , ah lallai dole tayi abinda taga dama zaku fito da shi ne ko sai ranku ya ɓaci daga ke har Aishar.......!

*MOM ISLAM*
[14/07, 8:19 am] Mom Islam Ce: *YARINYA MAI TAƁARGAZA*

*Zainab Habib [Mom Islam]*

*Wattpad @momislam2020*

*AREWA WRITER'S ASSOCIATION*

*Page 40 _41*

Mama na zaune ko kulasa batayi ba Aisha kam shirin ma kwanciya take dan bacci ya fara ɗaukarta, yayi faɗan har ya gaji ganin babu wanda ya kulasa yasa ya nufi ɗakinsa , sai da ya zauna ya tuno ai abincin rana yaci bai ci na dare ba ,haka dai ya haƙura ya kwanta , mama ta daɗe batayi bacci ba tana tunanin hali irinna malam da har zasu iya kwana batare da sunci komai ba shikam babu damuwarsa ashe ma yanada kuɗi , miƙewa tayi ta ɗauro alwalah ta kwanta , washe gari da asbha bayan sunyi sallah suka koma bacci, sai ƙarfe 8:am suka tashi aka fara hidimar ɗaura ruwan kunu , ana damawa aka zubawa malam da Aisha mama ta zuba nata , cokali Aisha ta ɗauko tace " mama ina ƙuli ƙuli , an cinye jarin mama ta faɗa , hanyar ɗakin malam tayi ta gaishe sa ta ajiye masa , tana fita ya ciro ƙosai a takarda ya fara ci yana haɗawa da kunun yana mita yana cewa " ko sugan ma bai ji ba , baiji alamun tafiyar mutum ba sai ganinta yai a kansa da kofin kunu a hannu , me kuma ya kawoki Aisha , zata sa masa kuka yace " wlh yarinyar nan kin zamo yar leƙen asiri duk iya iyawata kina neman kaini bango waye ya turo ki , mama ce Aisha ta faɗa da ƙarfi tace " inzo in duba kana shan kunun , malam dake galla mata harara yace " inbansha ba ubanki zansha maza ki ɓace kafin in saɓa miki bakisan har yanzu ban huce da jin gaushinku ba ko ? kuka Aisha tasa tayi ɗakin mama da gudu tace " wlh malam na nan yana cin bredi da ƙosai mama kije ki karɓo naki , a'a ƙyalesa Aisha kowa yai nagari dan kansa mama tace " ta koma ɗaki , malam dake jiyo maganar Aisha cikin ɗaga murya yace " wlh yau sai kin koma gidan su Zakari wlh , babu wanda ya kulashi daga mama har Aisha , zuwa 11:30am sukaji sallamar yaya Zakari. Ganin Aisha tana tattara kwanuka yasa shi cewa " maza ki yi ki gama kizo mu tafi Fiddausi ba lafiya bata iya komai , maƙe kafaɗa Aisha tayi tace " nidai babu inda zani sai dai kai ka tafi , zai kai mata duka mama ta fito tana faɗa hakan shine rarrashi ? sunkuyawa yayi yace " mama kiyi haƙuri tazo mu koma ne Fiddausi babu lafiya , guduwa ɗakin mama Aisha tayi tace " wlh bazani ba da ƙarfinta , dariya mama tayi tace " to ai sai ka shigo daga zuwanka zaka fara ɗaukar hukunci , ina Ummi yaya Zakari ya tambaya , Aisha da take can ɗaki tace " Ummi na gidansu dama ita keson zuwa gidanku , yaya Zakari ya tunzura matuƙa to shikam mai suka

yiwa Aisha take gudunsu ? duk cikin zuciyarsa yake mamaki , shigowar malam ne yasa yaya Zakari neman gurin zama tare da tsugunawa ya gaida shi , lafiya malam yace " cikin ƙaguwa kazo tafiya da Aishar ne ? " eh yaya Zakari yace " yasan ko bataso dole ta fito tunda har malam ya sa baki , maza ki fito Aisha ki koma gidan ku kar in ƙara yi miki magana , Aisha dake shirin kuka ta fito sanye da hijab tana ɗan share yar ƙwlar da ta fito daga idon ta.
Am malam na mance ban faɗa muku ba nasi mota dama inada ɗan kuɗi to ogana ya cikamin kafin su malam suce wani abu tuni Aisha ta daka tsalle tayi waje tana ihu , masha Allah mama da malam sukace Allah ya sanya albarka ya tsare mana kai duk inda ka shiga Allah ya kareka daga dukkan sharri .amen yaya Zakari yace " ya miƙawa mama ɗari biyar malam ma ɗari biyar yace " ni zan wuce sai gobe zan tafi da Aisha inta yarda , caraf malam ya karɓe da cewa " au karma ta yarda wlh sai ta bika barin dubota , mama dai shiru tayi fitar malam ta juyo da kallonta ga yaya tace " ya jikin Fiddausin ?da sauƙi yayan yace " amma fa bata iya wani aiki amai ke damunta , Allah ya bata lafiya mama tace " bari a kira Aisha zaka tafi da Ummi ne? eh yaya Zakari yace " ai dole tafiya sai da Ummi inba haka ba Aisha bazata zauna ba to mama tace " suna jiran shigowar malam .hanunshi a na Aisha gam ya miƙawa yaya Zakari yace " maza ku tafi amma dai ka sanya ta a islamiya ? eh yaya Zakari ya bashi amsa yau dama zamu wuce makarantar da su , su kuma suwaye ? malam ya tambayi yaya , Aisha da Ummi ne , Ummi kuma to bazata koma ba cewar malam , ihu Aisha tasa tace " wlh in Ummi bataje ba ko an tafi dani sai na gudo ,zaro ido malam yayi kana yace " wai ke yarinyar nan kamar ba mutum ba ina magana kinayi wlh zanyi miki ruɗu ruɗu da jiki kafin kibar gidannan , miƙewa yaya Zakari yayi ya nufi gidansu Ummi samunta yayi harta yi wanka ta fito da yar ledarta a hannu gaisawa sukayi da mamanta yace " zamu tafi ne , cike da fara'a maman tace " to Allah ya kai ku lafiya Ummi banda gigiwa a natsu dan Allah , Ummi na washe baki tace " to mama suka fice , suna dawowa gidan ya samu Aisha ta fito su take jira sallama ya yiwa su mama ya fice dasu, Allah ya tsare mama da malam sukayi musu .suna fita yaya ya buɗe musu back side waro ido Ummi tayi a fili tace " wanan motar fa ? Aisha dake turo baki tace"motar yaya ce yarinya , cike da murna suka shige mota yaya yace " yawo zamuje yau zamu zaga gari , tsalle suka shiga yi .
Sunyi nisa da anguwar suka hango wata mota na bin bayansu tun yaya Zakari na bata hanya yaja ya tsaya , ganin motar ta nemi guri yasa shi yin kamar yana jiran wani abu ne , rage glass ɗin motar saurayin dake mazaunin driver yayi ya miƙowa yaya zakari hannu , saurayin da a ƙallah zai yi shekara talatin a duniya , matashi ne bugu da ƙari ga kyau kai kace ɗan india gashin idonsa kamar na mace pink lips ɗinsa abin sha'awa ga baƙin saje da ya kewaye fuskarsa bugu ƙari ga shi fari kyakyawa indai taƙaice muku zance iya haɗuwa wanan gayen ya haɗu , barka aboki na Khamis yace " wa yaya Zakari yawwa barka amma sai dai ban gane ka ba , cewar yaya Zakari murmishi Khamis yai yace " suna na Khamis ɗa ga Alhaji Abubakar mai nera ba lallai ka sanni ba amma nasan kana jin labarin mahaifina a faɗin ƙasarnan , Khamis na maganar yana kallon su Aisha dake back side sunata wasa ita da Ummi , lura da irin kallon da Khamis ke yiwa su Aisha anya babu ayar tambaya ? yaya Zakari ya faɗa cikin ransa, ok na gane shi tabbas ai ba ɓoyayye bane yaya Zakari ya faɗa , jim Khamis yayi yace " wa inan ƙanenka ne ? eh yaya Zakari yace " tare da haɗe rai , masha Allah Khamis ya faɗa ko zaka bani adress ɗinka ? waro ido yaya Zakari yayi to menene dalilin hakan? ya tambayi kansa , tsintar kansa yayi da bashi harda number waya , godiya Khamis yayi yana sakarwa Aisha da Ummi kyakyawan murmishinta , hankalin Aisha ne ya karkato ga yaya tace " yaya dama kanada aboki bature ne ? eh yaya Zakari yace " dan a halin yanzu yafara dana sanin bawa Khamis adreshin sa dakuma lambar waya, gashi yaja mota yayi gaba bayan haka yana ta yiwa su Aisha murmishi, ya daɗe a gurin ya juya suka nufi gida dan bayajin zai iya kaisu inda yayi niya , yaya naga kayi hanyar gida? Aisha ta tambaya ,eh mun fasa ne haɗe rai sukayi zuciyarsu babu daɗi haka ya dawo gida yai parking motar a waje suka buɗe suka nufi cikin gidan , da sallama suka shiga babu motsin kowa gidan

kamar ba mutane kai tsaye ɗakin anty Fiddausi suka nufa samunta sukayi kwance a palo duk ta rame ga awara cikin farar leda a gefe , hankalinsu na kan awara suka ce ina wuni anty , ɗago kai tayi tace " lafiya shine kuka gudu ko ? dariya suka sa suna cewa " nan ba'a yawo shiyasa , yaya Zakari ne ya shigo hanunsa riƙe da baƙar ledar kankana a yayanke ajiye wa yayi ya nemi guri ya zauna ya ɗauko ledar tare da mimiƙa musu kowa ɗaya suka tashi zasu fice yace " in bazaki ci awarar nan ba kibasu man , basu Fiddausi tace " ta mayar da kai ta kwanta......!

*_MOM ISLAM_*
[14/07, 8:20 am] Mom Islam Ce□: *YARINYA MAI TAƁARGAZA*

*Zainab Habib [Mom Islam]*

*Wattpad @momislam2020*

*AREWA WRITER'S  ASSOCIATION*

*Page 42 - 43*

Gidane tangameme kyau da tsarin gidan abin kallo ne tsayawa misalta haɗuwarsa ma ɓata lokaci ne .
parking Khamis yayi da motarsa wata budurwa naga ta taho tana cewa " bro yau kuma da kanka kake driving? Afnan ba wani guri naje ba so karki damu mu shiga ciki , wace ya kira da Afnan ɗin ta riƙe masa hannu suka shige tsararren palon gidan da yaji kayan alatu , a ƙallah zatayi shekara sha tara da aihuwa ,fara ce sosai kamar balarabiya ga dogon hanci ,suna shiga suka tarar da wata dattijuwar mata mai kama da Khamis cikin fara'a matar tace " my son ina kaje haka tun safe ? mami karki damu ba wani nisa nayi ba , amma wlh ina cikin damuwa ammi na ya marai raice fuska kamar mai shirin kuka  , damuwa kuma my son ? ammi ta tambaya dan san jin ko menene , Afnan kallonsa take ko ƙiftawa babu dama in sun zauna akan sami hakan ta mutu a kansa shikam bai san ma tana yi ba, tashi ki bamu guri Khamis ya faɗa tare da kallon Afnan , turo baki tayi tace " Ammi kin gansa ko ? murmishi Ammi tayi tace " ƙyaleta son karka damu ina jinka , gyara zama yai tare da ruƙo hanun Ammi ya haɗe da nasa yace " Ammi naga matar aure , a gigice Afnan takai dubanta ga reshi ga mamakinta da gaske yake maganar babu alamun wasa , alhmdulilh my son dama ina baƙin cikin ace duk iya wanan shekarun naka babu mata ai babu daɗi , a ina take?" Ammi ta tambaya  ,a Tudun wada ne nama sami adrees ɗin gidan su , farinciki fal zuciyar Ammi Afnan kam miƙewa tayi fuu kamar zata tashi sama ta bar gurin , babu wanda yai maganarta sukaci gaba da hirar budurwar da yace " yayi sai kwatantawa Ammi kyau irin nata yake yi, to naji tashi muje kaci abinci nasan babu abinda kaci cewar Ammi , no Ammi ni wanka zanyi yanzu in tafi ki tayani da adu'a ,Ammi da fara'arta tace " insha Allah amma sai kaci abinci , miƙewa yai ya nufi dining ya buɗe flaks tuwon shinkafa ya gani yana buɗe kular miyar yaga miyar kuɓewa ɗanya , murmushi yayi yace " my Ammi yau love me over , dariya Ammi tasa tace " in banyi maka ba wa zanwa my son farincikin ka shine nawa i love you my Ammi na , love you too my son Ammi ta faɗa tana dariya , wanke hanunsa yai ya fara

kai loma kasancewar gwani ne gurin cin tuwon shinkafa miyar kuɓewa , yana gama ci ya buɗe farfesun kaji yaji kaɗan ya ɗauki hollondia yasha ya miƙe yace " my Ammi yau fa kiyi haƙuri hira zani gurin surukarki , dariya Ammi ta kuma sawa tana girgiza kai , yazo wucewa zuwa bedroom ɗinsa yaci karo da Afnan tsaye tana kuka , to lafiya ke kuma ? Khamis ya tambayeta tare da shigewa bedroom ɗin nasa ba tare da ya tsaya jin amsarta ba , kuka ta kuma fashewa dashi cikin ranta tana mamakin halin ko in kula da lamuranta.
Khamis na fitowa daga wanka ya nufi gaban mirorr ya shafa haɗaɗun mayukansa da turare , kayan da ya ɗauko ya sanya shadda ce gezna blue wace tasha aiki ya sanya hula ya ciro sabon takalminsa yasa yakuma feshe jikinsa da zafafan turaruka , ya ɗauki wayoyinsa ya fito palo a inda yabar Ammi anan ya sameta tana zaune amma hankalinta na TV Ammina na fito , Khamis yace" masha Allah ka gaida suruka kace ina gaisheta , duk wanan zancen da akeyi Afnan na rakuɓe a gefe tana kallo , fitowa harabar gidan yayi kai tsaye parking spice ya nufa drivers ne suka fito da gudu suna cewa " barka mai gida , ywwa kawai Khamis yace " kowa ya koma mazauninsa ba nisa zanyi ba , to suka ce Allah ya kiyaye hanya ,Khamis yace " amen , motarsa ya ɗauka aka buɗe masa get ya fice cike da nishaɗi , tafiya yake amma bangaren zuciyarsa wanan yarinyar da ya gani ta tafi da tunaninsa tabbas yana sonta, yayi tafiya mai nisa ya iso anguwarsu danna lambar yaya Zakari yayi ring ɗaya aka ɗauka , cikin sanyin murya yaya Zakari yace " dawa nake magana ? Khamis ne wanda kaba adrees ɗazu , ok yaya Zakari yace " na gane fatan dai lafiya ? eh lafiya gani a anguwarku zaro ido yaya Zakari yayi yace " to gani nan fitowa , haɗa ido sukayi da anty Fiddausi tace " lafiya ? lafiya yaya Zakari yace " kana ya ɗauki wayarsa ya fice , yana fita ya shiga waige dan Khamis ya sauya mota bata ɗazu bace , fitowa Khamis yayi yana murmishi tare da ƙarewa gidan yaya Zakari kalo jinjina kai yayi ba tare da yace " komai ba , abokina Khamis ya faɗa cikin ɗagun murya ,juyowa yaya Zakari yayi cikin ransa yana cewa " to me wanan bawan Allahn yake so a gurina , ƙarasowa yaya Zakari yayi zuciyarsa cike da was wasi da kuma fargaba tabbas Khamis shine wanda ake hira da shi gidajen talabijin da dama to gashi yanzu ya gansa a zahiri any ba wani abu yake nema ba ? Khamis ne ya katse masa zance da cewa " barka da yamma ya miƙawa yaya Zakari hannu, shima yayan hannu ya miƙawa Khamis suka gaisa Khamis yace " ya yarannan lafiya yaya Zakari yace " yana basarwa dan Allah farar ciki nakeson ka gaya min sunanta , zaro ido yaya Zakari yayi yace "wa enan yaran fa shekararsu goma sha ɗaya wanan shekarar ce ma ta sha ɗayan murmishi Khamis yayi yace " koda ganinsu ai mai hankali zai gane shekarunsu , zamu gaisa ne kawai , basa nan yays Zakari yace " cikin ɗaure fuska  , ina sukaje ? Khamis ya tambaya , jin shishigin na neman yin yawa yaya yace " sun koma islamiyar kwana , shiru Khamis yayi kasancewar sa mutum mai saurin fahimtar ƙarya da gaskiya , ya juya kansa yana shirin shiga mota yace " dan Allah in sunzo ka gaishe su , tom zasuji yaya Zakari yace " tashin motar Khamis ne yasa shi jan gauron nunfashi yafara tunani mai kiɗimarwa , kasa ƙarasawa gida yayi ya dawo ƙofar gidansu ya sami dakali ya zauna sai tambayoyin Khamis suke dawo masa sabo.
Cikin hikima malam ya shigo da fara'arsa ya sami mama ta gama jollof ɗin shinkafa da taliya sai ƙamshi take , mama na ganinsa ta ɗaure fuska ta juya kai gefe , ta tare babbar riga malam yayi tare da rataya carbi a kansa yace " haba maman Aisha fushi ake dani wanan yarinyar tazo ta haɗamu dake ko tazamo tauraruwa innalilahi mama tace " kafin malam ya ƙarasa , cikin zafin rai tace " inaga dai Aisha ba yarka bace ko ? kake siffanta ta da abubuwa marasa kyau ga tsana da ka ɗora mata, anya kana tunanin wanan abin bazai fanɗara zuciyarta ba , to to yimin faɗa malama yanzu dai zubomin abincin inci tukun ko shima baza'a bani ba sai anyi min faɗa ? ni na isa ? gaskiya nake gaya maka , mama tace " ta miƙe ta shige ɗaki ta barshi a gurin.
tukunyar ya nufa kai tsaye tare buɗewa ya ɗibi abinci iya san ransa mama bata sani ba.
Washe gari malam ya tashi da azababben zazzaɓi mama da ta shigo gaishesa ya buɗe ido ya gallah mata harara yace " wato shinkafar da na ɗiba jiya dan baki bani

ba shine yau na tashi da mugun zazzaɓi to ban shirya mutuwa ba ,malam ya faɗa yana cigaba da masifa , sai da ya gama , mama tace " tunda masifa kake nema kwana biyu gara in barma gidan ,me amfanin zama na kana nufin ni maiyya ce ko yaya ? jin mama tace " zata bar gidan yasa wani mugun zufa ketowa malam yasan inhar mama tabar gidan kashinsa ya bushe....!

*_MOM ISLAM_*
[14/07, 8:20 am] Mom Islam Ce: *YARINYA MAI TAƁARGAZA*

*Zainab Habib [Mom Islam]*

*Wattpad @momislam2020*

*AREWA WRITER'S ASSOCIATION*

*Page 44 _45*

Shigewa ɗaki mama tayi dan fitinar malam tafara isarta.
Koda Khamis ya koma gida babu wanda ya kula duk da yaga Ammin nasa a palo amma ya wuce ta ko kulata bai yi ba , ganin haka ba ƙaramin tashin hankali ta shiga ba miƙewa tayi ta nufi bedroom ɗinsa da ɓacin rai a fuskarta inhar yana cikin damuwa baya kula kowa , tura door ɗin tayi tare da sallama, my son maiya faru naga ka shigo cikin damuwa ? kansa a sunkiye duk da sanyin AC dake kaɗawa bai hanashi zufa ba kamar wanda yayi wanka , zama Ammi tayi kusa da shi ta ruƙo hanunsa tana murzawa cikin sanyin murya tace " bayan rasuwar Abbanka banida buri banda indinga ganinka cikin farinciki da kwanciyar hankali ,gashi duk iya ƙoƙari na yau naga na gaza Ammi ta fashe da kuka , a razane Khamis ya ɗago ya kalli Ammi ya kwantar da kansa a kan ciyarta ya saki kuka , tsagaita kukan nata tayi tace " to faɗa min maiya faru ? Ammi ina sonta Ammi yayanta baya sona zaro ido Ammi tayi tace " yanzu akan wanan kake tada hankalinka ? insha Allah zan shige maka da yardar Allah my son karka sami damuwa kuma bana son in ƙara ganinka cikin wanan yanayin , tom Ammi Khamis ya share fuskarsa yace " Ammi yunwa nakeji , Ammi da farinciki ya kamata ganin ɗan nata ya sake ta kamo hanunsa ta nufi dining dashi ta buɗe faten dankali wanda yaji kifi da kayan lambu ta shiga bashi a baki yana ci suna hira yana ƙara kwatanta mata kyau irin na Aisha amma har yanzu bai faɗa mata Aisha yarinya bace , bayan Ammi ta gama bashi ya miƙe yana dube dube tare da cewa " Ammi ina Afnan ? Afnan taje gidansu ɗazu cewar Ammi , jimm Khamis yayi yace " ko lafiya Ammi ? Ammi dake tattare plet tace " oho na dai ga ta ɗau bag fuska babu walwala na tambayeta menene tace " babu komai so nikuma gaskiya ban matsa mata ba tunda ba yarinya bace, shiru Khamis yayi ya riƙo hanun Ammi yace " gobe zamu ko ?" murmishi Ammi tayi tace " insha Allah.
Washe gari yaya Zakari zaiyi sammakon fita yace " su Aisha suzo ya kaisu makaranta sbda ya gama komai zuwa kawai zasuyi , cikin jin daɗi ya daukesu a mota bayan su gamawa anty Fiddausi gyare gyare , yana kaisu islamiyar ya wuce gidan su , da shigarsa ya samu malam na surfa faɗa , sallama yayi tare da durƙusawa ya gaida malam cikin fara'a malam ya amsa yana tambayar su Fiddausi , suna lafiya yaya

Zakari yace " tare da miƙewa ya nufi ɗakin mama samunta yayi kwance nunfashi na sama da ƙasa a razane ya ƙarasa kanta ya tallafo ta yana cewa " sannu mama , da ƙyar take amsawa tana yi masa nuni da hanunta , kallon inda take nunawa yayi yaga ashe maganin ulcer zai ɗauko mata cikin azama ya ɗauko ya tsiyaya mata ya bata yana mai ƙara yi mata sannu , samun guri yayi ya zauna ganin bacci ya kwasheta ga zufa tana yi alamun ciwon ƙirjin ya sauka ,miƙewa yayi ya fice " lokacin malam ma yabar gidan , kai tsaye chemist ya nufa ya siyo mata kalar maganin da take sha ya wuce gurin mai siyarda kaji ya siya mata ɗaya shagon dake gefensa ya nufa ya haɗo mata kayan shayi ya fito , komowa gida yayi lokacin har ta tashi tana riƙe da buta a hanunta , cikin fara'a yace " masha Allah mama jiki yayi sauƙi , cikin sakin fuska mama tace " eh wlh gashi har zanyi sallah ma , shigewa ɗaki maman yayi ya zauna jiranta , bankaɗo labulen malam ne yasa yaya Zakari ɗago kai , malam ne ya cire aswakin bakinsa yafara surfa bala'i yana cewa " ai ba nisa nayi ba duk abinda ka siyo a ido na dan babu abinda ban gani ba tayi ta fito a raba a bani nawa ehe ya ƙarasa shigowa ya nemi kujera ya zauna.sunkuyar da kai yaya zakari yayi yace " dama ku biyu na siyowa banida burin fifita mutum ɗaya , shiru malam yayi yana dai jiran shigowar mama , da sallama ta shigo babu wanda ta kula ta shimfiɗa darduma ta tada sallahar azhar tana idarwa tayi adu'ointa ta shafa ta cire hijab ɗin ta , ta janyo ledojin ta fito da komai waje ta raba kazar gida biyu tabashi rabi ,tana shirin raba kayan shayin ya dakatar da ita da cewa " me ya kawo raba kayan shayi zan koma girki na ne ? oho mama tace " ta miƙawa yaya Zakari kazar tace " yaci shima a'a yace " mamakin halin malam yasa shi shiga damuwa matuƙa , mayarda kayan shayin tayi ta ajiye tare da ficewa waje ta barsu shi da yaya Zakari a zaune.
Ring ɗin da wayarsa take yi ne ya dawo da shi daga duniyar tunani , malam dake shirin tashi yace " ba kiranka akeyi ba ? ciro wayar yayi a aljihu ganin number da ake kiransa yasa shi kallon malam , hakan baya malam damar ƙin fita yana son yaji ko meye , ɗaga wayar yaya Zakari yayi tare da sallama bayan sun gaisa da Khamis , Khamis yace " abokina yau muna nan zuwa fa yanzu muka fito daga gida , bana gida yaya Zakari ya faɗa cikin dakewa , a ina zan sameka ?dan Allah nida Ammi na ne ,Khamis ya faɗa cikin marai raice fuska , yaya Zakari daya ƙosa da magana yace " gani a gidan mu , miƙawa Ammi wayar Khamis yayi ,yaya ne yaji muryar mace dattijuwa ɗana nice mahaifiyarsa kayi haƙuri kayi mana kwatance alheri ne zai kawomu dan Allah , to kawai yaya Zakari yace " ya shiga yi musu kwatancen anguwar ,Ammi ma tasan anguwar godiya Ammi tayi masa sukaci gaba da tafiya.
Malam dake tsaye yace " kai dawa kake magana ne ? nida wasu ne tun ranar da nazo muka tafi da su Aisha a hanya ya tsayar dani kuma bayan haka har anguwarmu ya biyoni wai yanason ɗaya daga cikinsu , murmishi malam yayi cikin ƙarfin murya yace " Allah yasa Aisha ce , razane yaya Zakari ya ɗago yana kallon malam , malam Aisha fa shekararta sha ɗaya ko ka mance ne , washe baki malam yayi yace " ai ko tara ne zamuyi koyi da halin manzon mu , mama dake waje zuciyarta nayi mata ɗaci ta girgiza kai ta dawo ɗakin ganin malam na shirin komawa ɗakinsa , malam na fita yaya ya dubi mama yace " mama anya malam ba rikicin tsufa ya fara ba ? hmm mama tace " babu wani rikicin tsufa inaga ya ware ta daga cikin ƴaƴan daya haifa ne , ring ɗin da yakuma ji a karo na biyu ne yasa shi miƙewa yace " mama ki shinfiɗa tabarma inaga sun ƙaraso , miƙewa mama tayi ba tare da ta ƙara magana ba ta fito da tabarma ta shinfiɗa Allah yasa gidan a share yake ta dawo ɗaki , fitowa yaya Zakari yayi yace " sun fa iso barin je , to mama tace " ta koma ɗaki ta zuba uban tagumi wai ƴar Aishanta ne ake zuwa gurinta anya ma Aisha ake nema kuwa ? ".
Khamis dake back side kusa da Ammi yace " Ammi wlh anguwar nan babu daɗin tafiya duk wari , dariya ma yaba Ammi tace " daɗinta ba nice nazo da kai ba kaine kazo da ni nidai bazance komai ba , hango yaya Zakari na dube dube yasa Khamis ɗago masa hannu yace " abokina gamu anan , mamaki ne ya kama yaya Zakari ganin mota ta uku kenan kuma duk daban to wa enan wane kalar kuɗi ne dasu , kawai da zancen yayi ta hanyar miƙowa Khamis hannu da ya fito yanzu , fitowa Ammi tayi

tana murmishi , tsugunawa har ƙasa yaya Zakari yayi ya gaisheta amsawa tayi cikin fara'a tare da tambayarsa iyayensa suna lafiya yaya yace " kana yayi musu iso har cikin gidan, dajin motsin su malam ya fito yana washe haƙora yana yi musu barka ,ƙwalawa yaya Zakari kira yayi  yaya Zakari na zuwa malam ya miƙa masa dubu ɗaya yace " ka siyo musu lemu kayi sauri , da mamaki yaya Zakari ya fice ya siyo lemu guda huɗu da ruwan gora ya kawo musu , godiya Ammi tayi ta gaishe da mama , bayan sun gama gaishe gaishe Khamis ma ya gaishe su , Ammi ta fara gabatar da abin da ya kawosu . yara ne su biyu nidai yace " min fara to sunanta muke son ji kuma muna neman arziƙi na neman ita yarinyar , karkuga nazo ni mace Allah ya yiwa maigidana rasuwa kuma ƴan uwana suna Nigar in magana tayi ƙarfi zasu zo , karaf malam ya amshe da kai Zakari wacece a ciki ?Aisha ya nuna cewar yaya Zakari , masha Allah momy tace " kasancewar sunan mahaifiyarta Aisha  , maza kirawo ta kokuma kasa a ɗauko ta su gaisa , mamaki ne ya kama mama kamar yana neman kai da ita gudun kar ta bashi kunya yasa ta yin shiru ,suna islamiya yaya Zakari yace " a'a babu damuwa ai inhar an bamu izini sai yaci gaba da zuwa Ammi tace " cikin jin amsar da za'a bata , mama da sai yanzu zatayi magana tace " baiwar Allah bakisan ko waye Aisha ba shekararta sha ɗaya fa , a razane Ammi ta ɗago ta kalli Khamis da ya sunkuyar da kai ƙasa yana wasa da yatsun hanunsa tsabar fargaba , kanada hankali kuwa Khamis yarinyar da da ace anyi maka auran wuri ka haifeta , gyɗa kai mama tayi tana adu'ar Allah ya kare mata Aishan ta , kuka Khamis ya fara yana cewa " Ammi mutuwa zanyi inhar ban aureta ba , kunya ce ta kama Ammi tace " oh ko kunyata bakaji ko ? my son  am sorry Ammi bansan ranki zai ɓaci ba kiyi haƙuri Malam da mama da yaya  Zakari mamaki suke amma malam shikam burunsa yaji zancen maganar auran Aisha, kan Ammi ya kulle tasan zasusha raino , to malam muna bara cewar Ammi , babu damuwa ai duk arxiƙi ne Allah ya dai daita su , amen Ammi tace " tare da godiya , murna fal cikin Khamis ji yake kamar zai tashi yayi rawa amma babu hali , miƙewa sukayi Ammi ta ajiye bandir ɗin ƴan ɗari biyar biyar sukayi wa su mama sallama , har bakin mota yaya Zakari ya rakasu Khamis sai godiya yake ta yiwa yaya Zakari , kunya ma yaya Zakari yaji yayiwa Ammi Allah ya tsare ya shige ciki , yana shigowa yaji hargagin malam na cewa " ai wlhi sai mun raba kuɗinnan shine suna tafiya naje bayi in dawo kika kwashe kuɗin ko ?".
Zakari ɗibo min lemukan nan tunda basu sha ba miƙon kawai , miƙo masa yaya Zakari yayi ya koma gefe yana kallon ikon Allah malam harka ta kuɗi babu sanya hankali ya tashi , ya miƙe ya dunfaro mama yace " raba uku kiba Zakari kibani kema ki ɗauka , inaaa mama tace " babu rabon da zanyi tunda ka tattago zancen aure kayan tari zan fara siya mata ko so kake sai auran yazo inyi wuƙi wuƙi da ido sai dai in zanbar gidannan yau amma bazan bada ba, taɓɓ yau akwai tashin hankali a gidannan muddin baki kawo kuɗinnan ba , yaya Zakari da ya gama yi musu dariya a ciki yace " to malam ka barwa maa tunda ta kawo uzurinta , gidanku nace dan bakada hankali dana baka dubu guda sai da ka kasota duka gashi ko sha basuyi ba ai tabani wani abun in rage zafi ko ? malam kayan tari fa tace " kayan tarin gidanku ? malaɓ ya watsa masa daƙuwa to kuɗinnan kamar naci , miƙewa yaya Zakari yayi ganin abin babba ne yace " sai gobe zani ɗauko yara a islamiya , Allah ya kaimu su malam sukace....!

Wlh zan koma wattpad da facbok dan sunfi shar'hi naga kamar kun gaji ne🙄.

*_MOM ISLAM_*
[14/07, 8:21 am] Mom Islam Ce🙄: *YARINYA MAI TAƁARGAZA*

*Zainab Habib [Mom Islam]*

*Wattpad @momislam2020*

*AREWA WRITER'S  ASSOCIATION*

*Page 46 & 47*

Yana zuwa bakin get ya samu an tashe su dube dube ya shiga yi amma bai hango su ba , fitowa yayi daga cikin motar ya fara waige hangosu yayi ko wacce ɗaure da hijab ɗinta a kwankwaso suna dame da wata budurwa da aƙallah zatayi shekara goma sha biyar , amma da alamu sun sata kuka , da sauri ya ƙarasa gurinsu ya samesu sun ganshi suna sa hijab ,faɗa ya dinga yi musu yace " wa budurwar meye naki na kulasu ba ƙannenki bane , bata kulashi ba ta ja jakarta ta wuce " cikin tsoro suka shige mota suna wuli wuli da ido , suna isa ƙofar gidansu yayan suka buɗe murfin motar da gudu suka shige , ganin anty Fiddausi zaune da kwanon awara a hanunta  yasa cewa " sanu anty suka wuce ciki , bayan sun cire uniform suka fito neman abincin dare , tambayar anty Fiddausi sukayi ina abincin su ? yatsina fuska tayi tace " ai sai dai ku girka banyi ba , karaf a kunen yaya Zakari da ya shigo yanzu, yace " haba yarannan fa sunyi aiki ɗazu girki ma yana neman ga gararki taɓ ku koma ku zauna barin yi muku girkin , tana kallonsa ya shiga kitchen ya haɗa komai yai sanwar taliya harda ja ɉage ya gama ya fito , ruwa na tafasa yasa taliya ya juya ya dawo waje yana  ƙarewa Fiddausi kallo da mamaki a fuskarsa , amma baiyi magana ba .
Tun a mota Ammi ta fara faɗa tana cewa "ashe kai yarinyar da kake nema ƙarama ce kasa naketa ƴar murya to inka aureta ya zakayi da ita ? kokuma za'akai ajiyar dukiyar aure ne ? da sauri       Khamis yasa a'a Ammi wlh inhar ban kasance da wanan yarinyar ba zan iya mutuwa , Ammi kam kunyar zancen nasa taji amma shi ko a jikinsa, suna isa gida Ammi ta shige ta barshi a mota ranshi in yayi dubu ya ɓaci inda batason ɓacin ransa  haka shima baya son nata , da gudu ya fito ya nufi part ɗinta ganin bata nan yasa shi juyowa ya dawo palo tare da haɗa kai da guwaiwa ya rasa me ke yi masa daɗi , fitowar Ammi ne yasa shi saurin miƙewa ya kamo hanunta cikin murya ta mai shirin yin kuka yace " Ammi na ki gafarce ni na haƙura da maganar Aisha , hawaye na sintiri a fuskarsa , hankalin Ammi a tashe taya za'ayi Khamis ya yarasa wacce zai nemo sai ƴar 11yrs ina bazai yuwu ba ,Ammi ta faɗa a fili , jin tace bazai yuwu ba yasa Khamis miƙewa ya nufi bedroom ɗinsa ya sa key ya faɗa gado yana mai sakin marayan kuka.
Washe gari har ƙarfe tara  shiru babu labarin Khamis bai fito ba kuma Ammi ta gwada wayarsa shiru , hankalinta ya tashi sosai tama rasa dabara , ƙara zuwa bakin ƙofar ɗakinsa tayi ta bubuga amma shiru ta kira sunansa yafi a ƙirga bai amsa ba , Ammi tayi ficiki ficiki kamar mai ciwo ga gida ita ɗaya , rashin extra key beyi ba Ammi ta faɗa tana share hawaye , da wowa palo tayi ta zauna tare da rafka uban tagumi tana jiran tsammani , takai awa ɗaya zaune a gurin babu motsin fitowar Khamis kodai ya mutu ne ? Ammi ta tambayi kanta .
 bayan yaya ya gama girkin ya ƙwalawa su Aisha kira , a kasalance suka fito kasancewar sun galabaita da yunwa maza kuje kuci yaya ya faɗa , ɗauka Aisha tayi sukaje suka fara ci suna hira  , zubawa anty Fiddausi yayi ya shige ɗakin ya miƙa mata kasancewar ta koma ɗaki, da sauri ta karɓa da alamu yuwa takeji amma

tayiwa kanta na ƙin yi girki , ba tare da ta tambayesa yaci ko baici ba ta fara kaiwa cikinta , zama yayi yana ƙare mata kallo darajar cikin dake jikinta yasa yake tausaya mata badan haka ba bata isa ba.
bayan sun kammalah cin abinci sukayi sallah suka kwanta.
Kwanan Khamis biyu a kulle idanun Ammi sun ƙanƙance tsabar kuka agajin drivers da masu gadi ta nema akazo aka fara buge ƙofa , cikin sa'a ƙofar ta buɗe, wani uban wari ne ya ziyarci hancin su Ammi toshe hanci Ammi tayi tana dube dube , hangosa tayi can ƙarƙashin gado kamar wanda ya shekara yana ciwo da salati ta ƙarasa gurinsa tana kiran sunansa , baya iya magana sai ɗago hannu da yakeyi , cikin azama Ammi ta kama hanunsa tana shirin miƙar dashi , mai gadi ne ya temaka mata ta miƙar dashi ta nufi toilet dashi tace " suje ta gode , wanka Ammi tayi masa da brush ta shafa masa mai ta temaka masa ya sanya kaya ,ta zaunar dashi bakin gado , baya iya zama hakan yasa tana zaunar dashi ya ɓingire a gurin kasancewar jikin babu ƙwari , daƙyr Ammi ta iya fito dashi palo ta ƙwalawa ƴar aikin gidan kira ,da sauri tazo ta tsuguna gaban Ammi , Fati maza ki gyara ɗaƙin son kar inga datti cikin ladabi tace " to ta miƙe ta nufi ɗakin nasa , driver Ammi ta kira tace " hospital zai kaisu , a ga gauce suka fito dashi aka sanya a mota suka nufi hospital, da isarsu aka fara bashi kulawar gaggawa ruwa aka ƙara masa da alurai bacci yai nasarar ɗaukarsa , zuwa 12:pm ya buɗe ido fuskarsa ta ciko babu laifi sunan Ammi ya kira hawaye na zuba ta gefen idonsa , na'am Ammi tace " taja kujera dan taji mai zaice, Ammi na ki yafe min bazan ƙara yin abinda zai ɓata miki rai ba na haƙura da Aisha Ammina na haƙura .Ammi ce taji maganar kamar wasiyya hakan yasa hankalinta kuma tashi tace "my son insha Allah sai ka auri Aisha koda arziƙin da muka mallaka zai ƙare ta hanyar nemanta ni Amminka zan temaka maka da yardar ubangiji , murmishi Khamis yayi ya na shirin sauƙowa daga gado fuskarsa ɗauke da fara'a sai dai ramar da yayi sosai ta baiyyana , mayar dashi Ammi tayi tace " bakaga drip a hanunka bane my son ? naji sauƙi Ammi na sami lafiya , cewar Khamis naji Ammi tace " koma ka  kwanta yakusa ƙarewa ma komawa yai ya kwanta yana ganin fuskar Aisha nayi masa yawo .
Zuwa yamma aka biya komai aka sallamesa suka dawo gida , duk da jikin nasa babu ƙwari amma yana maganar zuwa gurin Aisha , Ammi mamakin wanan irin so takeyi , dole ta la llaɓa shi gudu karya ƙara yin irinna jiya , sun samu Fatima wato ƴar aikin gidan ta gama abinci dining kawai  suka nufa ,sai da Ammi da Khamis suka cika cikinsu sanan suka miƙe kowa ya nufi part ɗinsa , jin ana kiran mgrib yasa Khamis fitowa bayan yayi alwalah ya nufi masallacin gidan , Ammi ma alwalah tayi tayi sallah , jin wayarta na ring yasa ta ɗagawa bayan ta duba sunan , aslamu alaikum Ammi tace " daga cab ɓangaren akace wlkslm Ammi na gode da kikabar Afnan ta dawo batada lafiya , a zabure Ammi ta tashi daga zaman da tayi tace " aiko lafiya ta taho ni banma san musababin tahowarta ba , nima taƙi gayamin damuwarta amma ya kamata ke dakin matsa mata Ammi , mom Afnan kiyi haƙuri muma ɗazu muka dawo daga hospital son babu lafiya , innalilahi mom Afnan tace " maiya sameshi ? zazzaɓi wlh Ammi ta bata amsa , Allah ya ƙara lafiya mom Afnan tayiwa Ammi sukayi sallama.
bayan yayi isha'i ya dawo gida sbda bacci dake idonsa da alamu aluran da akayi masa basu gama sakesa ba , sallama yayi ganin Ammi a palo yace " Ammi yau da wuri zan kwanta bacci nakeji , tom Ammi tace " kasancewar likita yayi mata bayanin hakan ,kayi adu'a my son , insha Allah Khamis yace " ya nufi bedroom ɗinsa , sai da ya shiga toilet yai brush kana ya kwanta dan babu halin wanka bacci na idonsa .
Aisha da Ummi ne zaune bakin katifa suna shirin zuwa islamiya , wata baƙar leda Aisha ta karɓa a hanun Ummi tace " wlh yau sai malaminnan yayi dana sani , suka fito suna jiran yaya , bayan yaya ,ya fito ya samesu  fuskarsu cike da annuri ,to yaya yace " ayi dai karatu ba wasa ba , to sukace cikin haɗin baki , anty Fiddausi na ɗakinta tana sana 'ar tata wato bacci , ko sallama beyi mata ba ya fice dasu , suna shiga ya tada mota suka nufi islamiya ana suwa bakin get ɗin ya sau kesu tare da bawa kowacce nera hamsin yace " in suna son wani abun , godiya sukayi masa kana

suka shige ciki , hango malam Umar na taron latti kuma shine malamin su yasa Ummi cewa " wlh Aisha jeki hura masa nikuma zan kareki , da ƙwarin guwai wa Aisha taje dai dai saitin kunnensa ta hura masa cikin ikon Allah babu wanda ya ganta bare yai mata magana , suka wuce suna tafiyarsu kamar ba suba , koda suka shiga aji babu malam babu alamarsa Aisha ce ta leƙa ta window ta hango malam Umar yanata susa malamai sun taru a kansa ya sosa nan ya sosa can ,ganin duka ɗaliban makarantar na fitowa ganin abin da ke faruwa yasa su Aisha suma suka fito , wani uban ihu da malam Umar ya zabga kai kace anyi masa alura ,sai surutai yake ,yana cewa " kuzo mu cashe kuzo ƴan yara wayo bayana ku ɗibo ruwa kuyimin wanka , dama ya gama cire kayan jikinsa duka yana shirin cire gajeren wandonsa malaman sukayo kansa da gudu sun rasa musababin sashi hakan sun fara tunanin anya ba haukacewa yayi ba , tsalle yayi ya hau bishiyar mangwaron dake makarantar ga ƙaiƙayi kamar ana ƙara masa ,ganin abin baya baya yasa shi fara wurgo mutane da ɗanyun mangwaro yana ihu , wata malama ce tace " anya ba hauka malam Umar ya fara ba ? dauran malaman ma haka suke faɗa , gashi ya hau ƙololuwar reshe kaf cikin malaman babu mai iya sauko da shi , malaman ne suka kalli ɗaliban sukace akwai mai iya temakawa malam a cikinku ku sauko da shi , babu wanda ya ɗaga hannu sai Aisha , waro ido sukayi suna cewa " kece zaki iya ? eh Aisha tace " wani malami dake gefe yace " ku barta ta gwada basirarta , aiko suka barta ta hau bishiya tana zuwa saitin malam Umar ta karyo reshen itace ji kake timmm malam Umar ya faɗo , da sauri aka yo kansa ana yi masa sannu a zabure ya miƙe riƙe da kafaɗarsa yana kiran wayo zan mutu waiyo ƙaiƙayi susa yake kamar zai cire fatar jikinsa, sudai yau suna ganin ikon Allah wata malama na shirin yiwa Aisha faɗa malamin dake gefenta yace "ai ta fimu hikima kuma tayi ƙoƙari ,barta kawai malamar zatayi magana taji wani azababben ƙaiƙayi na shigarta da gudu ta yarda hand bag ɗinta tana gudu tana susa ta fice daga makarantar , inalilahi malaman suka shiga mai maitawa aka bi malama da gudu aka kamota aka sanyata a office suka kulle shima malam Umar da keta kewaye makarantar sun kasa kamashi badan haka ba kullesa za'ayi malam sai ihu take tana zage zage tare da cewa " kuzo kuyimin wanka da ruwa mai ɗan ɗumi ɗumi ko zan warware , babu wanda ya kulata sai ma kewaye makaranta da sukeyi gurin kamo malam umar abin ya citura , Aisha da Ummi suna haɗa ido sai su sakarwa da juna murmishi , daƙyar aka kamo malam Umar aka kulleshi a aji......!

Ina jiran comments

*MOM ISLAM*
[14/07, 8:21 am] Mom Islam Ce: *YARINYA MAI TAƁARGAZA*

*Zainab Habib [Mom Islam]*

*Wattpad @momislam2020*

*AREWA WRITER'S  ASSOCIATION*

*Page 48_49*

Bayan sati biyu , tunda aka sallamo sa daga asibiti bai kuma batun Aisha ba sai yau gudun kar ya ɓatawa Ammi rai duk da yasan tace " masa ta amince da maganar auran , cikin shiri ya fito yana sanye da farin boyel wanda ya fito da ainihin kyansa , durƙusawa yayi gaban Ammi yace " Ammi zani gurin Aisha ki tayani da adu'a ,insha Allah my son Ammi tace " cike da kulawa , jirani ina zuwa Ammi ta cewa " Khamis , samun guri yayi ya zauna yana jiran Ammin , fitowa tayi hanunta riƙe da wata farar leda mai ƙyali ta miƙa masa tace " wanan na my suruka ne , farinciki fal zuciyar Khamis yana ganin Amminsa zata kula masa da rainonsa , tom Ammi aiko zan kai mata ya fice yana shirin buɗe mota drivers suka fito , ɗaga musu hannu yai tare da cewa " ba nisa zanyi ba ya shige tsarariyar motarsa ƙirarar lexus ya harba titi tafiya yake cike da nishaɗi yana jin inama ɗauko ta zaiyi ta dawo gidansu ai da abin yafi armashi amma bazai yarda a jima ba'ayi biki ba , duk cikin zuciyarsa yake wanan batun , yana zuwa ƙofar gidan ya faka motarsa tare da ciro wayarsa ya danna number yaya Zakari , yaya Zakari dake bacci bai ma san ana kiran ba anty Fiddausi ce ta tashesa ta miƙa masa wayar , bai duba mai kiran nasa ba ya amsa , sallamar da yaji anyi ne ya tabbatar masa da mai kiran duba screen ɗin wayar yayi yaga sunan da yasa no. wlkslm yaya Zakari yace " ina yini ya iyali , lafiya yaya yace " yana jiran abinda zai kuma cewa " Aisha na gida ne ? bata nan yaya Zakari ya faɗa muryarsa babu yabo babu fallasa , nunfasawa Khamis yayi yasan dawan garin yace " to na gode ya ja motarsa ya dawo gida , yana shigowa ya tarar da Ammi zaune da jarida a hanunta , tana ganinsa ta miƙe tare da cewa " lafiya my son? murya kamar ta mai shirin kuka yace " Ammi wanan brothern nata ya hanani ganinta pls Ammina ki temakeni , da kallon tausayi Ammi ta bishi tasan wanan lamarin banda ƙaddara da ta riga fata ina Khamis ina Aisha anguwarsu ma abin kallo ce ga ɗanta kyakyawa yan mata na rubibinsa amma ya ɓige da yar ficika , janyo hanunsa tayi ta zaunar tare da cewa " come down my son kabi komai a hankali mai haƙuri zai ci riba ina lefin kabar yarinyar nan ta gama secondary in yaso sai kaji power zuwa gurinta , no Ammi dan Allah kice susa rana tunda sun amince , zaro ido Ammi tayi cike da tsoro take kallonsa ikon Allah Ammi ta faɗa a fili kai kuma kalar taka soyayyar kenan ? kwata kwata bakajin kunyata ?" rufe ido Khamis yayi yana cewa " my lovely Ammi ayimin afuwa bana sanin lokacin da nake surutan suka sa dariya dukkan su , Ammi wa zaki tura maganar tambayowa ? kawunka na  anguwar rimi mun fara waya dashi jiya , wow my Ammi kina sona , ya wuce bedroom ɗinsa cike da farinciki , sbda duk wanan ɓacin ran da ya dawo dashi ya goge , faɗa bed ɗinsa yayi kamar ƙaramin yaro ya fara tsalle harda rera waƙa , kin zamo farinciki na, masoyiya ke nake soo..lol.

Anty Fiddausi dake kan kujera a zaune ta sakko ta zauna kusa da yaya Zakari tace " my blood waye yake kiranka kwana biyu ? naji sai ka dinga cewa"batanan waye bata nan? miƙewa yayi daga kwanciyar da yayi , ya bata labari tundaga haɗuwarsa da Khamis har zuwanshi na yau, dan ƙari anty Fiddausi tace " Aisha yarinya ce ƙarama bugu da ƙari batasan halin rayuwa ba taya za'ace za'ayi maganar aure ? hmm Khamis yace " batare da ya ƙara kula zancen ta ba.

Washe gari ƙarfe 10:am kawun Khamis ya iso , Ammi ce tayi masa kwatancen anguwar ba tare da ɓata lokaci ba driver ya kaishi kasancewar ya bar motarsa a nan gidan , suna isowa anguwar ya tura yaro acewa mai gidan yayi baƙo , yaron ne ya fito tare da cewa" wai yana zuwa ,to kawu yace " ya jingina jikin mota , fitowar malam ce ta sashi faɗaɗa fara'arsa ya miƙawa malam hannu suka gaisa , nine wan mahaifiyar Khamis ,washe haƙora malam yayi kana yace " mu shiga daga ciki , malam na gaba kawu na baya suka shige , gidan shiru mama bata nan hakan yasa malam hamdala na zai zartar da hukunci cikin sauƙi  , bayan malam ya shimfiɗa tabarma suka sake gaisawa , kawu yace " maganar yara ce ta kawoni Khamis yaga Aisha yana so muna roƙon arziƙi da a yanke mana dukiyar aure bamason bikin yaja

lokaci , masha Allah malam yace " banason yi mata auran dole amma bari zuwa gobe shi yaron yazo suga juna zansa yau a kawota , to kawu yace " ya yiwa malam godiya tare da ajiye masa kuɗi masu yawa ya fice , kawu na fita malam ya tura kuɗin a aljihu ya nufi ɗakinsa , wayarsa ya ɗauka ya danno lambar yaya Zakari , da mamaki yaya Zakari ke kallon mai kiran yaushe rabon da malam ya kirasa Allah dai yasa lafiya ba jikin mama bane , gudun karta tsinke yasa shi kamawa tare da sallama , bayan malam ya amsa yace " maza ka kawo Aisha gida yau , gaban yaya Zakari ne ya yanke yana tunanin baya wuce wanan mai nacin kuma malam a ƙarfin halinsa sai yace " zai yiwa Aisha aure yanzu , malam suna makaranta fa , faɗa malam ya fara yana cewa " ni ban isa dakai ba kenan dahar zan gaya maka magana kayimin kunnen uwar shegu , zan kawota yaya Zakari ya faɗa , kashe wayar malam yayi ya fara zance shi ɗaya , zanga samu inga rashi fitinaniyar yarinyar ashe mai ƙashin arziƙi ce wlh bazanyi wasa da wanan damar ba muddun ina nunfashi, miƙewa yaya Zakari yayi ya nufi ɗakin su Aisha samunta yai zaune sun haɗa kayan wasa sunayi , da kallo ys buita na tausayi can yace " Aisha ɗauko hijabi kizo Ummi kema taho kuje gida inaga kwana zakuyi , Aisha ce ta kalli fuskar yaya Zakari tace " lafiya dai yaya ?" eh lafiya yace " mata ya juya ya nufi mota , suna shiga suka fara tsalle a dole zasu gida, cikin ƙan ƙanin lokaci sai gasu a ƙofar gidan su da sauri suka buɗe ko wacce tayi gidansu cike da murna , lokacin mama ta dawo , sallama Aisha tayi ta faɗa jikin mama tana cewa " mama ai nadawo kenan na gaji da zaman gidan yaya , dariya mama tayi tace "oh nikam mai ake yimiki ne bakida dama Aisha , ina malam Aisha tace " tana kallon ƙofar ɗakinsa , bayanan mama tace " koda na dawo ban samesa ba , taɓɓa barin leƙa Aisha ta miƙe ta nufi ɗakin malam, hangoshi tayi zaune kan tabarma yayi nisa da ƙirga kuɗi baima san tana tsaye ba , a hankali Aisha ta koma ta kirawo mama , mama bata ɗauka wani abin bane ta biyo Aisha suka leƙa ɗakin , ɗago kan da malam zaiyi sukayi ido biyu , na shiga uku malam yace " yana kallon Aisha hanyarki da sheda inkikazo sai kin ɓatamin rai banda dole mezai sa in sa azo dake , kekuma ya nuna mama , meya kawoki ? taɓe baki mama tayi ta juya batare da ta bashi amsa ba, dariya Aisha tayi tace " aheeee malam ka fiya son kuɗi inka mutu ɗakinnan zan shiga inyita kuka kambun uba wlh yarinyar nan kin rai nani babu abinda zai hana banyi miki aure watan gobe ba , dariya Aisha ta kuma sawa tace " wlh da naji daɗi , ware ido malam yayi daganan yaja baki yai shiru gudun kar bakin nasa yaja masa matsala , mama dai na jinsu bata maida zancen nasu gaske ba , ta fara haɗa wuta sbda ɗora abincin dare,

ƙin shiga gidan yaya Zakari yayi ya juya zuwa gareji , yana tafiya sai ga motar Khamis tayi parking Allah baisa zasu haɗu ba , amma Khamis ɗin ya gansa , yaro ya aika yace " masa kace ana sallama da Aisha ,sai da yaron yasa dariya kana ya shige cikin gidan ya faɗi aikan , malam dake ɗaki yace " kace tana zuwa , mama zatayi magana malam ya dakatar da ita yace " babu ruwanki irinku ne masu toshe hanyar alkairi maza Aisha fito kinyi saurayi , da gudu Aisha ta fito tare da rufe fuska tana dariya tana tsalle a dole ta girma , maza kije Khamis ne yazo ina jiranki zamuyi magana , a'a malam ya za ayi ka tura yarinya kamar Aisha gurin mai mota ? duniyar nan fa ba abin yarda bace , to malama kicigaba da yimin wa'azi shine fa mijin da zai aureta banison shishigi da baƙin ciki , saboda kinga kaf zuri 'arku bakuda attajirai shine Allah ya kawo mana har gida kike neman gurguɗewa maza Aisha ta jeki Allah ya dawo min dake lafiya, a guje Aisha ta fice ta nufi waje ganinshi da ita sau ɗaya amma zai iya ganeta , Aisha Khamis ya ƙwala mata kira , turo bakinta na tsiwa tayi tace " dallah malam kaine me kirana ? eh Khamis yace " yana murmishi , shigo man yace " mata tare da buɗe murfin mota , yasin bazan shiga ba kalan ace min ƴar iska kome zaka faɗa ka faɗa ni banason gulma , zaro ido Khamis yayi yana mamakin surutu irinna Aisha , to my Aisha ina sonki kina sona ? Khamis ya faɗa tare da ƙara sakar mata murmishi , tsayawa kallonsa tayi sai yanzu ta tuno inda ta gansa , oh ashe kaine wanan baturen kai gaskiya kanada kyau sosai , daɗi ne ya kama Khamis ya shafa sajensa yana jin ƙaunar Aisha na shigarsa, Ammi na tace " in gaishe ki , ina amsawa Aisha tace " tana kallon fuskarta ta mudubin motarsa ,baki bani amsa ba

Aisha na , wlhi ina sonka sosai ma tahau tsalle kaine na shirin fim ɗin da muka kalla jiya ka iya tsalle kana ta kaiwa wasu naushi tana shirin naushinsa ya kauce tare da sa dariya , ga chocolate Ammi tace " in kawo miki , da dariya Aisha ta karɓa tace " na gode rabona da inci tun sallah da mukaje muka samo kuɗi yaya ya karɓe ya siyo mana , dan Allah kace ina gaisheta sosai zanzo gidanku amma inhar zata yimin wainar fulawa da ɗanta malele, dariya yasa yace " meye wanan ? ni banma san sunansa ba amma naga Afnan na yin wainar fulawa , aiko na fasa zuwa Aisha tace " tana tafa hannu , gyara riƙon ledar tayi tace " ka tafi gidanku inma jira kake in baka baza kaci ba , ta faɗa tana hararar sa shiko dariya ma ta basa ya dinga ƙyalƙyalewa ,Allah na ganoka irinku yan sa rani ne Aisha ta faɗa tare da shigewa gida da gudu tayi masa gwalo,
shikam wanan nishaɗin da Aisha ta sanya shi yau zaiyi bacci mai daɗi tare da mafarkinta , ya daɗe a tsaye daga ƙarshe ya tada mota ya bar anguwar , driving yake cike da nishaɗi , yana isa gida yai horn mai gadi ya buɗe tare da ɗaga masa hannu , miƙawa mai gadi 1k yayi cikin rawar jiki mai gadi ya durƙusa yana yi masa godiya , batare da ya kulasa ba ya nufi ciki yana jefa keys ɗin hanunsa yana cafewa, da sallama ya shiga palon yana cewa " my Ammi am very happy suruka ta amince Ammi na kina ina ya hau dube dube.....!

*godiya nake masu comments karkuga bana kulaku ina ganin irin soyayyar da kuke nunamin iya wuya ana tare*

*MOM ISLAM*
[14/07, 8:21 am] Mom Islam Ce: *YARINYA MAI TAƁARGAZA*

*Zainab Habib [Mom Islam]*

*Wattpad @momislam2020*

*AREWA WRITER'S ASSOCIATION*

*Page 50 _51*

Da sauri Ammi ta fito fuska cike da fara'a tace " masha Allah yarona yayi farinjini kai amma fa naji daɗi , kace sai maganar sadaki da sa rana , tsalle Khamis ya buga yana rawa da gudu ya ruga ɗaki yana cewa Ammi am so sorry nayi rawa a gaban ki , murmishi Ammi tayi sbda farincikin ɗanta shine burinta , koda kawu yazo gidan su Khamis ya faɗawa Ammi abinda malam yace " Ammi ce tace " ai yanzu ma ya dawo bai daɗe da fita ba ka shigo sun dai daita , ok tom masha Allah kawu yace " sintiri fa ya gammu dole mu zage yanzu gidan zan kuma komawa , godiya Ammi tayi masa ya fice , kai tsaye gidan su Aisha kawu ya koma , sawa yayi yaro yayi masa sallama da malam fitowa yaron yayi yace " wai ga shinan , malam na fitowa ya hau washe baki yace " wa kawu ya shiga , kawu na shiga sai ga baban Ummi nan ya shigo nan aka gaisa , malam ya kira Aisha cikin zumuɗi tazo ta zauna tana wasa da ledar dake

hanunta , kallonta baban Ummi yayi yace " kina son Khamis ?" juyawa tayi ta kalli mama , mama da batasan Aishar na kallonta ba.
Tambayarki muke kinyi shiru , eh Aisha tace " idanunta a na baban Ummi , mamaki da tsoro ya cika zuciyar baban Ummi amma babu halin magana tunda iya abinda ya kawosa shi zaiyi ba shida ta cewa " sbda tsoron azabar faɗan malam , ganin Aisha yasa kawu zaro ido cikin ransa yace " dama wanan ɗan nawa yake so innalilahi wanan wace irin jaraba ce ?" bai bari zancen ya fito fili ba ya ce " to yanzu maganar dukiyar Aure fa , baban Ummi ne yace " kubada dubu ɗari ,badan malam yaso haka ba ,a nashi inda shine dubu ɗari biyar zai ce gaskiya an kwafsa masa , ya haɗe rai , kawu ne ya dire kuɗin a gurin sai da aka ƙirga dubu ɗari huɗu ne sukayi wa Allah godiya nan fa malam yaɗan fara murmishi , kasancewar Aisha ta wuce ɗaki yasa kawu cewa " munason asa rana dan Allah bamson akai da nisa , to to malam yace " kana ya kalli baban Ummi ka gaya masa man ,malam yace " baki na rawa a'a malam baban Ummi yace " abi komai a hankali zuwa ƙarshen wanan watan a sa ranar kafinnan yan uwa sun hallara , tunda bazakayi magana ba ni inada bakin magana innasa yan uwan zasu canza ne ?" malam ya tambayi baban Ummi , shiru baban Ummi yayi dama yasan kafin a tashi dole sai sunyi faɗa sbda malam akwai ƙin shawara ,ansa biki wata biyu masu zuwa malam ya faɗa ranshi fess , masha Allah kawu yace " ya miƙe yana jaddada godiya a garesu yai musu sallama , kawu na tafiya baban Ummi ya miƙawa malam kuɗi tare da yi masa Allah ya sanya albarka , amin malam yace " tare da godiya ya tattara kuɗi ya miƙe , ficewa baban Ummi yayi zuciyarsa babu daɗi, yana shiga gida ya samu maman Ummi zaune a tsakar gida tana tsinke alaiyyahu , sallama yai ta amsa ɗago kan da zatayi taga fuskar tasa kamar ta mai shirin yin kuka , lafiya baban Ummi na ganka haka ? inafa lafiya ankawo sadakin Aisha.zaro ido maman Ummi tayi tace " sadaki fa kace wanan Aisha tamu? eh itafa caɓ amma babu wanda yafi ganganci fiye da malam , hmm baban Ummi ya nisa kana yace " banda yaga ruwan kuɗi wanan ai bai dace ba sam , to Allah ya kyauta aikin gama ya riga ya gama tunda gashi har ansa rana , mamaki da tausayin yarinyar duk yabi ya kama maman Ummi ba komai take dubawa ba sai ƙanƙantar shekaru Allah ya tabbatar da alkairu maman Ummi tace " cikin sanyin jiki .
Leƙa ɗakin mama malam yayi ya samu tana kuka iyeee yar baƙinciki kukan me kike arziƙi yazo mana har gida kuma nasan zakifini morarsa tunda tafi sonki , Aisha da keta jijiga mama tana jin kalamin malam ta kallesa tace " wlh zance na fasa tunda abin haka ne , ubanki nace " dan gidanku ko nine nace an fasa ai nayi ƙaranta wlh ko da wasa ,share hawaye mama tayi tace " a gaskiya malam baka kyauta min ba , baka duba nima inada haƙƙi a kanta ba ka zartar da hukunci amma sai naga kamar ana shawara kafin haka , ungo dubu ashirin kisi wasu abubuwan nikuma zanji da kayan gado da katifa da kujeru , babu inda mama ta iya haka ta karɓi wanan kuɗi zuciyarta na tafar fasa inalillahi take mai maitawa ,ganin mama taƙi dena kuka yasa Aisha sakin kuka tace " mama in bakiso nima baniso kidena kuka kinji , babu komai Aisha Allah yayi shine mijinki karki damu duk abinda Allah ya ƙaddara babu makawa sai ya faru , ta rungume Aisha . shidai malam da ya gama surutunsa ya fice dan tunda mama ta gama faɗa masa lefinsa ta barshi tsaye kamar gunki.
Washe gari 8:am kawu ya iso gidan Ammi , Ammi na ganinsa tace " oh yaya munsaka ɗawainiya , murmishi kawu yayi yace " ai yiwa kaine karki damu , kinsan jiya naje gidan su yarinyar da Khamis yake nema ,mun gama magana na bada sadaki anma yanke ranar wata biyu , farinciki fal zuciyar Ammi ta dinga yiwa kawu godiya tare da yi masa fatan alkairi , hirar su ta yan uwa suka shiga yi bashi yabar gidan ba sai sha biyu bayan an zubo masa abinci yaci.
Anty Fiddausi ce a kan cinyar yaya Zakari tana zuba masa shagwaɓa amma sam hankalinsa baya gurinta , lura da hakan da tayi ne ta sa masa kuka tare da cewa " kwana biyu baka kula da ni shiyasa nace banison ciki amma kaƙi yarda da magana ta ,yasan duk rigima ce takeso da shi shikam a halin yanzu hankalinsa yayi gida yanaji a jikinsa mama bata cikin kwanciyar hankali , kiyi haƙuri Fiddy ba haka bane

banajin daɗi ne, ina iya bakin ƙoƙari na gurin ganin na sakaki farin ciki kiyimin uzuri zani gida dubo mama yanzu zan dawo, ruƙosa tayi tana cewa " haba mijina nikam banison kayi nisa dani , afuwan insha Allah yanzu zan dawo yaya Zakari ya faɗa tare da haɗe hannayensa , to Allah ya tsare anty Fiddausi ta faɗa cikin murya mai shirin kuka , amen yaya yace " kana ya fice bai tsaya ɗaukar motarsa ba ya hau mashin ya gaya masa anguwar da zai kaisa , kasancewar anguwar batada nisa cikin lokaci ƙanƙani suka iso , kuɗi ya ciro yaba mai mashin ɗin ya shige gidan nasu da sauri , ganin mama da maman Ummi a zaune yasa shi durƙusawa ya gaishe su , amsawa sukayi cike da kulawa maman Ummi ta miƙe tana cewa " mama Allah ya rufa asiri , amen mama tace " ta kalli fuskar yaya Zakari , lafiya dai na ganka kamar baka cikin nutsuwarka ? lafiya mama meke faruwa a gidannan? me ka gani ? cewar mama gabana nata faɗuwa tun ɗazu any kuwa lafiya ?" uhm mama tace " lafiyar kenan ashe kaima mahaifinnaka baiyi shawara da kai ba , shawarar me kuma mama ?" yaya Zakari ya faɗa , gyara zama mama tayi tace " ka nemi guri ka zauna da sauri ya ja kujera yar tsuguno ya zauna yana kallon mama , ansa ranar auran Aisha ,a fusace yaya Zakari yace " aure kuma ? wanan wace irin rayuwa ce ? wlh nasan hakan zata faru menene riba a aurar da Aisha ? sekace mun gaji da ita ?" babu neman shawara haka ya yanke hukunci itama ai Aishar duk da ita ɗazu fa da mai bin maganar auran yazo aka tambayeta cewa " tayi tana sonsa , tsaki yaya Zakari yaja kana yace " mama Aisha guda nawa take batasan komai akan so ko ƙi ba gaskiya ba'ayi mata adalci ba,
uban adalci ne ba'ayi mata ba kanada hankali kuwa ?" har zan faɗi magana ku zauna kai da uwarka kuna neman warwarewa to wlh baku isa ba sbda nayi istahara auransu alkairi ne dan haka babu makawa sai anyi aurannan ,malam ya faɗa yana shirin shigowa , buɗe baki yaya Zakari yayi zai yi magana mama tayi masa alamar yai shiru , miƙewa yayi idanunsa na fitar da ƙwallah yace " mama zan tafi sai gobe cikin rashin jin daɗin yanayin da yake ciki mama tace" ka kwantar da hankalinka insha Allah komai yai tsanani maganinsa Allah adu'a zamuci gaba da yi mata ,tom kawi yaya yace " dan magana ma bazata yiwu ba ya fice , ya daɗe a kofar gidan zaune yana riƙe da kai ya rasa meke yi masa daɗi ina zaisa kansa , ciwon kan da yaji ne yasa shi runtse idonsa ya miƙe tare da shiga gidansu Ummi yace " ta fito su tafi maman Ummi dake kitchen tana girki tace " yau baza'a da Aishan bane?eh banma ganta a gidan ba , da sauri Ummi ta janyo hijab ɗinta a jikin igiya ta riƙo hannun yaya suka fito ƙofar gida ya tari mashin , suna isa anguwar suka sauka tare da bawa mai mashin kuɗinsa suka shige gida , da shigarsa ya samu anty Fiddausi na kitchen tana soya doya da ƙwai Fidy zo man Ummi jeki karɓa mata aikin , to anty Fiddausi tace " ta miƙe da ɗan cikinta da zai kai wata uku ta nufi ɗaki , da shigarta ta gansa zaune ya haɗa kai da guwaiwa hawaye na zuba a fuskarsa , salati ta fara mekuma ya faru ?"anty Fiddausi ta faɗa tana shirin tayasa kukan , wai Aisha ce za'ayiwa aure nanda wata biyu wanan wane irin hukunci ne ? aure kuma ? dai dai kaji kuwa ?"anty Fiddausi ta faɗa tana zaro ido , eh man shiyasa tun safe nake jina babu lafiya amma wanan yaron shima ba ƙaramin sakarai bane , ubanme zaiyi mata inhar ya aureta anya malam yayi tunani kuwa ?jinjina kai anty Fiddausi tayi tace " tunda anriga an yanke hukunci sai dai mu tayata da adu'a .
Tunda Khamis yaji wanan kyakyawan albishir ɗin yake ta zumuɗi kaf abokansa ya basu labarin auransa sunma koma ce masa na Aisha.
Kasuwa Ammi ta tafi ta siyo akwatuna masu tsada daga ganinsu ma zaka sheda hakan ga wasu kaya da taje jida harda su breziya tofa , atamfofi kam babu na ƙaramin kuɗi kashe kuɗi Ammi takeyi kamar bata san zafinsu ba , ga kayan makeup data haɗa a babban akwati akwatunan zasukai kala goma sha biyu , duk da haka ma bata gama siyan kayan ba .
Niƙi niƙi suka dawo da kaya cikin both haka drivers da masu gadi suka dinga shiga da kaya , Khamis da yayi shirin zuwa anguwa jin motsin shigowar Ammi yasa shi dakatawa oyoyo my Ammi ya faɗa lokacin da ta ƙarasa shigowa, da dariyarta tace " ango ango dariya masu shigoda kayan sukayi tare da cewa" Allah ya sanya alkairi ,

amen Ammj tace "suka koma bakin aikinsu , zoka gani ba'a gama siyayyar ba ma , inason momyn Afnan tazo gobe muga abinda babu , zama Khamis yayi yana ƙarewa kayan kallo cikin farinciki yace " Ammi baza'a ƙaro akwatunan ba kuwa ? no a barshi haka amma dai a ƙara yawan kayan Ammi ta faɗa tana murmishi......!

Masu yimin magana ta PC karku ɗauka wulaƙanci ne pls adinga yiwa juna uzuri some times post da typing nake kawai afuwan .

*MOM ISLAM*

[19/07, 3:29 pm] Mom Islam Ce: *YARINYA MAI TAƁARGAZA*

*Zainab Habib (Mom Islam)*

*Wattpad @momislam2020*

*AREWA WRITER'S ASSOCIATION*

*Page 52-53*

Harma ya hango ranar auran su kasancewar in zaiyi misali yana ajiye Aisha a matsayin babbar mace , Ammi ni zan fita  Khamis ya faɗa, to a dawo lpy my son , Ammi taci gaba da duduba kayan sbda taga abinda babu .
Washe gari tun safe Afnan da momynta suka iso kana ganin fuskar Afnan kasan bata cikin kwanciyar hankali ,a palo suka yada zango yar aikin gidan ta cika gaban su da kayan  ciye ciye , fitowa Ammi tayi cike da farinciki ta dubi momyn Afnan tace " munata shirye shirye ,dariya momyn Afnan tasa tana cewa" munada bidiri ai zuciyar Afnan kamar an buga mata guduma tsabar baƙinciki da tasan wanan maganar zata zo ta tarar da batayi gigin zuwa gidan ba , amma tunda ta faɗa wa momynta dalilin dawowarta gida babu damuwa komai zai dai daita amma tasan akwai ƙura a gaba sbda koda sau ɗaya Khamis bai taɓa nuna alamun kulawa da ita ba .janyo akwatunan momyn Afnan tayi ta fara duddu ba kayan kasancewar Ammi tabar gurin yasa Afnan matsowa tace " wlh momy wanan kayan ba ƙaramin kashe kuɗi sukayi ba ,hmm momyn Afnan ta nisa tare da cije leɓe tace " wanan uban kaya kamar wacce ta fito daga gidan wani hamshaƙi? indai ko ina nunfashi sai kin auri Khamis wlh wanan alƙawari ne na ɗauka . farinciki na ya baiyyana a fuskar Afnan ,jin motsin tahowar Ammi yasa su yin shiru sukaci gaba da duba kayan ,Ammi na isowa momyn Afnan tace " oh my sister kinyi aiki fa Allah ya sanya alkhairi amen Ammi tace " kana ta nemi guri ta zauna sukaci gaba da tattauna abinda zai wakana.
Washe gari da yamma Khamis ya shirya zuwa gurin Aisha wani lallausan yadi ya sanya mai tsadar gaske wanda ya fito da ainihin kyansa gashin kannan yasha gyara hannayesa suna ɗauke da tsadaddun zobuna wa inda suka ƙara ƙawata kyansa fitowa palo yayi yana ƙwalawa Ammi kira , da sauri Ammi ta fito tana washe baki tace " kai my son karfa kasa Aisha tace " da wancan da wanan akwai ban banci suka kwashe da dariya , Ammi sai ma ranar da na kai mata chocolate kinga murna harda

rawa cemin take wai balarabe , dariya Ammi ta ƙara sawa tace " ai kana kama dasu shiyasa , to Ammi ayi min adu'a zan tafi hira ,ya rufe fuskarsa , cike da kulawa Ammi ta dubesa tace " my son Allah ya tsaremun kai a duk inda kake. amen Ammi Khamis ya faɗa kana wuce, kai tsaye parking spice ya nufa ya ɗauki motarsa ya fice yana jin wani farinciki , driving yake yana murmushi shi kaɗai yasan inda yake ji a ransa , yana isowa unguwar yai parking a ƙofar gidan su , yaro ya hango da bazai wuce sa'anta ba ya aikesa ya kira masa Aisha , bayan yaron ya shiga bai kai ga cewa " komai ba sai gata ta fito da uban gudu ta rungumeshi , dariya yaron yasa yace " Aisha wanan ɗan uwanku ne? dariya Aisha tasa tace " kai wanan saurayi na ne baka ganshi kamar balarabe ba ,shidai Khamis na tsaye yana jin hirarsu hanunsa a na Aisha gyaɗa kai yaron yayi tare da cewa " kinji daɗi natafi aikana ya wuce " da gudu , ko ka goyani kokuma in koma gida wlh ,Aisha ta faɗa tana cuno baki , murmishi Khamis yayi da har dimple ɗinsa ya loɓa yace " my Esha zan goyaki amma ba yanzu ba ko kinaso mutane suyi miki dariya? girgiza kai tayi tace " to ina tsaraba ta , bugar goshinsa yayi da tafin hanunsa alamar mantuwa ya dai daita nutsuwarsa da cewa" zan siyo miki amma gaya min me kikafi so , alewa da chocolate da tuwon madara ,Aisha ta faɗa tana tsalle ,tsayawa kallonta yayi yasan she is very young amma a hakan yake da buƙatarta , tana ta surutanta bai kulata ba dan bai san tanayi ba , taɓosa tayi tana cewa " balarabe ciromin waccan yar bebin ta cikin motarka , sai a lokacin yaji abinda take cewa" taɓɓ Khamis ya faɗa a cikin ransa , me zakiyi da ita? wasa harda goyo kuma in ɗinka mata kaya , dariya Aisha ta basa dan har ga Allah tana sashi nishaɗi , leƙawa ta cikin motar yayi ya ciro mata babyn ya miƙa mata ,tsalle ta doka tace " kai balarabe ina sonka sosai ta rungume babyn , wani daɗi ne ya kama Khamis a dole kalmar so ta fito daga bakin masoyiya, rugawa gida tayi da gudu ta leƙo tace " balarabe in zaka sake zuwa ka taho min da kayan yar bebi dan Allah ta ƙara da gudu , ya daɗe a gurin yana dariya daga ƙarshe ya tada motarsa ya bar anguwar.
Tunda Ummi ta koma gidan yaya Zakari kewar Aisha ke damunta shiko yayan kwata kwata Aisha ta fice masa daga ransa.
Yunwar da ta addabeta ne yasa ta fita kitchen dan bataci abincin dare ba , ƙwai ta fasa har guda goma ta tsiyayo mai da maggi da albasa ta hau suya , lokacin yaya Zakari da anty Fiddausi na zaune tana kukan amai ya dameta , jiyo ƙamshin suyar ƙwai yasa ta tashi daga zaman da take tace " itafa ƙwai zataci kuma soyayye, ya fara jin bacci ya fito ya nufo kitchen ɗin jin kitchen ɗin ya gaure da ƙamshi kuma na ƙwai yasa shi dube dube kuma gashi risho da zafi , bai gama shan mamaki ba har sai da yaga babu ƙwai ko guda ɗaya alhalin yasan jiya da ragowar guda goma , a hanzarce ya dawo ɗakin anty Fiddausi haskata yai da fitilar wayarsa kasancewar yanzu suka ɗauke yace " naga babu ƙwai fa ina aka kai ?" wlh ban sani ba nikam, ni da nake ɗaki kwance ko fitowa banyi ba , mamaki ne ya kuma kama yaya yai ƙwafa yace " koma dai menene wataran Allah zai haɗani da mai satar nan .
Ummi na ɗaki zaune ta sa tiren ƙwai tana ci tana gyɗa kai daga ɗakin tana jiyo surutun su yaya amma tayi burus , sai da ta cika cikinta fam sanan ta tura ragowar gefen jakarta , goge hanunta tayi da zanin gado ta haye ranta fesss bacci mai nauyi yai awon gaba da ita.
Washe gari Ummi sai fama da tusa take da ta zauna zataji tusa ,suna zaune da anty Fiddausi taji wani uban wari ,toshe hanci anty Fiddausi tayi tace" haba Ummi kamar kinci ƙwai? wuli wuli da ido Ummi ta shiga yi tana shirin tashi ankara da alamun rashin gaskiya yasa anty Fiddausi lura da ita , zo nan anty Fiddausi ta ƙwala mata kira , ƙin zuwa tayi ta ɗauki buta tare da shigewa bayi , tana shirin yin fitsari taji gudawa ta taho , zaro ido Ummi tayi tana cewa" na shiga uku wlh na mance ƙwai na sani gudawa , kuka ta fara a bayn gida tare da cewa" yanzu wazai siyamin maganin kashi ?" haka ta miƙe ta jiƙe da zufa tayo waje ,anty Fiddausi dake zaune bata tashi daga inda take ba ta daka wa Ummi tsawa , a firgice Ummi ta saki tusa tana jin gudawa na shirin zubo mata tayi bayi da gudu tana kuka , dariya ma abin

yaso bawa anty Fiddausi hakan sai ya tuno mata da nasu kashin da sukayi , ganin shiru shiru Ummi bata fito ba yasa anty Fiddausi miƙewa ta nufi ɗaki ta kwanta .
Washe gari .
Zaune Aisha take ta haɗa kayan wasanta da ƙyallaye tana yankawa da reza , mama dake zaune kusa da ita ta girgiza kai dan tana tausayin Aisha kasancewarta yarinya ƙarama , lafiya mama kike kallo na ?" Aisha ta faɗa tana yiwa ƴar bebinta rawa , lafiya Aisha mama tace " kana ta miƙe hawaye na zuba a fuskarta ta nufi ɗaki.
Aisha taga kukan da mama ta keyi bata bita ba ta cigaba da zama har shigowar malam , kasancewar yanzu malam basa faɗa da Aisha , yawwa malam ga mama can a ɗaki tana kuka na tambayeta tace " wai tsire takeson ci , Aisha ta faɗa tana jujuya ƴar bebi , zaro ido malam yayi kana yace " tsire ko to inma sawa kuɗina ido takeyi tun wuri ta fasa dan wlh ba kuɗin banza gareni ba , dariya Aisha tasa tace " malam wasa fa nake maka , kinci gidan ku malm ya watsa wa Aisha daƙuwa , turo baki Aisha tayi tace " amma fasa auran bazan aureshin ba ta murguɗa baki , tsugunawa malam yayi cikin muryar lallashi yace " habba Aisha na karki ƙara faɗar hakan banaso zomuje in siya miki tsire kici , da sauri Aisha ta miƙe ta nufi gurin malam ya riƙe mata hannu suka fice , da fitarsu waje wasu tsofaffi suka fara gulmar su malam suna cewa " wlh auran jari zeyi mata dubi ƴar yarinyar da zai aurar taɓ ,karab a kunnen malam amma burinsa kar Aisha taji duk da ba lallai tasan ko me suke nufi ba , haka dai suka wuce zuciyar malam babu daɗi  ya nufi gurin mai tsire , Aisha ta mance da sun taɓa zuwa satar tsire ita da Ummi, gaisawa malam sukayi da Lawali bayan ya amsa yace " malam kazo  siyan tsire ne ?" eh malam yace " na ɗari biyar zaka bani jikin lawali na rawa ya fara zuge tsire ,hango Aisha da yayi ne yasa shi tsayawa yana nazarin kamar itace tayi masa sata ita da wata yarinya , tabbas ita ce lawali ya faɗa a fili , sarai Aisha ta gano komai amma batada damuwa tunda akwai malam , malam wanan ɗiyarka ce ?" Lawali ya tambaya eh malam yace "yana washe baki masha Allah Lawali ya faɗa yana yiwa Aisha kallon inna riƙeƙi zakisha wuya, bayan Lawali ya gama sawa malam ya miƙa masa , kuɗin malam ya basa kana suka wuce , suna isowa gida malam yaba Aisha leda ɗaya yace " ƴar albarka kici ki ƙoshi ki samma mamanki ɗan kaɗan , maƙe kafaɗa Aisha tayi tace " nidai ni kaɗai zanci ka bani in kai mata a naka ai inaji kace wa Lawali ya  sa naka da yawa , zaro ido malam yayi yace " duk wanda ya aureki wlh ya aurarwa kansa sai kuma yai shiru , mama da ta fito domin ɗora girki ta gansu da leda a hannu , ko saurarar su batayi ba tunda Aisha yanzu ba jin maganarta takeyi ba , ko yazo bazan fita ba yasin Aisha ta faɗa tana cuno baki , ganin abin zaiyi masa yawa yasa malam shigewa ɗaki yabar Aisha a gurin.
Ummi ta gala baita bata ma iya fitowa wunin ranar yaya Zakari a gida yayi shi kasancewar baya  jin daɗi sosai  , lura da rashin jin motsin Ummi yasa ya leƙa ɗakin nasu , ganinta yayi kwance rufe da bargo sai rawar sanyi take ga wani uban wari da yayi masa sallama , innalilahi Ummi Ummi ....ya kira sunan ta da ƙarfi , shiru bata amsa yasa shi shafa fuskarta jikinta yayi sanyi ga wani irin nunfashi da take fitarwa da sauri ya fice ya nufi shagon siyarda magani na nan anguwar tasu ya kira mai chemist ɗin , tare suka taho cikin sauri suna shiga ba'a tsaya ɓata lokaci ba aka sanya mata drip, bayan yasa magunguna a ciki yayi wa yaya Zakari sallama yace " in ya ƙare ka kira number ta , to yaya Zakari yace " jiki a sanyaye , fitowa anty Fiddausi tayi ta nufo ɗakin ranta a ɓace babu ko sallama ta bankaɗo labule tana ƙarewa yaya Zakari da Ummi kallo , cikin masifa tace " andai ji kunya ka rasa wacce zaka so sai ƴar cikinka , da mamaki yayan ke kallonta dan da farko bai fahimci me take nufi ba amma yanzu kam ta fahimta , ki nutsu Fiddausi , bazan nitsu ba kazo ka ɗorata a cinya kamar wata matarka koni ynzu baka yimin haka , anty Fiddausi ta faɗa tana riƙe da ƙugu , dariya ma taso bashi banda hauka da yarinya ƴar shekara goma sha ɗaya za'ayi kishi aiko sai da ya dara ya kwntar da Ummi yaja hanun anty Fiddausi sukayi waje , kai tsaye ɗakinsa ya nufa da ita ya zaunar da ita kan katifarsa , kina nufin son Ummi nake ko me ?" idanun anty Fiddausi na fitar da hawaye tace " eh man inba so ba ai naga ko shiga ɗakinsu bakayi , shitttt....ki fahimceni badan

larurarki ba babu abinda zai sa na ɗauko Ummi tausayinki da nake ji yasa hakan me zanyi da Ummi ? ki kiyaye bana son jin wanan zancen ya ƙara fitowa daga bakinki , kingane ko ?" gallah masa harara tayi ta fice tana magana ciki ciki.....!
[23/07, 8:50 pm] Mom Islam Ce: *YARINYA MAI TAƁARGAZA*

*SUBSCRIBE*
_DUNIYAR LITTAFAN HAUSA TV_

https://www.youtube.com/channel/UCcAjVQ74qod9_dL0e_AqkiQ

*Zainab Habib (Mom Islam)*

*Wattpad @momislam2020*

*AREWA WRITER'S ASSOCIATION*

BOOK 1

*Page 54 -55*

bayan ruwan da aka sa mata ya ƙare sai da aka kuma sa mata wani dan ta galabaita sosai , zuwa ƙarfe takwas aka cire .bayan yaje ya biya kuɗin ƙarin ruwan ya dawo kitchen ya ɗibi ruwan zafi ya koma ɗakinsu ya ɗauki lipton da madara da suga ya haɗa mata shayi mai kauri ya nufi gurin ta , samunta yayi tana zaune ta rame sosai miƙa mata yaya Zakari yayi tare da cewa " maza ki shanye , idanunta sun ciko da hawaye tace " yaya bazan iya sha ba dan Allah ka ajiye , ɓata rai yayi tare da daka tsawa yace " kina tunanin yunwa ba ciwo bace ?" ko ita ma zata haddasa miki rashin ƙarfin jiki , maza kisha .kuka ta fara wiwi kamar wacce aka doka , ganin faɗan baze yi ba yasa shi matsowa ya fara bata da cokalin cikin cup ɗin , eyeee abu ya tabbata wlh Allah nidai bazan yarda ba tunda kaga za'a aurar da Aisha kake shishigewa wanan ƙwailar to na rantse da Allah baka isa ba , anty Fiddausi ta faɗa tana riƙe da ƙugu tana masifa , mtsw yaya Zakari yaja tsaki yaci gaba da bawa Ummi tea ko kallon inda take beyi ba, kuka anty Fiddausi ta fashe da shi tare da ficewa ta nufi ɗakinta da gudu , Ummi dake kwance bata fahimci abinda ke faruwa ba ita dai kallon yayan take kawai.
mama ta fara siyayyar kayan amfani su malam babu sanya har an kawo kayan gado , farinciki fal zuciyar Aisha itama zata fara kwanciya a babban gado . da yamma misalin ƙarfe biyar Khamis yazo yana sanye da farar shadda wacce ta haska kyansa , tsaye yake jikin mota yana karkaɗa keys ɗin motarshi ,yaro ya gani zai shiga gidan su Aisha ya tareshi tare da cewa" dan Allah kace Aisha tazo , to yaron yace " kana ya nufi ciki da gudu ,yaron na shiga ya sameta zaune ita da mama malam na gefe yana rubutu a allo , Aisha wai kizo inji wani yana tsaye jikin mota , maƙe kafaɗa Aisha tayi tace " kace bazan zoba , yaron zai fice isar da saƙon malam ya tsayar dashi yace " kace tana zuwa ,to yaron yace " ya fito daga gidan ya isarwa da Khamis aikan , maza ki tashi kiɗan bar baɗa hoda man Aisha na malam ya faɗa yana karya murya ,

wlh bazani ba shi yace " zai tahomin da wanan abin daɗin da mamansa ta bashi ya kawo min kwanaki amma yaƙi , oh Aisha rigima banda abinki kika sani ko ya kawo maza ɗauki hijabi ki gaishe shi , dariya mama tasa tana mamakin son duniya irinna malam , da sauri Aisha ta shige ɗakin mama ta ɗauki hijab ɗinta ta fito tana tafe tana waƙa ta iso gurin Khamis da ya gaji da jiranta ya shiga mota ya zauna , ƙwanƙwasa glass ɗin motar ta fara tana cewa" kyakyawa ka fito man , sarai ya jita yasa dariya ya buɗe murfin motar kana ya fito hanunsa riƙe da farar leda zatayi magana ya kamo hanunta ya damƙa mata ,dariya tasa tace " Allah ya soka al kur'an da zance bana sonka , murmishi Khamis yayi dan shi komai nata birgeshi yake , to zan koma gida yarinyata na kuka cewar Aisha , zaro ido yaya Khamis yayi yace" yarinyarki kuma kina da yarinya ne ? cewar Khamis , eh man ka mance wacce ka bani ?" oh na tuna Khamis ya faɗa yana dariya , Ammina tana gaisheki tace " inyi miki photo , meye kuma photo kace hoto sai ka tsaya kana yiwa mutane kwainane , Aisha ta faɗa cike da tsiwa , am sorry my Esha yaushe za 'ayi hoton , gobe in kazo ni wlh na gaji gida zani dan nasan tsayuwar da kake yi duk dan in sammaka ne to bazakaci ba ta shige gida da uban gudu , ta kusa ture mama .Baza ki dinga nutsuwa ba Aisha ?" kiyi haƙuri mama bazan sake ba ,Aisha ta faɗa dan tasan a yan kwanakin nan mama bata da walwalah , zokiyi min jajjage kiyi sauri cewar mama , rataye hijab ɗinta Aisha tayi ta fara tanayi tana waƙa can kamar an tsikareta ta kalli mama tace "mama yaushe yaya zai zo ya ɗaukeni ? dariya ma taba mama banda abin yaro da kunenta taji ance bazata ƙara zuwa gidan ba tunda ta amsa maganar aure amma yanzu tace " wai gidan yaya , katse tunanin mama tayi da cewa" kuma fa naga an tafi da Ummi nasan tana can tana jin daɗi ni babu ni , Aisha mama ta kira sunanta , na'am Aisha tace " tana shirin kuka , kallonta mama tayi tace " kefa kikace kina son aure to meye na damuwa ? ni bana sonsa mama ki faɗawa malam zan koma gidan yaya wlh anfi cin daɗi , mama ce tace " Aisha ki rufamin asiri dan Allah karkisa malam yazo ya fara kuncemun gwanjon masifa kinsani sanin kanki zaice nice nake zuga ki ,shure shure ta shiga yi dan haka mama ta bata guri .

three days letter.

Ammi ta gama siyyar komai na akwati ranar kaiwa ya rage , zaune Khamis yake a gefenta hanunsa riƙe da waya yana dannawa ajiye wayar yayi ya dubi Ammi da hankalinta ke kan kayan dan har yanzu tana nazarin abin da babu a cikin kayan , Ammi wlh idan yarinyar nan tazo zakici dariya sosai , murmishi Ammi tayi kana tace" ai takusa zuwa Allah dai ya nuna mana ranar lafiya , suna tsaka da magana sukaji sallamar Afnan da jakarta a hannu , oyoyo daughter Ammi tace " tana rungumota , gaishe da Ammi tayi ta dubi Khamis tace " bro ina yini .

Lafiya Khamis yace " ba tare da ya kalleta ba wanan abin nasa ba ƙaramin ƙona mata rai yake ba , ace har yanzu bai ga alamar so a tare da ita ba shin shi besan soyayya bane , duk wanan tunanin a zuciya Afnan take yinsa , shiko Khamis bai san ma tana yiba dan ya kuma maida hankalinsa ga wayarsa , maza kije ki ajiye kayan a bedroom ɗinki kizo kici abinci Ammi ta faɗa tana murmishi , tom kawai tace " ta nufi ciki ,da shigarta ta bugo ƙofa tare da sakin marayan kuka komai ya kunce mata ya zatayi banda momyn ta tace " tazo akwai plan ɗin da zata haɗa da babu abinda zai kawota ganin baƙinciki itama Ammin bata damu da damuwarta ba bare shi da kamar bayama son magana da ita , takuma sakin kuka ta faɗa gado.

Amme da mamaki ya isheta tace " son na rasa meke damun Afnan duk time ɗin da tazo gidannan sai inga kamar tana cikin damuwa , sai da Khamis ya ɗau lokaci sanan yace " Ammi karki sa damuwar wanan a ranki koma mene ne tunda bata nemeki ba just ki ƙyaleta , hmm Ammi tace " a gefen zuciyarta tana hango akwai tashin hankali amma Allah yasa kar harsashen ta ya zamo gaskiya, jin alamun tafiyar takalmi ne yasa ta ɗaga kai , fita zakayi ne my son? Ammi tace " cikin muryar irinta mai damuwa , Khamis dake shirin fita yace " Ammi kince za'a kai kayannan naga har yanzu ba'ayi himma ba , me kakeci nabaka na zuba barin kira momyn Afnan cewar Ammi , cikin sa'a tana gwada lambar ta shiga bayan sun gaisa Ammi tace " maganar

kai kaya in zaki zo kizo da wuri dan Allah , momyn Afnan dake kan hanyar zuwa gidan Ammi tace " mun kusa insha Allah gani nan driver zai kawoni , Allah ya kawoku lafiya Ammen tace tare da ajiye wayar. suna gama waya Khamis ya fice bai jira me Ammi zatace ba , Ammi na shirin tashi ta hango Afnan na tahowa idanuta sun kumbura da kuka , subhanallh my daughter Ammi tace " tare da tambayar ta meke damunta , babu komai Ammi Afnan ta faɗa zuciyarta na ɗaci.
 Tunda Ummi ta dawo daga islamiya ta haɗo kayan wanke wanke tana gamawa ta share gidan leƙa ɗakin anty Fiddausi tayi taga tana bacci lakadan kuma tasan ba lallai ta tashi yanzu ba kasancewar in tana bacci bata tashi da wuri , a hankali a hankali ta nufi ɗakin anty Fiddausi ta hura mata wani abu a baƙar leda ta fito a hankali ta dawo ɗaki.

Tsalle ta shigayi yi tana cewa " matarnan naga rawar kanki yana nema yayi yawa , tunda kike yawan yiwa yaya faɗa dan yabani shayi a baki .kururuwar ihun da taji ne yasa ta bazama ɗakin da gudu tana cewa " lafiya anty , samun anty Fiddausi na soshe soshe tayi tana cewa " wayo my Zak waro ido Ummi tayi tace " Zak kuma ?" yaya Zakarin ne Zaki?...!

Afuwan yau babu yawa ina mura .

BARKA DA SALLAH

*MOM ISLAM*
[23/07, 8:50 pm] Mom Islam Ce: *YARINYA MAI TAƁARGAZA*

*Zainab Habib (Mom Islam)*

*Wattpad @momislam2020*

*AREWA WRITER'S ASSOCIATION*

BOOK 1

*Page 56 & 57*

Maza dan ubanki samomin toka ko a maƙota ne ina jin ƙurajen zafi ke addaba ta anty Fiddausi ta faɗa tana ci gaba da susa , ƙin tashi Ummi tayi sai kuma tayi kalar tausayi ,tsawa anty Fiddausi ta daka mata wanda yai sanadiyar tashin ta da gudu ta ɗauki abin kwashe shara taje ɗibo tokar , da sallama ta shiga gidan dake kusa da nasu , wata mata dake zaune kan kujera ƴar tsuguno ta amasa da wlkslm ,Ummi ce tace " wai inji anty na ki sammata toka ,miƙewa matar tayi tare da karɓar abin kwashe sharar ta ɗibo a murhu marar zafi ta miƙa mata , cikin sauri Ummi ta nufi gida tana shiga ta tarar yaya ya dawo ,tunda anty Fiddausi ta hangota take ƙwala mata kira tana cewa " dan Allah ki kawomin tokar , my Zak jeka karɓo wani kallo yaya Zakari ya watsa mata duk da ta bashi tausayi amma bai nuna mata ba ya fice abinsa.

Tun a mota momyn Afnan tayi wa Afnan waya tace " ta shirya tare zasu je kai kaya dan suga kalar yarinyar inyaso susan nayi , wanka Afnan ta yi kana tayi simple make up ta sanya doguwar riga wacce ake kira da abaya fara mai adon golden ɗin duwatsu ta roling mayafin a kanta jin alamun tsayuwar mota yasa ta feshe jikinta da turare mai ƙamshi a gurguje ta ɗibo takalma da gyale tayo waje , tana zuwa palo momynta tayi sallama , rungume momyn tayi tare da cewa " my momy na shirya ok my daughter momyn ta ,faɗa tana rungume da Afnan , Ammi da ta fito yanzu cikin fara'a tace " sannu da zuwa sis ,ywwa momy tace " kana ta nemi guri ta zauna jerin kaya Ammi ta nuna mata tare da wata jaka daban mai ɗan karan kyau , masha Allah momy ta ce kana tasa Afnan kiran driver ,tare suka shigo Ammi ta nuna musu kayan suka shiga kwashewa suna sawa a bayan mota , to Allah ya kaiki lafiya Ammi ta faɗa cikin fara'a , kallon banza momy ta yiwa Ammi ta gefe tace "amen y Allah ta fito cikin makirci momy tace " daughter naga kin yi kwaliya zomuje man ko kinada gurin zuwa?" murmishin gefen baki Afnan tayi kana tace " muje to momy daga nan naga amaryar yaya , da fara'a Ammi tace " ai kuwa kya ɗauko mana photon ta , tom Afnan tace " suka fice zuwa mota ba tare da ɓata lokaci ba suka ɗauki hanya zuwa Tudun wada, cikin ƙanƙanin lokaci suka iso suna shiga anguwar Afnan ta hau toshe hanci tana cewa " momy kinji wari kuwa ?" uhm momy tace " ba tare da tayi magana ba , sai da taga driver yayi parking a wani ƙofar gida mai ɗauke da ƙofar galan galan kai da ganin gidan kasan talakawa ne tab ɗijam momy tace " tare da sa hanunta a haɓa alamun mamaki ace Khamis ya rasa yarinyar da zai auro sai ƴar gidan talakawa tabbas zan zage dantse gurin nemawa Khamis auran Afnan kuma wlh sai ta mallakeshi duk wanan maganar a zuciya take yi batasan ta fito fili ba , murmushin mugunta Afnan tayi tare da dafo kafaɗar momynta tace " good my momy shiyasa nake daɗa sonki Allah ya barmu tare , waro ido momyn Afnan tayi dan batasan wanan suɓul da bakan da tayi ba driver zai ji , wayancewa tayi da yiwa driver mgna tace " kayi sallama kace anyi baƙi " tom yace " kana ya fice cike da mamakin maganar momy , da sallama ya shiga gidan jin ba'a amsa ba yasa shi ƙara yin sallamar Aisha dake kan bishiyar mangwaro tana leƙensa batayi magana ba ta hau tsinko ɗanyun mangoro tana wurgowa ƙasa , cikin sa'a sai a kan driver a take ya saki ihun da yai sanadiyar fitowar mama da alamu bacci take ihunsa ne ya tashe ta , yana shirin ficewa mama tace " lafiya ? shidai ba marar hankali ba dan bata taɓa ganinsa ba , duk a cikin zuciyarta take maganar ,lafiya ance in shigo in ce muku kunyi baƙi masu kawo kayan aure ne , Aisha dake saman bishiya ta washe haƙora tana dariya ciki ciki , to kace su shigo mama ta shiga shimfiɗa tabarma kusa da bishiyar manguwaro , Allah ya temaketa gidan a share yake ta fara ƙwalawa Aisha kira tana cewa " maza kizo ki kira maman Ummi kice mata ga masu kawo kaya sun zo , shiru mama taji babu amsa , kira ta kuma ƙwalawa a karo na biyu nan ma shiru , ta katanga mama ta leƙa ta ƙwalawa maman Ummi kira tace " tazo ga masu kawo kaya , gani nan fitowa maman Ummi tace " tare da yafo mayafi ta fito , momyn Afnan dake shirin fitowa ita da Afnan cikin ƙyanƙyami suke taka ƙafarsu haka dai suka lallaɓa suka nufi gidan Afnan mayafinta na kan hancinta , momynta data lura da hakan tace daughter karki sa damuwa ba jimawa zamuyi ba ki buɗe karsu zargi wani abun , sa driver tayi ya fara shiga da kayan Aisha dake kan bishiya tana ganin akwatunan tafara rawa da ƙafa tana murna ,sallamar su momyn Afnan ne ya dakatar da ita wa ƴan'nan ƴan gayun fa ? ta tambayi zuciyarta jibesu kyawawa amma wlh dole in nuna musu yau ina cikin farinciki sosai.
Suna shigowa mama da maman Ummi suka taresu da fara'a shigowar malam yasa mama ɗaga kai dan ganin ko dame yazo , hanunsa riƙe da leda babba cike take da kayan motsa baki ya risina yana gaida su momy ,a yangace momy ta amsa ta dubi su mama ta gaishesu , ajiye ledar yayi gaban su momy yana washe baki ya miƙe ya fita , yana fita Afnan ta raɗawa momynta a kunne mom wanan ne kayan tarbar tamu ? karaf a kunen Aisha Afnan na shirun ƙara yin magana taji saukar ƙaton mangoro a kanta ɗanye ,ihu tasa tare da riƙo momynta cikin fusata momyn ta kalli sama kamar zatayi masifa sai kuma ta dakata batayi ba, kunya iya kunya mama taji ɗaka kai tayi

ta hango Aisha zaune a kan bishiya tana rar raba ido innalilahi mama tace " tana tafa hannu kana tace " wato Aisha kece a nan me kikeyi ? sai da ta ƙwalowa momyn Afnan ta sauko ta fece da gudu , iya kawaici da mom Afnan tayi wanan karo bazata iya daurewa ba, take faɗa cikin ranta , a fili tace " wanan wace iriyar sheɗaniyar yarinya ce ?" zaro ido mama tayi ba tare da tace komai ba , maman Ummi ce tace " amaryar ce ,da mamaki Afnan da momynta suka haɗa baki gurin cewa " amarya kuma? eh maman Ummi tace " sai kuma daga baya take dana sanin gaya musu , tabɗijam Afnan ta faɗa tana keɓe baki , buɗe kayan akwatin su mama suka fara suna yabawa da tsada dakuma kyan kayan , miƙewa sukayi tare da cewa" to sai anjima .
Kunto ɗaurin zaninta mama tayi ta ƙirga dubu goma ta miƙa musu , no ki barshi kawai momyn Afnan ta faɗa tana ci gaba da tafiya, to Allah ya kiyaye hanya su mama suka faɗa cikin sanyin jiki , suna shirin fita harsu kusa fitowa daga gidan sai ga Aisha nan ta taho da uban gudu kamar zata bangaje Afnan , kutumar uba Afnan ta faɗa tana shirin damƙo wuyan Aisha , sorry my daughter ba girman ki bane karki kulata mu da muke neman mafaka?" momy ta faɗa tare da rungume Afnan suka shige mota , suna shiga driver ya jasu , cikin ƙanƙanin lokaci suka iso gidan Ammi , koda driver yai parking suka nufi part ɗin Ammi zaune suka sameta ita da Khamis da alama wata maganar suke mai muhimmanci , shigowarsu ne ya katse wa su Ammi maganar....!

Comments yayi low😏 kun sanfa mai jego ce zan tafi hutu yasin🙄

MOM ISLAM
[25/07, 2:19 pm] Mom Islam Ce🌹: *YARINYA MAI TAƁARGAZA*

*Zainab Habib (Mom Islam)*

*Wattpad @momislam2020*

*AREWA WRITER'S ASSOCIATION*

BOOK 1

*Page 58 & 59*

Kara gaida momy Khamis yayi kana ya nufi part ɗinsa , da ido momy ta yiwa Afnan nuni da ta bishi , miƙewa Afnan tayi tare da cewa " bro yau baza kasha tea bane ? tana tafiya tana maganar Ammi duk ta lura da abinda sukeyi amma sai ta nuna bataga komai ba , sai da Afnan ta ƙule momy tace " wa Ammi gaskiya da ina nan son ya fara neman yarinyar nan wlh da ban barshi ya aureta ba , kasancewar su talakawa futuk bugu da ƙari naji ana cewa" wata yar yarinya itace matar tasa gaskiya Ammi za'a cutar da rayuwarsa bakya tunanin ya daɗe beyi aure ba yanada buƙatar iyali ? nisawa Ammi tayi kana tace " nasan da haka karki manta son ba yaro bane kuma ban isa nayi masa auran dole ba cox dole sai abinda ya kawo min zan aminta dashi , momy da ta gama ƙuluwa da maganar Ammi tace " nifa dama bawai ina gudun matar da zai aura bane ki fahimceni Ammi ya kamata mu zaɓa masa mata yar gidan mutumci kuma ba talaka ba gudun kar mu ja masa raini ga abokansa , na

fahimceki Ammi ta faɗa tana jinjina maganar momy ,dama tasan za'ayi haka dan tana ganin yawancin ƙule ƙulensu bata dai nuna musu ne duk cikin zuciyarta take wanan batun , miƙewa momy tayi tace " ni zan tafi ina ganin sai satin biki zan dawo , Ammi da mamaki ya isheta ace kai da ɗan uwanka bazaku kashe ku rufa ba tace " Allah ya shige mana gaba zan kira Khadija daga gombe tazo gobe , yatsina fuska momy tayi tare da cewa " wato Ammi Khadija ta fini kenan ?karki mance mu biyu ne a gurin mahaifiyarmu mata kuma tace " ki kula da ni meye zatayi miki wanda bazan iya ba ?" miƙewa Ammi tayi ta dafa kafaɗar momy tace " ai ke kinada aure kuma mijinki na da buƙatar kulawarki so ki bari in tazo zata tayani wani abun, momy da tayi shirin tafiya haka ta fice batare da ta ƙara bi takan Ammi ba , a zuciyarta ta ɗau alwashin sai Khamis ya auri Afnan ko ta halin yaya.
Koda Afnan taje bedroom ɗin Khamis samunsa tayi kwance yayi ruf da ciki yana dane dane a wayarsa , da sallama ta ƙarasa ta zauna bakin gadon , sanin darajar amsa sallama ya sashi amsawa badan haka ba bazai kulata ba , my bro naga kamar kana cikin damuwa ne ? Afnan ta faɗa cikin sanyin murya fuskarta na kan tashi , ko juyowa beyi ba bare tasa ran zai amsa tasan abu ne mai wuya shayo kan wanan bauɗaɗɗen , tsaki taja ba tare da ta bari ya jiba ta kai hannu zata shafo kansa ,a faɗace Khamis yace " last worning wlh ko da wasa karki kuskura naga kamar kina wasa da tarbiyarki ya daka mata tsawa kana ya nuna mata hanyar waje yana masifa , da kuka ta fito ta faɗa jikin Ammi tana daɗa shagwaɓe fuska , daga ina kike ?" Ammi ta tambaya "daga room ɗin bro Ammi har dukana sai da yayi , zaro ido Ammi tayi ta hau rarrashin Afnan tana cewa" zai fito ya sameni ƙyaleshi.
Dawowa Aisha tayi da gudu ta faɗa kan mama tana cewa " mama wanan duk nawa ne ? wanketa da mari mama tayi tana yi mata faɗa , maman Ummi ma dake gefe bata sanya baki ba sai shirin buɗe akwatin dake gefenta da tayi , wayo daɗi Aisha ta faɗa idanunta cike da hawaye , kuka take amma tana dariya tana ganin an buɗo na kayan kwaliya ta zo gurin ta tsaya tana zaro ido , da gudu ta fice tana fita ƙofar gidan su taga wata ƙawarta mai suna Nafessa zata kai shekara sha biyu , janyota Aisha tayi tace " albishirinki ? goro Nafisa tace " tana dariya , an kawo kayan aure na yarinya harda kayan kwaliya da atamfofi ke zomuje ki gani , binta Nafisa tayi suka shiga gidan, suna shiga mama tace " me kikazo yi ?" nazo nunawa Nafisa kayan ne , zaro ido maman Ummi tayi kana ta watsa mata daƙuwa ta miƙe tana shirin rarumar sanda suka ruga da gudu.
Darajar cikin dake jikinta yasa shi miƙewa karɓo tokar ya fara shafa mata tana yi masa wayo wayo yana gamawa ya shige ciki ya barta , gado ya faɗa cike da tunani iri iri to me Fiddausi take nufi? tana nufin son Ummi nakeyi kenan ko me ? to inma soyayyar ce Ummi yarinya ce mai hankali ga nutsuwa dole nan gaba inta girma na zaɓa mata miji na gari Allah kaduba lamurana ya cigaba da kwanciya zuciyarsa babu daɗi , gidan su ma yayi yajin aikin zuwa kasancewar wanan irin badaƙalar cin mutuncin da zaije ya tarar.
Tun asbha Khamis yai wanka yaje sallah yana dawowa ya feshe jikinsa da turare ya nufi palo ganin Ammi bata fito ba yasa shi zuwa bakin ƙofarta yana nock , buɗewa Ammi tayi tana sanye da hijab har ƙasa my son ka tashi lpy ? ƙarasa shigowa Khamis yayi ya durƙusa har ƙasa ya gaida Ammi ta dafa kansa tayi masa adu'a ya koma ya zauna , lafiya my son naga ka fito da wuri haka ? Ammi ta jefo masa tambaya , sosa kansa yayi tare da sunkuyar da kai yace " Ammi na zani unguwa ne inason zuwa gurin friend ɗina ne mu fara shirya abubuwan da za' ayi lokacin bikinnan , dariya Ammi tayi tace " zumuɗi bikin saura 3 weeks amma kake ta ganɗoki pls ka kwantar da hankalinka bakada matsalar komai ai kuɗi ne meyinsu to bamuda problem just kaje ka kwanta kawai , no Ammi ji nake kamar in janyo wanan kwanakin nakeji , kunya ce ta rufe Ammi a zuciyarta tace " to yarinya ƙarama dole fa sai nasa ido a kanku koda tazo gidannan duk da kace badan komai kake sonta ba zaka iya renonta , Ammmeee Khamis ya kira sunanta dan yaga ta lula duniyar tunani na'am ta amsa tana shirin miƙewa dan karya gano tana tunani , murmishin gefen baki Khamis yayi ko me ya tuna oho , to Ammi na koma zanje na kwanta zuwa 11 o

clock a ta sheni, ok Ammi tace " ya fice ya nufi side ɗinsa yana shiga direct bedroom ya wuce ya faɗa bed tare da sakin na nauyan nunfashi ya janyo  phone ɗinsa daya ajiye yanzu yana duduba hotuna tsaki yasa kana yace " babu hoton Esha ma a ciki ya ajiye wayar ya ɗauki pillow ya rungume ,bacci yai awon gaba da shi cike da mafarkin Aishan sa.
 morning.
Malam na dawowa daga masallaci ya hau surfawa mama faɗa yana cewa " saboda Allah kima duboni kiji me ya hanani fitowa jiya da daddare abin duniya ya gagareki ko ?" wlh kidinga yin abinda kuɗa zai bi , mama dake gaban murhu tana dama kunu ta ɗaga kai ta dubi malam kana tace " to ai naga babu wanda ya damu da damuwar kowa ne shiyasa banyi karambani ba , ta cigaba da abinda takeyi , hannu malam yasa a baki alamun mamaki harda yaushe mama ta koyi gawa mutane magana cab dole yayi wa tufka hanci tun kafin ta wuce tunaninsa.
Ina kayan suke ?" kafin mama taba malam ansa Aisha ta fito da gudu tace " gasu kuma maman Ummi tace " duka nawa ne malam harda kayan kwaliya , kafeta da ido malam yayi beyi mamakin maganar da take faɗa irin haka ba sbda yarinya ce ƙarama , a cikin zuciyarsa har yanzu baya dana sanin aurar da Aisha ko kaɗan , ka shigo malam ka zaɓa min kaya innayi wanka du zansa , ta fice bata jira amsar saba , mama dake zaune ko uffan batace ba taci gaba da abinda ke gabanta , zama malam yayi ya fara buɗe kayan yana yaba kyansa da tsaruwarsa , tabbas ya zaɓawa Aisha mijin aure ......!

_AFUWAN JIYA KUN JINI SHIRU_ 

*MOM ISLAM*
[26/07, 6:17 pm] Mom Islam Ce: *YARINYA    MAI  TABARGAZA*

*Zainab Habib (Mom islam*

*Wattpad@ momislam2020*

*AREWA WRITERS ASSOCIATION*

BOOK 1

Page 60 & 61

Aisha na fitowa  daga wanka ta shigo ɗakin mama  da sauri  ganin bataga malam ba yasa ta  leƙowa tace " mama ina malam ɗin? oho mama tace " batare da ta kalleta ba , kai tsaye ta buɗe akwatin ta fiddo wata fitinaniyar riga mai kyau pink mai adon duwatsu da flawoyi ta yafa gyalen bata tsaya shafa mai ba ta feshe jikinta da turaruka sunkai kala ashirin amma kowanne sai da ta fesa , ta fito da gudu tana cewa" mama na tafi gidan su yaya a ƙafa , innalilahi mama ta ambata tana mamakin rawar kai irinna Aisha , tana fita taci karo da motar Khamis na tahowa , my Esha ya ƙwala mata kira cikin dadaɗan muryarsa, na'am Aisha ta amsa tana yi masa fari da ido tace " kyakyawa zo ka kaini gidan yaya kaji ,murmishi yayi kana ya lumshe idonsa ya buɗe mata gidan gaba kana yace " shigo tana shigowa ya figi motar suka

bar anguwar , wani irin ƙamshi yaji yana ziyartar sa na musamman ji yake kamar ya rungumeta , sai kallon fuskarta take a mudubi tana dariya ,ɗora hanunsa a kan nata hanun Khamis yayi jin jikinsa yayi yarrr yasa shi saurin janyewa tare da cewa" my Esha kinyi kyau sosai fa , ƙyal ƙyalewa Aisha tayi da dariya tace " kayan aurena ne na ɗauki wanan gudowa ma nayi fa , zaro ido Khamis yayi yace " momy batasan kin fito bane ? eh wlh inason zuwa gidan yaya inga Ummi , ƙara lumshe ido yayi a karo na biyu yana jin wutar sonta na ƙara ruruwa cikin zuciyarsa , suna cikin tafiya ta haango mai awara yana tallah da ƙarfi Aisha tace " ƙyaaak ƙyawaaa tsaya ka siyamin awara, awara kuma ? Khamis ya tambaya yana dariya , eh Aisha tace " tana shirin buɗe murfin mota stop my Esha zan siyo miki gobe banison siyan abu gurin masu tallah afuwan , ko saurarar shi batayi ba ta buɗe motar ta fice da gudu kasancewar ya tsayar da motar yana yimata magana , kai mai awara ka tsaya Aisha ta faɗa tana yi masa alamu da hannu tsayawa mai awarar yayi yace " ta nawa za'a baki ? ta hamsin Aisha ta faɗa tana kallon motar Khamis yana sa mata a leda ta arce da gudu ta nufi mota tana haki , da gudu mai awara ya biyota yana shirin buɗe motar cikin masifa , Khamis da mamaki yaishesa ya ciro ɗari biyar ya miƙawa mai awara , mai awarar na shirin basa canji Khamis yace " barshi jeka , kan uba Aisha tace" cike da masifa ta hamsin na siya ka bashi ɗari biyar wlh zan kamaka koma yau ba ta nuna mai awarar tana masifa , dariya taso ba Khamis sai kuma ya dake ,jin taƙi yin shiru tana ta zabga masifa ,kamota yayi ya haɗe bakinsu guri ɗaya ya fara tsotsa kamar yasami sweet idanunsa a rufe yake wanana aikin zaro ido Aisha tayi tayi nasarar fizge kanta tace ? walahi bakinka ƙamshin minti amma malam yace " wanan iskanci ne kuma wlh sai na gayawa mama , lumshe ido Khamis yayi yana buɗesu ya sauke kan Aisha am sorry my Esha karki gayawa momy pls zan siya miki chocolate , maƙe kafaɗa Aisha tayi tare da kafesa da ido , me kike kallo my Esha ?" Khamis ya jofo mata tambaya babu komai Aisha tace " suna isowa anguwar tace " to nagode tana shirin fita ya riƙo hanunta tare da cewa " bakison muyi fira ko my Esha ,inaso Aisha ta faɗa tana gimtse fuska dan burinta bai wuce ta ganta a gidan yaya ba , to sai anjima Khamis ya faɗa kamar marar lafiya , bata kulasa ba ta fice da gudu tana dariya , shikam ya daɗe a gurin ya juya kan motarsa ya ɗauki hanyar zuwa gida.

Tana shiga babu sallama ta shige ɗakinsu da gudu , faɗawa kan Ummi dake bacci tayi tana cewa " ke tashi nakusa aure , kamar daga sama Ummi taji maganar Aisha ta miƙe ta rungume Aisha tayi suka shiga hira , anty Fiddausi dake shirin zama kan kujera tajiyo maganar Aisha ta zaro ido tare da cewa " waye a ɗakinnan ? nice Aisha ta faɗa cikin ɗaga murya, wato kinzo ne babu ko sallama bare ki gaisheni ? yi haƙuri anty Aisha ta faɗa dan ba da masifa tazo ba shiyasa ta yi ladabi , fitowa tayi ta gaida anty kana ta koma gurin Aisha .

Tun a mota Khamis yake jinsa wani iri wanan yarinyar tana neman sashi cikin wani hali , kwata kwata yanayinsa ya sauya haka ya isa gida jikinsa ba ƙwari ya na shiga palo bai ci karo da kowa ba hakan ya sashi wucewa part ɗinsa yana shiga ya cire agogon hanunsa da zobunansa ya cire kayan jikinsa ya ɗaura towel ya nufi bathroom ya kuna ruwan ɗumi ya daɗe a bahon wankan idanunsa a lumshe yana tuno Aishansa , ganin tinanin bazai fisheshi ba yasa shi fitowa ya goge jikinsa yakuma ɗaukar wani towel ɗin ya ƙugunsa , jiki ba ƙwari ya fito ya janyo stool ɗin dake gaban miror ya zauna yana ƙarewa kansa kallo , kyakkyawa Khamis ya kira sunan cikin sanyin murya sai yaji kamar itace " mace ta farko data fara kiransa da kyakkyawa, a gurguje ya taje lalausan gashin kansa ya shafe jikinsa da mayuka masu ƙamshi , drower kayansa ya nufa ya ciro wani lalausan yadi mai ruwan madara ya sanya hula kana ya ciro farin takalmi ya ciro wani agogon mai tsadar gaske da zobuna ya fito ya nufi part ɗin Ammi bai sameta a can ba ya nufi palo samunta yayi a zaune tana waya cikin wayar nata ne yaji tana cewa " ai baze gagara ba , to meye Khamis ya tambaya cikin zuciyarsa , ka fito Ammi ta faɗa tana yi masa murmishi , eh Ammi ya shirye shirye ? dariya Ammi tasa kana tace " yau dai saura one week ankusa angon mamana , sunkuyar da kai Khamis yayi yace " Ammi na angma gyara

ɗayan part ɗin fa , masha Allah Ammi tace "tare da cewa" ai tare zamu zauna da Aishar ko ?" Ammi tayi tambayar ne cikin sonjin me zai ce ,am um Ammmi Khamis ya fara dubur burcewa murmushi Ammi tayi kana tace " Allah ya kaimu lokacin ,amen Khamis yace " kana ya miƙe ya fice , kai tsaye parking spice ya nufa yana shirin fita yaji ana kiransa tabbas muryar Afnan ce ya juya yana kallonta ,sanye take da riga da wando sun kamata sosai pls zan bika ta faɗa tana kashe masa ido cikin ƙissa , no ba dake na shirya tafiya ba ,Khamis ya faɗa yana shirin buɗe murfin mota , riƙe murfin motar tayi ta juya ganin babu mai kallon su yasa ta ɗora hanunta kan nasa ta matso daf da shi suna jin nunfashin juna takai bakinta dai dai saitin kunensa kana tace " ina sonka yaya Khamis...ya kasa koda motsi sai kalonta da yakeyi beyi ƙoƙarin hanata kusantoshi da tayi ba ya juya da nufin barin gurin ya zagaya ya nufi ɗayar motar tasa ya shige da sauri kana ya rufo da ƙarfi ya fice ba tare da ya kulata ba dan basa shiri kuma duk wani ƙulle ƙulle da sukeyi yana ankare da su yasan momynta ce mai shirya mata komai , mai gadi na jin horn ya fito daga ɗakinsa da gudu ya buɗe get ɗin Khamis ya fice da gudu, yana tafiya yana tunanin iskanci irinna Afnan tabbas ita cikakkiyar mace ce kuma mai aji amma bazai iya auranta ba badan komai ba sai dan baya ra'ayin auranta ga wacce yagani yaji yana so kuma insha Allah next friday zamu kasance a tare yana tafiya yana tunani , har ya iso wani katafaren mall mai kyan gaske mislta kyawunsa ɓata lokaci ne bare kayan cikinsa sai yayan manya , parking yayi a inda aka tanada dan ajiye motoci ya nufi ciki ya danna wani abu ƙofar mai ɗauke da gilashi ta buɗe ya shiga....!

Nagode jariri yana lpy yana gaida masoyan mamanshi

*MOM ISLAM*
[04/08, 8:31 pm] Mom Islam Ce: *YARINYA MAI TABARGAZA*

*Zainab Habib (Mom islam*

*Wattpad@ momislam2020*

*AREWA WRITERS ASSOCIATION*

BOOK 1

Page 62 & 63

Yana fita bai yi nisa da anguwarsu ba ya tsayar da motar tare da kifa kansa tunani ya fara shin wai wa yannan mutane mesuke so dashi ne ? bashida mai bashi amsa yasa shi yin shiya ya juya motar zuwa gidan su bayan yai horn mai gadi ya buɗe masa ya shige yana shiga ya sami Ammi da Afnan a palo suna zaune amma inka kalli fuskar Afnan babu walwala, da sallama ya shiga ya zaune gefen Ammi " a'a my son ya naga ka dawo daga fitarka bai bawa Ammi amsa ba sai ma kallon Afnan da yake kallo mai kamada na tsana, Ammi ta lura da kallon da yake wa Afnan hakan yasa tace" maza muje ɗaki inada magana dakai son , a lokacin ne ya kalli Ammi ya sunkuyar da kai ya nufi hanyar ɗakinsa , miƙewa Ammi tayi tabi bayansa , a palonsa ta zauna dan ya shiga bedroom ɗinsa , yana fitowa ya zauna daf da ita Ammi ta dubesa tace " my son bana son kana ɗorawa kanka damuwa inhar matsalar Afnan ne

ka kawantar da hankalinka nasan abinda suke kitsawa itada mahaifiyarta kuma na tabbata kansu suke so ba komai ba kadena sa damuwa pls Ammi ta ƙareshe maganar kamar zatayi kuka, ruƙo hanunta yayi kana yace " Ammina kinsan damuwa ta nagodewa Allah daya zaɓamin ke a matsayin uwa .
Anty fiddausi tasa yaya Zakari ya tattara su Aisha ya maida gida , babu musu yace suje su huta dama suna buƙatar zamansu guri ɗaya sbda suji daɗin bidirinsu , tun a mota suke ta nuna masu siyarda kayan marmari da yaya ya gaji ya fita ya kwaso musu soyayyen kifi ya kawo musu , babu godiya suka karɓa suna turo baki , lura da wulaƙancin da suke ne yasa shi cewa" to me kukeso ?"apple suka bashi amsa cikin rawar jiki ,yaya Zakari daya tunzura yace" dan ubanku kunsan kuɗinsa kuwa ? to yanzu sun dena saidawa uku ɗari biyu yaja motarsa yana cigaba da mita , juyowa yayi yaga suna shirin buɗe ledar sufara ci ya daka musu tsawa tare da cewa " wlh inhar baku bari munje gida ba to nida ku ne , cikin ikon rabbi sai gasu a ƙofar gidansu yana shirin buɗe mazauninsa suka buɗe suka sa kai gida , girgiza kai yayi ya bi bayan Aisha , suna shiga yai sallama mama ya samu a zaune a bakin ƙofarta tana zaune durƙusawa har ƙasa yai ya gaisheta bayan ta amsa ne tace " yanzu Aisha tashigo da gudu tare kuke? eh yaya yace " gidanmu taje tun safe harda Ummi na dawo dasu , ywwa gara da ka dawo da Aisha ,shigowar malam yasa yaya Zakari juyawa daga tsugunen da yake yace " malam barka da yamma , ywwa malam yace " kana ya miƙe ya nufi ɗakinsa , kuɗi masu yawwaa yaya Zakari ya bawa mama yace " gashi tayi hidimar biki sanya albarka gami da godiya mama tayi masa ya miƙe ya fice ,yana fita Aisha ta fito ta haye jikin mama , jinjina kai mama tayi tace " waye ya kaiki gidan yayanku , Khamis taba mama amsa , zaro ido mama tayi tace " Khamis kuma har da yaushe yazo anguwar nan ? tun da safe Aisha taba mama amsa , hmm kawai mama tace " kana ta janyo ledar ganye tace " tsinke min miyar taushe zanyi , da murna Aisha ta janyo ta fara tsinkewa.

******************

ƊAURIN AURE

Ranar ta kasance Juma'a dubban jama'a suka sheda ɗaurin auran Khamis da Aisha akan sadaki mafi albarka, ɗaurin auran da ya samu shedu da manyan mutane ta ɓangaren mahaifin Khamis da malamai ta ɓangaren malam , Khamis na hango sanye da wata fitinanniyar shadda gezna wace ta amsa sunanta ga abokansa suna gaisawa da mutane .
daga haka suka nufi mota bakin ango kamar gonar auduga , motoci ne a jere a ƙallah zasu kai guda talatin duk manya ne a ciki direct anguwarsu Khamis suka nufa parking sukayi a ƙofar gidan suka fifito badan motocin bazasu isa filin gidan ba sai dan zuwa yamma za'awuce da amarya hall , ango ne a gaba yayin da abokansa wasu a gefe wasu a bayansa daka gansu kasan nera ta zauna , kai tsaye parlon Ammi suka nufa sun sami palon cike da mata ƴan taro Ammi ce tasa a kaisu ɗayan part ɗin da yake a tsare anyishi domin hutawa , da shigarsu ƴan aikin gidan suka fara kokawar shigo da take away kasancewar daga hotel akayi odar komai sunci sunsha dan drinks kamar ba da kuɗi aka siyesu ba .
Tunda aka ɗaura aure aka hana Aisha fita cikin ikon Allah ta fice tabi gidan su Ummi dama Ummi a shirye take suka fice fuskarta cike da kwaliya dan anyi mata makeup kuma tayi kyau , gurin mai siyarda jigida ta nufa kasancewar jikinta akwai dubu ɗaya da malam ya baya duk akan rarrashi ta kashe , suna shiga shagon suka gaida baba tsoho yana amsawa suka nemi gurin zama , janyo jigida Aisha tayi tace " nawa wanan ?" ɗari biyu tsohon yace " taɓe baki Ummi tayi tace " taɓɓ wlh kada ki siya zomu shiga cikin kasuwa , wurga masa jigidar tayi tace" yasin bazan siya ba kaci kayanka , tsoho da mamakin rashin kunyar da sukayi masa yace " kuna neman albarka kuwa kuzo har kan kayana kuna yimin rashin arziƙi rawa suka shiga yi masa suna tafi , bulala ya ɗauko yana shirin dukansu sukaja jigidar sukayi gaba suna yi

masa gwalo da gudu ya bisu amma ya kasa cimmasu hakan yasa tsoho ya dawo ya riƙe guwaiwa yana haki.
Wani guri suka samu nesa da gurin tsohon suka zauna suna shawara akan jigidar suka fara Ummi da tayi tunani tace " nidai na bar miki tunda aure zakiyi, mtsw Aisha taja tsaki tace " ke dallah auran banza dan sun raina min hankali zasu ce wai kar na fita to na dinga fita kenan walh daga yau har ranar da naga dama , waro ido Ummi tayi tace " kin mance anty Fiddausi gidansu ma ba kullum take zuwa ba ? oho ita taso walh nikam babu mai rainamin wayo an gayamusu ni sa'arsu ce hamm Aisha tace tana girgiza ƙafa, yanzu ki tashi wlh kwaɗayin awara nakeji kuma bada wanan kuɗin zan siya ba dan wanan kuɗin inason siyan mudun madarar kuka ne tunda naji mama tace " auren ba'a dawowa gida akan kari , mtsw Aisha takuma jan tsaki tare da cewa " wlh badan yana siyo min abin daɗi ba wlh babu abinda zesa inje gidansu , Ummi ce ta katseta da cewa " wlh shawara Aisha kawai kice kin fasa muci gaba da wasanmu ....bata gama rufe baki ba Aisha tace " kan uba wlh bazan yarda ba duk kayan da suka kawo na wanan akwatunan kice su kwashe tab bakida hankali kuma malam yace " zai bani kuɗi indiga kashewa kinga dole na yarda kema in kina son saurayin nawa wlh zanyi masa magana ya aureki kema a kawo miki naki kayan , taɓ Ummi tace " mezanyi dashi bakinsa abin ƙyama ja kamar maye , wani wawan mari Aisha ta bata tana mayarda nunfashi, kika mareni Ummi tace tana riƙe da kumatu tana shirin yin kuka , Aisha da ko a jikinta tace " wayace kicewa kyakyawa maye wlh zan ƙara miki mu kunce ma , ƙin miƙo hannu Ummi tayi haka dai suka miƙe kowa yayi tashi hanyar , Ummi hanyar gida tayi Aisha kuma cikin kasuwa ta miƙe , tana tafiya tana masifa batasan tazo gurin Lawali mai kazar amare ba , tsayuwa a gurin tayi tana tunanin gurin zuwa ....!

Masu yimin ya jiki ina godiya Allah yabar ƙauna ina ganin comments ɗinku inayi muku fatan alkairi jiki alhmdulilh .

*MOM ISLAM[06/08, 12:30 pm] Mom Islam Ce: *YARINYA MAI TABARGAZA*

*Zainab Habib (Mom islam*

*Wattpad@ momislam2020*

*AREWA WRITERS ASSOCIATION*

BOOK 1

Page 64 & 65

Cikin sa'a Lawali ya hangota ita bata gansa ba ji tayi ance wa na kama?" a gigice ta juya tare da zubawa da gudu ta nufi hanyar gida jiki na rawa idanunta har suna fitarda ƙwallah tasan inhar ya kamata to kashinta ya bushe.
Ta nufi gida da mugun gudu , tana shiga yan uwan mama suka tarota tare da cewa " tun ɗazu angwaye sunzo sunata jiranki ina kikayi ?sai a lokacin ta tuno taga jerin motoci a ƙofar gidan su , kamota wata mata mai kamada mama tayi ta cire mata kaya tare da sake yi mata wanka , kasancewar tasha lalle tun jiya da kitso yasa yau makeup kawai ya rage suna shirin shafa mai sukaji sallamar wata mata da alamu ba

musulma bace tana ɗauke da wata jaka mai kyau, bayan sun gaisa da mutanen tsakar gidan tace " daga gidansu oga Khamis ne aka aikoni nayiwa amarya kwaliya , to maza kije Aisha kinga ke ake jira ƙanwar mama tace " tare da shinfiɗa musu tabarma , cikin sauri aka tsarawa Aisha kwaliya tabbas inba kayi mata farin sani ba, ba lallai kace ita ce ba sbda tayi kyau sosai , wata weeding gawn ta jiro daga bag ɗinta ƴar madai daiciya iya tsayin Aishar ta sanya mata tare da belt akayi mata rolling kanta da farin raga mai adon bit mai kyau , kowa dake gurin ya  yaba kyau irin na Aisha  wani fitinannen takakmi aka ciro mata hill mai tsini sosai , wow fans kuzo kuga Aisha nidai nace amarya ƴar mitsila kufa?.
Ƙannen Ammi ne suka shigo su biyu da ganin su kaga wayayyun mata bayan sun gaisa da su mama suke tambayar ina  amarya , nuna Aisha akayi ɗayan ƙanwar Ammin daskarewa tayi yayin da taga Aisha cikin zuciyarta tace " wanan ƴar yarinyar gaskiya an tsinkamu to ubanme zataje tayi a can ɗin , ƙanwar Ammi da sukazo tare ta dafa kafaɗarta tare da cewa" muje ko mu ake jira , ok tace " suka nufi mota , wasu daga cikin yan uwan mama duk sun shiga motar harda maman Ummi harda Ummin ma kasancewar ta ƙawar amarya lol .
Wata rantsatsiyar mota mai nunfashi aka sanya Aisha kasancewar tsoron dake cinta ga gudun da tasha ɗazu gakuma wanan mota mai kamada aljannar duniya yasa bata lura da mutum a kusa da ita ba.
Ji tayi an shafo gefen fuskarta a razane ta juyo sukayi ido biyu da Khamis murmishi ya sakar mata tare da yi mata alamar tayi shiru , shirun tayi ta sunkuyar da kai dan tsoron motar takeji , dubawa yai yaga driver baya ganinsa sbda motar  zubulin sharoon ce amma ta tsakiya da gilashi baƙi koda driver bazai hango na back side  ba , ɗan zamewa yayi ya rage tsayinsa suka koma tsayi ɗaya da ita yace " my Esha kinyi kyau sosai  , dariya tasa zatayi magana da ƙarfi  ya rufe bakinsa da nata yana aikawa kansa da saƙo dan ita batasan dalilin hakan ba , ya jima a hakan jin mota ta tashi yasa shi rungumeta , gaskiya yau abinda yakeji na dabanne ga wani sanyin daɗi dake ziyartar shi gashi ga Aishansa yau wayo daɗi , yimin hira mai daɗi my Esha Khamis ya faɗa yana kashe mata ido ,ganin dimple ɗinsa da suka lotsa tasa dariya tana cewa " waye ya wawake maka kumatu ? nima inaso , Allah ne Khamis ya faɗa yana dariya to shi wanan jan bakin fa ko gogawa kayi ?" noo my Esha kin cika tambaya hira fa nace kimin Khamis ya faɗa yana kama kumatunta , jin anyi parking yasa Khamis leƙawa , har an iso cewar Khamis.
Sai da kowa ya gama fitowa aka buɗewa su Khamis mota a hanunsa ya rungume Aisha suka shiga ciki masu gulma nayi masu dariya nayi , Afnan da tuni ta hallara mazauni tayiwa kanta kusa da Khamis , itama tayi kyau ba lefi amma fa Aisha ta zarce sai dai  dole za'ace Afnan ce Amarya tunda itace babbar budurwa a gurin , guri ya cika da masoya da abokan arziƙi kiɗa ke tashi kamar gurin ze tsage Aisha da ba sabawa tayi ba sai ƙam ƙame Khamis take wanan lamari ba ƙaramin yiwa Afnan ɗaci yayi ba .
MC ne ya miƙe tare da cewa" batare da ɓata lokaci ba zamu kira amarya da ango suzo su nuna farincikin su a wanan fili , Khamis ba kunya ya ruƙo hanun Aisha suka shiga tsakiya yana jujuyata ,tasowa Afnan tayi cikin yanayi mai kamada na yan bariki tazo daf da Khamis ta raɗa masa a kunne zan wakilci ƙwailar matarka inshiga a madadinta , ko kallon inda take beyi ba ya rungume Aisha tare da ƙwalawa mai hoto kira , haka aka dinga watsa hotuna kamar banza , a wanan karon Afnan rai ya ɓaci sosai da kuka ta fice daga hall ɗin zuciyarta kamar zata tsinke MC ya wasa Asha da Khamis kan Khamis kamar zai fashe an yabi tauraruwar sa ' an raba kyaututuka sosai babu wanda bai fito da kyauta ba , an tashi taro lafiya Khamis ya sunkuci abarsa suka wuce mota , suna shiga ya kwantar da ita kan sitt ɗin motar yana daddan na mata jiki wai ta gaji tunda suka shigo batayi magana ba duk surutunta kamar ruwa ya cinyeta , ganin yana shirin ɗaga mata riga ne yasata cewa " Allah ya hana ta ture hanunsa , murmishi Khamis yayi yace " aini bai hanani ba ko ? haka malamin mu yace " wai iskanci ne , Aisha ta faɗa tana daɗa ture masa hannu , oh Khamis ya dafe goshinsa kome ya tuna sai naga ya cire hanunsa tare da

cewa" Aisha maza tashi ki bani labarin yanayin da kikaji a gurin shagalinnan , tab Aisha ta faɗa tana taɓe baki , tace " sunayin abu kamar wasu mahaukata nima da ka ɗaukeni badan maman Ummi tayimin faɗa ba wlh bazan yarda ba sbda naga ka rainani , eyeeeee Khamis yace "yana waro ido tare da cewa " mai maita inji oya me kikace ? rufe baki Aisha tayi tare da miƙewa daga kwanciyar da yayi mata tace " cewa nayi kai kyakyawa ne, uhm Khamis yace " tare da lumshe idonsa ya lashi pink lip ɗinsa na ƙasa hakan yasa dimple ɗinsa ya loɓa  wanan abu ba ƙaramin yiwa Aisha kyau yake ba , taɓowa tayi tana dariya, shima dariyar ya tayata sukeyi kamar wasu kuntatu , bani labari dan Allah pls ya haɗe hannayensa my Esha , uhm Aisha tace " kasan me ?" a'a Khamis yace " to in gaya maka ɗazu da muka shiga kasuwa nida Ummi kawai na mance naje gurin Lawali hmm ai yana cewa " ya kamani na zuba da uban gudu , dariya Khamis yasa iya ƙarfinsa harda tafi yace " to me kikayi masa ?" taɓ sirri ne wlh basai kaji ba bazan gayawa kowa ba Aisha ta faɗa tana turo ƙaramin bakinta , kina komawa gida za'a kawoki gidanmu zaki zauna dani ? eh man zan zauna malam yace " gidanku akawai lilo , waro ido Khamis yayi kana yace " lilo kuma ya akayi ya sani ?" oho Aisha tace " tana wasa da hanun Khamis, wata firar tasu driver na jiyowa shima ya dara wata ko baya ji , da haka suka isa ƙofar gidansu Aisha akayi parking wa inda aka ɗauka mutanen gidan da yan anguwa masu zuwa tsegumi duk suka fito wasu har tsawa sukayi wai suna jiran fitowar Aisha suga angon nata shiru babu Aisha ba ango haka suka gama tsayuwar munafurci sukayi gaba , wani daga cikin abokan Khamis ya bubuga glass ɗin motar yace " juliyat an romiyo ku temaka ku fito man , sarai Khamis ya jisa  ƙasaitar ta motsa dan haka ko saurarar sa beyi ba , yaci gaba da hira da Aisha yanaji a ranshi kamar yau ya fara haɗuwa da ita gashi duk lokacin da ya kalleta kyau take yi masa bare yau taci kwaliya ga zanen baƙin lalle da ja da akayi mata gani yake tafi sauran mata.....!

Muje zuwa fan comments sharhi 

*MOM ISLAM*
[07/08, 9:32 am] Mom Islam Ce: *YARINYA    MAI  TABARGAZA*

*Zainab Habib (Mom islam*

*Wattpad@ momislam2020*

*AREWA WRITERS ASSOCIATION*

BOOK 1

Page 66 & 67

Miƙo hanunsa yayi tare da cewa " sai kinzo gidanmu ya buɗe mata murfin mota da gudu ta nufi gida cikin nishaɗi , tana shiga ta faɗa cinyar mata a kunne ta raɗa mata cewar " mama kyakkyawa ya shamin baki kuma...mama ta toshe mata karki sake banaso kul ko wani karki gayawa , tom Aisha tace " hango anty Fiddausi da tayi ne yasa ta miƙewa taje gurinta tace " anty ashe kinzo ya jikin ? da sauƙi anty Fiddausi tace " a zuciyarta ta yaba kyaun da Aisha tayi a zahiri kam tayi ƙan ƙanta sosai.
Zuwa sallahar isha'i yan ɗaukar amarya sunzo lokacin tana tare dasu mama sunata yi mata nasiha akan rashin ji , yan kawo amarya ne suka shigo bayan sun gaisa suka

sheda cewar sunzo ɗaukar amarya ne , Aisha batasan menene aure ba hakan yasa ko gezau bataji ba bare tayi kukan rabuwa da mama , haka aka sauya mata kaya su maman Ummi suka riƙe mata hannu kasancewar gidan ango sunce kar su malam su siyi komai na ɗaki hakan yasa komai yayi musu sauƙi , kukan rabuwa da Aisha mama keyi sosai mutane na bata haƙuri Aisha kam se cewa " tayi mama zan dawo kuma zan kawo miki chocolate ,wani baƙinciki ne ya kuma kama mama ace an aurar da Aisha batasan zafin kanta ba .
Haka suka sanyata a mota aka wuce da ita gidan su Khamis , sunyi tafiya mai nisa kana suka iso anguwar G R A ne anguwar tsararrun gine ginen sun ishi mai karatu misalta gidan su Khamis , get man na buɗewa suka shige parking motocin sukayi gurin da aka tanada kana kowa ya fito ji kake ana rangaɗa guɗa mai sauti bakin Ammi kamar zai taɓo haɓa tsabar murna Aisha tazo da kanta ta riƙo hanun Aisha suka shige ciki , kai tsaye part ɗin Ammi suka nufa a palo suka yada zango aka fara gaisawa yayinda momyn Afnan ke zaune kujerar dake kallon tasu Ammi ita kuma Afnan na zauna idanunta sun kumbura kamar tayi kuka , ƙara lulube Aisha Ammi tayi tanajin sonta cikin zuciyarta , miƙar da Aisha Ammi tayi tace " wa enda sukazo su biyota ta nuna musu part ɗin Aisha , kai tsaye suja bi ta wata ƙofa mai glass da zata sadasu da sashen Aishar , wow fans ku ƙaddara aljannar duniya ɗakin Aisha tun daga palo har bedroom sai wanda ya gani an zuba tsadaddun kaya nera tayi kuka kamar ba'asan zafin kuɗi ba , sosai kowa ya yaba da kyau da tsari irinna part ɗin ga wani sanyi AC dake ziyartar kowane baƙo dake zaune a palon , daga can waje garden ne mai cike da kayayyaki mai cike ƙayatarwa, da haka kowa ya yaba da tsarin gidan .
Haka suka tafi suka bar Ammi da Aisha a zaune cikin farinciki. around 9:pm Khamis ya shigo part ɗin Ammi da sallamar shi momyn Afnan ce ta amsa tare da murmishi waigawa yayi yaga Afnan a zaune tana kallonsa , zauna man momyn Afnan tace " tana nuna masa gurin zama , kwata kwata jikinsa bai bashi ya zauna ba dan haka yace " ina jinki , nunashi momyn tayi da yatsa kana tace " wato ni zaka kawowa raini ? to inason magana dakai zama Khamis yayi zuciyarsa babu daɗi burinsa yaga Ammi da Aisha yasan suna tare , momyn Afnan dake shirya zantukan da zata gaya masa tace " inason ka auri Afnan ba wai shawara nake baka ba umarni ne so ina jiran amsarka ta riƙe ƙugu kamar mai shirin faɗa , kamar daga sama sukaji Ammi tace " momyn Afnan banison sakarci gida nawa kikeso ki raba masa hankali ki fita a idona dama zaman da kukayi kenan? maza kaje yar mutane na kuka ka barni dasu , Ammi ta nuna masa hanya , ficewa yayi sai da ya dai daita nutsuwarsa ya nufi gurin Aisha yana shiga part ɗin nata ya sameta zaune a ƙasa ta takure ta kifa kai da guwaiwa tana kuka , aslamu alaikum Khamis yace " da dadaɗan muryarsa , a zabure ta ɗago kai tare da cewa " kyakyawa kazo ka kaini gurin mama dare yayi bacci nakeji , dafe goshinsa yayi tare da cewa " haba my Esha kefa kikace zakizo ki tayani kwana ko kin fasa ne ?" eh tace " tana gyaɗa kai waro ido Khamis yayi yama rasa mezai ce mata , barinyi wanka in fito ko sai muyi magana , da sauri Aisha ta miƙe tana cigaba da kuka tace " ni tsoro nakeji karka tafi ka barni , no my Esha wankafa nace miki Khamis ya faɗa yana cire shaddar jikinsa , bata yarda ba yasa shi kamo hannunta suka nufi bedroom ɗin da ya kasance nashi , suna riƙe da hanun juna zaunar da ita yayi a bakin gado ya ƙarasa cire kayansa dagashi sai gajeran wando ,zaro ido Aisha tayi tace " malamin islamiyarmu ya hanamu ganin mutum da gajeren wando , murmishi Khamis yayi yace " to ai ni halak ɗinki ne ni mijinkj ne rufe fuska tayi tace " miji kamar inda su anty Fiddausi suke da yayanmu ? eh ya bata amsa , taɓɓ Aisha tace " wahala nikam bazanyi aure ba wlh wata mahaukaciyar dariya ce ta kubcewa Khamis ya dingi ƙyal ƙyalawa har saida yaji tayi shiru , to yanzu me kikayi inba auran ba ? Khamis ya tambayeta , nazo inyiwa mamanka kwana ɗaya gobe zan koma gidanmu inga Ummi da mama da malam , to Allah ya kaimu Khamis ya faɗa ya shige wanka, tunda ya shigo toilet ɗin ya faɗa bathroom yaketa sakin murmishi ko na meye oho haka ya cucuɗe jikinsa yana mai jin nishaɗi , kayi ka fito wlh ko kaji jiki ya jiyowa kunnensa kuma muryar Aisha ce ,still murmishin ya kuma yi ya fito ya ɗauki

towel ya tsane jikinsa ya fito ɗaure dashi a ƙugunsa ,tana ganinsa ta rufe ido tana cewa " ƙato da ɗaurin zani waro ido Khamis yayi yana kallllon inda take waƙar tana tafa hannu , taso muje inyi miki wanka ko zakiji daɗin jikinki , wani irin kallo tayi masa mai kamada kama rainani tace " bari kaji mu yammata ne inji su maman mu kuma an dena yimin wanka ni nakeyi , to aini mijinki ne yar budurwa zomuje in yi miki firjewa ta hau yi dole ya haƙura ya ƙyaleta sai da ya gama shafe jikinsa da mayukansa masu daɗin ƙamshi kana ya taje la llausan sumar kansa data kwanta kamar ta larabawa , ya nufi drowar , wasu sleeping drees ya ciro nashi masu ruwan sky blu ya sanya , dariya ta shigayi tana tafi wai yayi kamada wani ɗan film ɗin indian hausa , murmishi Khamis yayi kana yace " to jekiyi wankan ina jiranki, tana shiga ta tsaya dube dube tsalle ta shigayi tana cewa " kyakkyawa nanma kalar bayin da muka kalla jiya ne a tv inna mai ƙosai wlh film ɗin ya haɗu ta fara yi masa waƙar leƙowa yayi yace " wai bazakiyi wankan ba kizo ki kwanta ?" cuno baki tayi tace " to zo kabani sabulu kuma babu bokiti a bayin , nuna mata bathroom yayi yace shhiga ban taɓ Aisha tace " bazan shiga ba tunda uwata ta haifeni ban taɓa shiga ba amma yau kace in shige hu ' um tana shirin ficewa da gudu ya tarota yana cewa " kinfi son inta magana ko bazakiyi wankan ba , to shikenan ya tafi ya bata guri , da gudu ta biyoshi tana cewa" kyakkyawa kayi haƙuri zanyi to bani ruwan wanka , tara mata yayi tare da nuna mata soso da sabon brush da man goge baki , sai da ta gama rawar ta yana kallonta kana ta fara wankan turo mata ƙofar yayi ya fito yaci gaba da shirinsa , jin tana waƙa tana cewa" jirgin lulawa da ya lula sai da yakai barno .
Tanayi tana tsalle a cikin bathroom sai ka jita facakal a fitowa ta biyu ne ta bige ihu ta tsala tana kiran kyakkyawa kazo zan mutu....!

Kuna raina love you all🥰🥰.

*MOM ISLAM**

*YARINYA MAI TABARGAZA*

*Zainab Habib (Mom islam*

*Wattpad@ momislam2020*

*AREWA WRITERS ASSOCIATION*

BOOK 1

Page 68 & 69

Cikin shirinsa na salman khan ya iso gareta da gudu , kinji ciwo meya sameki ? ya dinga jero mata tambayoyi .ka ɗaukeni banji ciwo ba wlh wanan abin mai kamada sulu bazan ƙara shigarsa ba ta ƙamƙameshi suka dawo bedroom, maza shafa mai ki kwanta , maƙe kafaɗa tayi tace " walh na gaji bacci nakeji kuma wanan katifar zanhau ta haye da gudu tana tsalle a kai babu inda ya iya haka ya barta ta kwanta gudun kar tayi masa rigima , ja mata blanket yayi ya kwanta gefe shidai burinsa ya gansa gashi ga Aisha kuma yayiwa Ammi alƙawarin bazai yiwa Aisha abinda bataso

ba , kyakkyawa nifa bazan kwanta da kai ba kalan gobe da safe ace inada ciki wlh bazan yarda ba ta miƙe da sauri tana shirin kuka ,fuskarshi ba ita yake kallo ba hakan ya bashi damar tuntsirewa da dariya amma marar sauti , jin yayi shiru yasa ta kwanciya ta ƙudundune a bargon wai kar yazo kusa da ita.

